💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favour you always💔

_✍🏿M Shakur_

_Bismillahil Rahmanir Raheem, da Sunan Allah Mai Rahama, Mai Jinkai_
_This Novel is solely work of fiction, banyi dacin zarafin wani ko wataba, dafatan zan nishadantar daku_

💫💫💫💫💫
_What is drugs?_
_What are illicit drugs?_
_mesa people do drugs?_
_What do they feel when they do it?_
_why why why shaye shaye?_

_Oh Hey VIPs dina💃 ever been curious about this questions? Well this novel will walk you through  everything dangane da shaye shaye, overcoming it and many many more ku gyara zama a kakkabe zani_

1️⃣

Horn da akayi yasa  mai gadi yafito da saurinshi daga dakinshi that is just beside the gate ya zare sakatan gate din ya wangale gate din sabida motar ta shigo, wangale gate din da akayi yasa wata yar budurwa da bazata wuce 25-26yrs ba da wani matashi ke zaune gefenta kan plastic chair yana sanye da bugaggiyar shadda milk duk suka dago kansu suna kallon Gate din

ganin wanda zai shigo ciki da alamun tadi sukeyi abunsu dan kowannen su na dauke da murmushi kan fuskarshi, motar gidansune ta shigo har zuwa inda ake parking motar yay parking, bude bayan motar akayi wata yarinya fara dake sanye da jean da t-shirt ne tafito ta tsaya tana turo baki tai kini kini da rai, white flat shoe ne na vine a yar karaman kafarta da dududu size dinta bazai wuce 37 ba yar kafar, sai pencil jean din jikinta daya tsaya mata a daidai idon sahu, kafarta na haggu sanye dawani hadadden leg chain daya kama yar faran wrist din kafan nata, yama kafan nata kyau sosai bana wasaba dan silver color ne, ba karamin kamata sky blue Jean din chinos din yayiba batada wani girman ass but is a lil bit bumpy saidai tanada wani mahaukacin hips curve, irin matan da ake cema cylinder shape kenan, wani white non logo t-shirt ne ajikinta yadin so soft fari kal babu ko single stain ajikin rigan, tasaka wani simple necklace mai hawa uku masu dauke da pendent din moon shape wanda the last one ya sauko har kasan wajen gab da cikinta suna walkiya, babu komi kan fuskarta batasa makeup ba, dan ficicin pink lips dinta sun bushe sosai sai manyan idanunta da kwayan idanun kenan mai ruwan toka ko kadan ba bakake bane, tanada cikan gira baki, sai dan karamin sky blue dan gyalen data yane kanta dashi da ana ganin almost rabin kitson ta yan fici fici kalaba masu kyau sosa, wrist dinta na haggu sanye da digital watch sai dayan wrist din tadaura wani fine simple bracelet daya karama little tiny hand din nata kyau, ko kadan bata da girman jiki, batada wani tsayin kirki badai gajera bace, sanan batada kiba kawai she is super portable, bata da girma kuma baxaka kirata karama ba. Kallon direban daya bude kofa yafito tayi bayan ya kashe motar, turo baki tayi tareda hararanshi cikeda tsiwa tace "kai Isa bazaka bani jakana ba ninagaji da tsayuwa" da sauri Isa direba yazo wurin cikeda girmamawa yace "sorry Autan Mummy, dan gyara na dauko miki to" matsawa gefe tayi tana kwafa tareda kama waist dinta da hannu daya tana jiranshi yadauko mata jakan ya bata, wani bagpack yadauko mata irin na yan matan nan da yan makaranta ke amfani dashi da ake goyawa abaya fari ya mikamata yana murmushi yace "yauwa to ungo gashinan nadauko miki Auta" hannu tasa ta fizge jakan kaman ana fada sanan tajuya ta tafara tafiya tana fita daga parking tent din tai cikin yard dinsu, das das take tafiya kaman bataso tayi hips dinta na juyawa gashi jean ne ajikinta abin looks so alluring to the eyes, tundaga nesa take ballama Ya Siddiqa dake kallonta cikeda takaicin ta harara, saida takaraso wajen taja wani mugun tsaki tace "bashi ko tara eh? Anwani kafe mutun da idanu kaman za'a tsotsemai jinin jiki, sa'ido dai sana'ar banza ne" tai wani fari da ido tai gaba abinta batare data gaida koda mutumin dake gefen Siddiqa ba, azuciye Siddiqa ta tashi daga kan kujeran zata bita da sauri Sadiq yarike mata hannu yace "me haka ina zaki? Ki barta yarinya ce bakigani ba" cikin fushi Siddiqa ta fizge hannunta tace "Baby wlh duk rashin kunyan ta tai dani ni kadai bazan ma tanka taba, amma tsabagen rashin kunya ta kallemu taja tsaki sanan tacemana sa'idawa, that's an insult wlh saina fasa mata baki yau agidan nan" kafin yamayi magana ta fizge hannunta tai ciki tsabagen yanda kirjinta ke zafi yana tafarfasa sabida yanda Auta tamasu itada Sadiq rashin kunya haba mana, agaban wanda zata aura zata disgata.

Bude kofar falon nasu tayi ta shiga daidai Auta dake shirin shiga corridor ta waigo jin anbude

kofan, harara ta balla mata cikin murya kasa kasa tace "mayyar tabiyoni" dawani irin gudu Siddiqa tanufota dan taji metace wato itace mayya, ganin Siddiqa tabiyota da gudu yasa ta yunkura zata gudu amma ina Siddiqa tariga ta chapke bayan riganta ta fizgota azuciye ta bugata da bangon corridor cikin fushi tace "uban waye sa'idawa? Su waye zasu shanye miki jini sanan wakike cema mayya?" zaro idanu tayi cikeda rashin kunya tana kokarin ture hannun Siddiqa data chakumo gaban white t-shirt dinta tace "me haka? Kika batamin white rigana wlh saikin wanke shi, ki sakeni nace ko" bude kofar wani daki dake corridor akayi wasu yan mata guda biyu suka fito duk sunfi Autan girma alamun yayyunta ne suma dake kama da Siddiqa sosai, black beauty dasu, daya daga cikinsu wacce daga gani ita kebin Siddiqa tace "yauwa Ya Siddiqa cimana uban mara kunyan shegiya mai idanun mazuru" cikeda tsiwa tana kokarin ture hannun Siddiqa ta kwace kanta tace "eh kekuma mai idanun gapiya, gapiyan ma maicin kashi" dariya tayi sosai tace "eh gwaradai gapiya maicin kashi da mazuru mai satan kaji, kinji Ya Siddiqa lallasata dama atike nake da ita" bude wani kofa akayi dake facing corridor alamun dakin shine kodai master bedroom kokuma dakin wani babba agidan ne, wata matace baka itama Siddiqa na kama da ita sosai ta fito da akalla zatai shekara hamsin da hudu 54, dattijuwa ce amman jikinta nada kyau sosai tana sanye da doguwan rigan atampa da aka mata stone work hayaniyan dataji yasa tafito agurguje daga bayi dan tun dazu tana bayi ganin yanda Siddiqa ta chakume Auta yasa da sauri tajawo kofar dakin tanama Siddiqa wani irin mugun kallo tace "me haka kika chakume auta kasheta zakiyi?" cikeda fada dajin haushi Siddiqa tace "Mummy wai yarinyar nan nida Ya Sadiq zata kalla tacema sa'idawa, sanan wai zamu shanye mata jini, kuma wai ni take cema mayy......" da sauri Auta ta chabe maganar cikin muryanta mai zaki da dadi kaman zatai kuka tace "Mummy karya take mini, aini bance hakaba, sune keta kallona kuma sai hararana Ya Siddiqa takeyi fa, ni banmata komiba daga dawowa na" kafin Mummy tai magana Siddiqa ta bugata da bango tana jijjigata tace "dan ubanki nike miki karya, bakida kunya ko sabida kinga kinyi girma kema kin fara nono"  cikeda jin dadi Lubabatu Mai bin Siddiqa tace "yauwa Ya Siddiqa ki gurje shegen bakin datake mana rashin kunya dashi abango, shegen bakin kaman tsuliyan kaza" harara Auta data fara kuka ta watsama Lubabatun tafashe da kuka tace "muguwa kawai, agulmawiya, ai nadai fiki nonon kumadai, da fuska ki kaman burnt abinci" yowa wajen Lubabatu tayi cikin son ta jibgeta tace "dani kike?" Lubabatu tai wajen ta daga hannu zata sharara mata mari Mummy ta daka musu tsawa. "Siddiqa! Luba!" duk dagokai sukayi suka kalleta, harara Mummy ta zuba musu tama Siddiqa dahar lokacin ke chakume da Auta tace "cikamini yarinya kafin na mugun sabamiki" sakinta ahankali Siddiqa tayi da sauri Auta tai wajen Mummy tafada jikinta tasaki kuka, cikin kuka tace "Mummy kinga Ya Siddiqa ta shakemin wuya kasheni takeso tayi, Mummy kice mata karta karacemin nafara nono banso" tafashe da kuka sosai, ta tsani insuna fada suce mata sabida tafara nono ne kaman su take musu ranshin kunya ta tsani maganan, shafa bayanta Mummy tayi cikeda lallashi tace "zan musu magana, ta Allah batasu ba kinji, je wuce dakinki kiyi wanka zan kawomiki abincin ki yanzun nan" gyadama Mummy kai tayi tasa hannu tana share hawaye tawuce sumi sumi sanan ta juyo ta kalli yanda suka tsaya charko charko suna kallonta wani matsiyacin murmushi tayi irin na neman tsokanan nan sanan tama Siddiqa da Luba gwalo, da sauri Luba tace "Mummy kinga tana mana gwalo ko" da sauri Auta tabude kofar dakinta ta shiga, kwafa Luba tayi cikin konkoni tace "wlh gamuwata dake bazatai kyauba, nakama yarinya wlh sainai mata jina jina saidai duk abinda za'amin amin" cikeda fushi Mummy tace "mafashi, inbaki daketa ba kin raina Allahan

daya hallice ki, shegiyar yarinya yar bala'i kawai, da katon kanta kaman na giginya" bude kofa Luba tayi ta shiga tana magana ciki ciki tana kunkuni tace "badai kaina ba kan autanki dai" daga murya Mummy tayi tace "me kikace dan ubanki?" turo baki tayi da kyar tace "aini badake nike ba" "kimayi kiga in ban zubar miki da hakora ba da ranan nan" Mummy tafada tana huci, tabe baki Zeenatu da tuntuni tana tsaye tana kallon draman batare datace musu komi ba tayi tajuya zata shiga dakin da sauri Mummy tace "zonan Zeenah" juyowa tayi tama Maman tasu kallon haushi tace "gani Mummy" binta Mummy tayi da kallo daga sama har kasa tace "nasan duk yayana kece slow poison, wanan dabakice uppan ba Allah kadai yasan me kike hadawa aranki, wlh ko kurjewa naga Auta tayi, kurjewa nace to wlh sainaci ubanki, wuce kije kitchen kihado mata abincinta kikaimata taci" hararan kofar dakin da Autan ke ciki tayi tajuya tai hanyar fita daga Corridor, kallon Siddiqa dahar lokacin ke tsaye idanunta sun cika da kwalla tap tsabagen yanda abinda Mummy tayi ya bakanta mata rai tayi, yarinya tazo tamata rashin kunya sanan tama wanda zata aura Ya Sadiq rashin kunya dudda haka Mummy batace komiba, murmushi Mummy tayi ta taho wajen kama hannun Siddiqa tayi suka fita daga corridor sukai falo cikeda lallashi tace "ya isa to kekuma, bakomi Auta zatayi kudingajin haushinta ba, yarinya ce, dududu guda nawa take aduniya eh? Daga ke har Sadiq din ai duk yayyinta ne? Yakuri kinji zan mata magana zata dena, wuce ki koma wajen Sadiq kinbarshi shi kadai, kuma ki saki ranki karya ganki duk wani iri yagane akwai matsala, nunama saurayi ake kana tsananin son dan uwanka, tashi kitafi" tashi Siddiqa tayi tawuce tafita daga dakin deep down bata hakura ba tai alkawarin saitaci uban Auta wlh.

Fitowa da Zeenatu tai daga kitchen rikeda plate da jellof rice kekai dayaji fried plantain akai yasa Mummy tace "ahaka zaki kaimata abincin kaman zaki kaima awaki? My friend go back to that kitchen ki daura abincin nan kan tray, ki dauko mango juice din dana hadamata kidaura akai da glass cup, ki kuma samata salad ki sako mata nama guda biyar kinsan tanason nama" juyawa Zeenatu tayi tana kunkuni tace "saikace president zan kaima abinci" kasan cewan Mummy bataji taba yasa ta gyara zama tacigaba da kallon datake yi, jin Zeenatu tasake fitowa yasa tadago kai ganin tayi yanda tace yasa tace "kuma wlh ko kallon banza kika mata sainaci ubanki, kina bata abincin kifito kinajina ko banso adameta bacci zatayi" gyadamata kai tayi tai corridor.

Bude kofar dakin Zeenatu tayi babu kowa adakin saidai  karan saukan ruwa dataji alamun tana wanka, dakin fess fess sai kamshi yake, fentin dakin off white ne sai dan gadonta dakeda girma normal normal an shimfida bargo mustard, curtains dinta kuma combination of white and Mustard kana shiga dakin zaka gane mai dakin nason this two colors white da mustard, karasawa ciki Zeenatu tayi tana kallon  cookie jar dake kan bedside drawer ta dako rabi

basuyiba, suma sunada cookie din dan Mummy ke ijiye musu adaki yara sudan sami kayan kwalama but su harsun cinye nasu dayake su ukune da ita sai Ya Luba, da Ya Siddiqa, itako Auta dakinta ita kadai dudda ma tsabagen rigima da fadan dasuke yi ne yasa Mummy taraba musu daki but dudda haka shegiyar bata iya kwana ita kadai dakin kawai zamanta ciki da ranane kawai dare nayi takeyin dakin Mummy, Mummy ma saitai bacci take iya sneaking out ta tafi dakin babansu in yana garin in kuma bayanan to tare suke kwana, ajiye mata abincin tayi akan gado daidai lokacin tabudo kofan bayin tafito daure da mustard towel dinta akirji daya saukan mata iya cinya tana kallon Zeenah data ijiye mata abinci tana turo baki takaraso ciki tana hararan ta tace "me kikemin adakina dakin kine eh, kifita kona hadaki da Mummy wlh" harananta Zeenah tayi saikuma tai murmushi cikin lallabawa ta kalli jar din cookies din tace "auta indan dibi cookies dinki?" wani kallo auta tamata saikuma ta balla mata harara ta zauna kan gado abinta tareda daukan tray din tadaura kan cinya zata faraci, ahankali Zeenatu ta zauna kusada ita murya chan kasa irin muryan begi begi dinan tace "haba yar kanwata Rahima naaa, indan dauka, 2 kadai zan dauka namufa yakare ne please" turo baki tayi ta make mata kafada ashgawbe tace "ba bakusona ba Mummy kadaine ke sona agidan nan, kuyita sa Dady namin fada, jiya saida kikaja Dady yasani nai wanke wanke bansan wani gulma kikamai ba, bazan bayarba" da sauri Zeenatu tadaura hannunta kan kafadarta aranta cewa take "shegiya mai shegen kafiya wacce bata mantuwa kawai, zaki gane kurinki ne yau" cikin sigan lallashi tawani jawota jikinta tace "kai, Allahu Rahima, to kiyakuri bazan karafadamai ba kinji Autan mu, yakuri, in dauka eh Autan Mummy da Daddy mu" wani irin murmushi tayi cikedajin dadi ta gyadamata kai tana gyara zama tace "dauki 10 nabaki duka" tashi Zeenatu tayi da sauri cikeda jin dadi tai wurin jar din tace "thank you Rims Auta" tadebi cookies din tai hanyar fita daga dakin sanan ta juyo ta kalleta ganin bata faracin abincin ba tana kallon abincin tace "kici abincin mana" yatsine fuska tayi ta dago kanta ta kalli Zeenatu tace "Ya Zeenah the food smell peprish wlh" aran Zeenah tace "mayya, ba Ya Zeenah ba ko Anty Zeenah zakice min bazanji tausayin ki ba, kinsaba kirana ai gasai, hancinta kaman na aljanna hartaji kamshin yajin" murmushi tayi tace "common ai Mummy bata bari asa yaji tasan bakison yaji, ci babu yaji ko kadan, natafi" gyadamata kai tayi tadebo rice din takai baki, maida kofar Zeenah tayi tarufe bayan tafito takafa kunnenta jikin kofar tana murmushi kaman an mata kyautan makka ba'a banza Mummy ke cemata kunama slow poison ba saitayi baxaka taba cewa ita bace ko zata iyaba, su Siddiqa da Luba biyemata suke suyita hauka tana haukata su, itako cin ubanta take ta karkashi.

Ahankali take tauna shinkafan dan bata iyacin abinci da sauri sauri ba, wani irin masifan yaji dataji waaaa abakinta kaman an nika attarugu buhu daya a abinci yasa tafeso abincin waje furururr da gudu, da sauri tadau mango juice din dake kan tray din ta kwankwade tana nishi da sauri da sauri, ajiye cup din tayi ganin batadena jin yajin ba yasa ta shiga hurama bakinta iska tawani irin zabura ta mike tray da abincin duka suka kifo kasa tana nishi fast fast, idan akwai one thing da her whole body baya iya tolerating in this life is pepper, wani irin ihu takurma tareda fashewa da kuka tana kiran Mummy hakan yasa Zeenah ta kwasa da gudu tana dariya tai dakinsu ranta fess, tai maganin mara kunyan.

💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favour you always 💔

_✍🏿M Shakur_

2️⃣

Bude kofan dakinsu da gudu tayi ta shiga tasaka sakata da sauri Lubabatu dake kwance tana danne dannen awaya tace "kekuma dawa zaki shigowa mutane daki da gudu haka?" hannu Zeenah tasa abaki alamun tai shiru kar Mummy tajisu hakan yasa Lubabatu tai shiru tana kallonta, ihun auta dukansu sukaji ta kwalama Mummy su kira tana kuka sosai atare dukansu suka fashe da dariya Lubabatu ta taso daga kan gadon da sauri tazo wajen da Zeenah ke tsaye tana dariya tace "me kika mata makira eh?" wani irin murmushi Zeenah tayi kafin tace "wanan Black Cameroon pepper dinan na  container na juyemata duka a abincin aiko taci shine take kukan nan gobema takara zama bayan tasan hanyan kitchen asa nakai mata abinci saina samata wanda yafi wanan" takara kwashewa dawani dariyan, shiru Lubabatu tayi tana kallonta cikin jin haushi tace "haba Zeenah ai duka kuma yay yawa kema kinsan koni bana iyacin Black pepper nan fadanshi yay yawa balle ita dabama tason yaji ko kadan inda tata ta za'abi da karma ai girki da attarugu just tomato and onion, inama laifin 1 spoon koshi ya isa yakoya mata lesson kika juye duka kinsan awa nawa zatayi tanajin yajin kuwa?" maganan Luba yasa Zeenah itama duk taji wani irin badadi zatayi magana sukaji muryan Mummy tana ihu tace "wlh, wlh kashekine kawai bazanyi ba yau Zeenatu inna kama ki, muje Auta" takama hannun Autan dake kuka sosai tabude dakinta suka shiga ciki dakine hadadden gaske komi tsaf yana kamshin turaren wuta, zaunar da ita tayi akan gado tace "zauna ina zuwa bari na kawo miki gishiri da ruwa yajin zai tafi stop crying" gyadama Mummy kai tayi tana hura baki tana kuka Mummy tajuya tafita da sauri daga dakin tai kitchen dinsu taje ta dauko salt da ruwa a fridge tahado mata da yogurt tadawo, gishiri da ruwa tabata da sauri ta karba tasha sosai tana kuka idanunta sunyi ja kaman wacce akama shegen duka, karban goran ruwan Mummy tayi ganin tana neman shanye duka ta ijiye tace "ya isa kekuma zaki fasa cikinki da ruwane? Karbi yogurt dinan kisha yajin zai tafi duka I promise" karban yogurt din tayi tana sauke ajiyan zuciyan kuka ta shiga sha itakuma Mummy ta juya ta ijiye ruwan kan side drawer gadon sanan tadawo ta zauna gefenta akan gadon, ahankali Rahima ta janye Yogurt din daga bakinta ta ijiye tawani matso jikin Mummy tadaura fuskarta kan kafadan Mummy tai lamo jikinta nadan bari, cikin wani irin murya na mugun shagwaba tace

"Mummy kibani abun please, yau baki baniba at all, am feeling hungry" daga kanta Mummy tayi da sauri daga kan kafadarta tana kallon yanda tayi kaman mara lapiya tace "kindai san babanku na garin nan ko, kuma kinsan baya bacci batare daya ganku dukaba, ki rufamin asiri kibari yay tafiya yacemin kwana uku zaiyi, gobe ko jibi zai tafi kibari inya tafi saina baki kinji" fashewa da kuka tayi sosai tana makema Mummy kafada tana goge hawaye da bayan hannunta, dan tsaki Mummy tayi cikeda gajiya da shegen rigiman banzan Rahima tace "ohh My God, Ke wlh kincika matsala Auta, nace kibari babanki yatafi ko kin wagemin baki kina kuka" kara kara karfin kukan nata tayi tana kallon Mummy tana ihu da sauri Mummy tace "to naji yishiru, yishiru lemme think, ki bari nai tunani to" shiru tayi tana sauke ajiyan zuciya tana kallon Mummy nata, hannu Mummy ta daura kan goshi tana tunani, kafin chan tabude ido ta kalleta murmushi ta sakinmata tace "shikenan to naji zan baki but saida daddare, kinga anama kiran sallan la'asar yanzu any moment from now babanku zai shigo, kibari idan zamu kwanta saina baki, yanzu tashi jeki cire towel dinan kisaka kaya babanku yahanaki zama da towel haka" dan turo baki tayi ta tashi tafita daga dakin tana tafiya ahankali Mummy tabita da kallo harta bace mata, dakinta tawuce ta tsallake barin shinkafan datayi tahau kan gado abinta, jakan makarantan ta tabude taciro wayarta Samsung mai kyau ta bude data tana dube duben message, fita tayi ta shiga game tafara bugawa, shima fita tayi ta jefar da wayan kan gado babu abinda kemata dadi, littafan ta taciro na school ta shiga dubawa suma babu wanda ke mata dadi hakan yasa ta watsar dasu akasa ta kifa kanta kan gadon tana nishi sama sama kaman mai asma tana bubbuga kafafun ta akan gado kanta nawani irin sarawa sai lashe bakinta take tana bubbude wa kaman wacce kejin kishi, bude kofanta da akayi yasa tabude idanuwanta dasuka kankance Lubabatu ce ta tsaya daga bakin kofa tana kallonta babu alamun wasa kan fuskarta tace "Malama kitashi kije ankira sallan la'asar nasan ma kona azahar bakiyiba kiwuce kije kiyi, kin daisan Abba yace mudinga kiranki idan zamuyi salla ko to kitashi" harara tawani irin watsa mata kafin takara gyara kwanciya kan gadon kifa kanta kan gadon tace "Malama kitashin mini agaban kofan daki tunda ba dakinki bane" daga bakin kofan Lubabatu tace "okay bazakiyi sallan bako bari nahadaki da Mummy" tsaki Auta tayi tace "anan dukanku kukafi auki gulmammun babbunan banza kawai" "Mummy, Mummyyy" Lubabatu ta kwalama Maman su kira, fitowa Mummy tayi ta tsaya daga bakin kofanta tana kallon Lubabatun, cikin tsananin jin haushi Mummy tace "wai menene matsalan ku da yarinyar nan eh, Zeenatu tasamata yaji a abinci kekuma mai kika biyota yanzu kimata, kasheta zakiyi?" cikin jin haushi Lubabatu tace "Mummy nifa ko dakin ta banma shigaba fa, kiranta nayi tazo muyi sallan la'asar" cikin fushi Mummy tace "to bazatayi ba kubarta inta gama hutawa zatayi Allahu Gafurur Raheem, wuce kibace daganan wurin munafukan yara sun tasa yar kanwarsu agaba wlh Allah zai saka mata" kallon dakin Luba tayi auta tamata gwalo tana kyalkyacewa da dariyan iskanci da sauri Lubabatu tawuce tana kunkuni tace "kiyita lalata ta yarinya bata salla kona asuba da kyar takeyi" da sauri Mummy tace "dani kike magana ciki ciki?" dakinsu ta shiga batare datace komiba, komawa dakinta Mummy tayi ta shiga bayi alwala ta dauro sanan tai sallan la'asar tafito dakin Autan ta leka ganin ta lumshe ido yasa tadauka bacci take tawuce dakinsu, ahankali tabude dakin dawani irin gudu Zeenatu tai bayinsu ta garkame kofan kwafa Mummy tayi tace "ai wlh saina rama mata, ba yanzu zamu haduba Zeenah"  ta kalli Siddiqa dake kan dadduma tana kallonta tace "harya tafi Sadiq din?" gyadamata kai tayi, tabe baki tayi tace "shine bakizo kin fadamin ba, anyway kutashi dukanku kuje ku daura abincin dare, Luba tashi kije dakin auta ki sharo min shinkafan data zubar akasa

kifito da komi waje" wani kallo Siddiqa tama maman nasu kafin ahankali tace "Mummy yanzu fisabilillahi ya zaki saka taje ta sharo abincin da kanwarta ta zubar ba dole su dingajin haushin autaba in aka kuma tabata kidinga masifa, ita autan batada hannu ne, bata iya aiki bane? Mummy gaskiya abinda kikeyi baida kyau wlh kina nuna sonk......." yowa kanta da Mummy tayi yasa tai shiru Mummy ta nunata da yatsa tace "ina baki girman ki amatsayin ki na yayansu baki kama kanki ko, wlh duk randa kika karamin magana haka I will not mind muna gaban kanninki ne saina kikkifa miki mari wlh, kitashi kiwuce kitchen kuhada dinner babanku yakusan dawowa" tashi Siddiqa tayi cikin bakin ciki sosai ta zare hijabin jikinta tafice daga dakin kaman zata tashi sama fuu, itama Luba tashi tayi Mummy tabita da harara tace "kindaiji aikin danasaki kiwuce ki dauko tsintsiya kije ki kwashe abincin daya bare inkin gama saiki wuce kitchen kuyi girkin" sanan ta kalli bayin tace "wlh Zeenah inna dawo dakin nan nasame ki abayi baki wuce kitchen kun daura abinci ba saina kakkaryaki dako ubanki inya dawo bazai ganeki ba" tana maganan tawuce tafita daga dakin.

Agaban dakin Autan ta tsaya tana kallon yanda Lubabatu ke tattare shinkafan Auta kuma na wasa da wayanta tana shishila kafa ko lura ma da Mummy batayiba. "Auta na" jin muryan Mummy yasa da sauri ta dago kanta, murmushi tayi ta sauko daga gadon da sauri tana gyara daurin towel din jikinta ashagwabe tace "Mummy na nazo yanzu?" Tsaki Lubabatu dake shara tayi ta cigaba da aikinta, ahankali Mummy tace "a'a anjima, me zakici yanzu dan bakici komiba, su dafa miki Indomie ne?" yatsine fuska tayi tareda girgiza kai dan batada apatite ahankali tace "a'a, banajin yunwa yanzu Mummy" murmushi Mummy tamata tace "to kwanta kicigaba da hutawa abinki" gyadama Mummy kai tayi tana murmushi tai kwanciyan ta tana hararan Lubabatu da gefen ido tana murguda mata baki, kallon Luba Mummy tayi tace "dau sharan kifita me kuma kikeyi?" daukan pakan tayi tafita daga dakin Mummy tarufo kofan tawuce tai dakinta.💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_* 💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favour you always 💔

✍️ M Shakur

3️⃣&4️⃣

Ahankali Zeenatu ta lallabo tafito daga bayin tafito tana leke leke ganin babu kowa yasa da gudu ta kwasa tai kitchen dinsu, babban kitchen ne sosai irin family kitchen dinan dake dauke da komi irin na yan gayun nan, Siddiqa da Lubabatu tagani suna aiki, Siddiqa dake wanke

kayan miyane agaban tap ta kalleta ganin ta shigo  tace "zogashi kiyi blending kayan miyan nan nariga na wanke miki, stew zanyi" da sauri takaraso ta karba ahankali itakuma Siddiqa takoma gaban gas, blender ta dauka ta zuba komi ta nika saida tagama blending din tass sanan ta juye a bowl tazo wajen ta mikama Siddiqa dake zuba rice a pot bowl din, karba tayi ta ijiye agefe tana kallon fuskarta ganin duk tayi wani iri hakan yasa tace "menene Mummy tamiki fadane?" girgiza kai tayi hakan yasa Lubabatu dake yanka su carrot itama ta tsaya tana kallon Zeenah tace "to menene duk kikai wani iri?" hawayen dake kokarin zubo mata tasa hannu ta share cikin wani irin yanayi na bakin ciki tace "Ya Siddiqa wai mesa Mummy batason mu tafison Rahima, kuma muyakamata ta......" hannu Siddiqa tadaga mata tareda girgiza kai tace "Zeenah karma kifadi abinda kikeso kifadi nasan me kikeso kifada, konima nasan banson rashin kunyan Rahima but sometimes nafi putting blame din akan Mummy, Mummy ko kadan bata barinmu mu nunama Auta the difference between right and wrong kuma itama bata nuna matan, sometimes ba iskanci zalla  takemana ba she really feels is very okay abinda take mana dan haka Mummy take nunamata, Mummy kullum kallon yarinya take mata, yarinyar da aka haifa jiya batasan ta girma ba yanzu, Allah dai ya shiryata, she will change eventually I know that komujima komu dade, now muci gaba da aiki kar Dady yadawo bamu gamaba" cigaba da aikin sukeyi su uku gwanin ban sha'awa sunadan taba hira.

Babansu bala'in mai kudine amma irin mutanen nanne da bai yarda ya shagalar da iyalinshi ba, dudda Mummy ta dameshi asamo musu mai aiki ki yayi acewarshi gashi da yara mata dasuka tasa tadinga koyamusu komi sunayi da kansu, saisa breakfast kawai Mummy keyi kullum shima dan suna zuwa makaranta da safene but weekend suke hadawa dakansu, gyaran gida ma haka sukeyi, dudda kudinshi bai irin ginin mansion dinan ba, gidanshi daidai daidai na rufin asiri ne 6 bedroom flat ne dakeda babban compound daya wadatu da fulawowi.

5:38pm

Horn akayi mai gadi yafito da gudu yabude gate danko a bacci yasan horn din motar Alhaji, shigowa wata babbar mota jeep tayi tai parking awurin da aka tanada dan parking, da sauri Mai gadi yarufe gate yadawo wajen parking din daidai wani magidancin mutum dake sanye da bakaken suit da neck tie ga wasu manyan littafai guda biyu masu kama da textbook a hannunshi idanunshi sanye da fararen glass kana ganinshi zaka gane daga aiki yake sabida yanayin shigan dake jikinshi, akalla mutumin zaiyi 64-65yrs, da sauri Mai gadi yadan russuna yace "barka da dawowa Alhaji ya kotu?" Mai gadi yay maganan yana mikamai hannu danya tayashi karban yan littafan hannun nashi dan murmushi yayi yabashi yace "Sani, barka da warhaka, ya aiki?" murmushi Mai gadi yayi yace "Alhamdulillah Alhaji" "to, to barkan mu" mutumin yay magana yanabin gidan da kallo wanda dabi'an shine kullu yaumin idan yadawo daga aiki saiyabi tsakar gidan da kallo yay inspecting gidanshi tsaf, idanunshine suka sauka kan kayan da aka shanyasu kan flowers yace "menake gani haka? Ban hana adena shanya a tsakar gidaba ga backyard nan inda akwai igiyan shanya kala kala, waye da wanan aikin?" Alhajin yay

magana azafafe ayanda yay maganan zaka gane irin iyayen nanne masu fada da masifa sosai, cikeda girmamawa Mai gadi yace "Allah huci zuciyan Alhaji laifinane wlh, kayan Auta ce kuma tariga tafadimani idan suka bushe na shigan mata dasu na shafa'a ne, a yakuri bari na kwashe su yanzu nakaima ta su ciki" da sauri Mai gadi yajuya zaije wurin kayan cikin fada Alhajin yace "zonan, dawonan Sani" da sauri Sani yadawo, yace "this should be the last time da Rahima zata saka aiki irin wanan kayi kanajina ko?" gyadamai kai Mai gadin yayi Alhaji yajuya yay hanyar flat dinsu Mai gadi biye dashi, da sallama mai kara as usual yayi yabude kofa ya shiga ciki yana kallon ko'ina jin sallaman Abban su yasa da gudu har suna yar rige rigen fitowa su Siddiqa suka fito daga kitchen din sukai wurin Mahaifin nasu cikeda murna. "Abba oyoyo, Abba sannu da zuwa, Abba Sannu dazuwa" sosai ya shigo da masifa amma ganin yaranshi duk sun fito daga kitchen da gudu suna mai oyoyo da sannu da zuwa cike da farin ciki yasa yasakin musu murmushin dabai shirya yiba ya tsaya yace "yaran Abban su" karban littafan shi Siddiqa tayi daga hannun mai gadi, itakuma Zeenah tace "Abba nizan cirema neck tie" murmushi yayi yace "to yar albarka gashinan zoki ciremin" itakuma Lubabatu da saurinta ta zaremai jacket din suit din jikinshi har rige rige suke, murmushi mahaifin nasu yayi sosai ganin sun gama cirewa yasa yazauna kan kujera yana sauke ajiyan zuciya yace "to nagode, Allah yamuku albarka yabaku mazaje nagari" duk zama sukai kusada shi sukace Ameen Abba, Siddiqa tace "Abba yaya aiki ya kotu? Mutane nawa kasa akai kai gidan yari yau?" dariya dukansu sukayi harda Abban nasu dan Judge ne shi a federal High Court din Abuja kullum inya dawo sai sunmai wanan tambayan, murmushi yayi sosai yace "yau babu kodaya, case akayi za'a sake zama sanan za'a yanke hukunci, me kukeyi a kitchen dukanku gidan ya dumame da kamshin girkin yan matan Abban su" da sauri Lubabatu dake kusada Abban tace "girki mukeyi Abba mai dadi" waigawa yayi kafin ya kallesu duka, babu alamun wasa kan fuskarshi yace "ina Rahima?" da sauri Zeenah kaman jira take tace "Abba tana daki, Abba kagani Ya Luba saida taje takirata tazo muyi salla taki, tun sallan asuba batayiba, Abba kagayau dazu data dawo daga school tama Ya Siddiqa da Ya Sadiq rashin kunya harda cema Ya Siddiqa mayya, tacema Yaya Sadiq dansa ido, sanan muma tamana rashin kunya, kuma kaga Abba mukadai keta girki bata tayamu komiba wlh Mummy wai mubarta tahuta tagaji tana kwance adaki" shiru Abba yayi yana sauraron ta duk cikin yaran nan nashi hudu baiga wacce take bashi matsala marajin magana irin Rahima ba, gashi harga Allah kusan yafi sonta kan dukansu wanan natural haka Allah yadauramai but bataji saisa ko kadan baya wasa da ita, basa shiri, duk gidan shi kadai take tsoro, horata yake da kyau, sabida Rahima ne yanzu yake kokarin yasan yanda zaiyi yadena tafiye tafiyen nan, babu randa baya mata addu'a kan Allah ya shiryar da ita, koya zaneta taci kukan ta koshi baya hana anjima takara laifin dayadaketa akai saisa yanzu yarage dukanta sosai danta girma baiso yamata illa koyaji mata rauni tana mace, ajiyan zuciya yayi ya kalli Siddiqa babban yarshi ta farko dan dukta fisu hankali ga fadan gaskiya, ahankali yace "hakane Mamana?" gyadamai kai tayi tace "hakane Abba" kwala mata kira yashiga yi. "Rahima! Rahima, Rahima!!!"

A mugun zabure Auta ta tashi daga kan gadon jin muryan Abban su na kiranta, tsoron Abba

take sosai bana wasaba, bakinta har rawa yake tsabagen firgita tace "na.....Na'am Abba, ganinan zuwa" gyara daurin towel dinta tayi tsabagen rudewa tama manta yahanata yawo agida da towel tafita daga dakin da sauri sauri gudu gudu tai falon.

Shigowa falon tayi harta karaso gaban Abba jikinta bari yake, sosa keya tayi arude tawani kwantar da murya looking so innocent kaman ta Allah, ahankali tace "sannu da dawowa Abba" tundaga kafa Abba kebinta da kallo daga ita saidan mustard towel din dake daure a kirjinta data daura tun dazu bayan tafito daga wanka ya tsaya mata acinya kanta babu dan kwali tai zuru zuru tana kallonshi, ko jiya saida yamata fada kan wanan daurin towel din gashi yauma same thing still saida ta daura, Zeenah Abba yataba batare daya janye idanunshi daka kan Auta datai zuru zuru tana kallonshi ba yace "je dakina ki dauko min dorinar nan mai baki hudu Zeenatu" dorina dataji Abba ya ambata yasa tafashe da kuka sosai jikinta narawa kaman mazari tace "Abba dan Allah ka yakuri menayi eh? Dan Allah karka dakeni banison dorinar nan please, Ya Siddiqa please kar Abba yadakeni" taja hannun Siddiqa takama tarike tana kuka sosai tana yarfe dayan hannun tana kallon Abba dahar lokacin kallonta yake irin kallon nan dake saka hanjin cikin yara kadawa in fear.

Ganin Zeenatu tadawo rikeda dorinar yasa tawani irin kurma ihu ta kwalama Mummy kira. "Mummy, Mummy kizo, Mummyna wayyo Allah na zan mutu"  tawani fada jikin Siddiqa ta chukwikwiyeta tana kuka kaman za'a nikata a injin, Zeenatu da Lubabatu sai gimtse dariyan su suke dadi kaman ya kashesu ganin yanda mara kunyan ta rude haka, har Allah Allah take Abba yafara lallasata, all this haukan kukan tanayi kaman zata koma cikin Siddiqa ko tashi Abba baiyiba yanadai rike da dorinar a hannu yana kallonta cikeda takaici, ganin towel din jikin nata na neman kwancewa yace "saki Siddiqa kitashi kizonan" sakin Siddiqa tayi tana kuka sosai ta sauko daga jikinta tana rike da hannunta tana gyadama Abba kai kaman kadangaruwa, gabanshi Abba yanuna mata da dorinar yace "kneel down here kuma nace kisaki yayan ki ko, saken mata hannu" arude tasaki Siddiqa tana kuka sosai tana yarfe hannu tace "Abba dan Allah karka dakeni kaji dan Allah" tana maganan tana kneeling a gabanshi inda yanuna mata tana gyara daurin towel din jikinta tana kuka sosai, daidai lokacin Mummy tafito arude. "wayatabamin Aut......" kasa karashe maganan tayi sabida mugun kallon da Alhaji yamata ta tsaya chak agaban corridor, Rahima na ganin Mummy takara karfin kukan ta tanama Mummy alamu da hannu datazo ta ceceta tana kallon Abban nasu tana kuka, ajiyan zuciya Abba ya sauke anatse yace "Rahima!" cikin kuka tace "na'am Abba, Abba dan Allah ka yakuri, wlh wlh bazan karaba, Abba in kanawa binta Rasulullahi in kanawa iyayen ka kayakuri Abba, Mummy dan Allah, Mummy kizo" tai maganan tana kuka sosai tana mikama Mummy hannunta kaman mahaukaciya, ahankali Mummy takarasa shigowa cikin falon cikeda damuwa ranta duk abace, takaraso gaban Abba zatamai magana ya daga mata hannu ganin babu alamun wasa akan fuskarshi yasa tai shiru, cikin kakkausar murya yace "Rahima nahanaki yima yayyunki rashin

kunya koban hanaki ba?" cikin kuka sosai tace "wlh kahanani Abba" gyadakai Abba yayi yace "bance miki kidinga kifitowa kuna aikin gida tareba" cikin kuka tace "kacemini haka Abba" ahankali Abba yace "good, ban hanaki yawo agida da towel ba?" fashewa dawani irin kuka tayi sosai tace "e....e..h kahanani Abba" "bance kidinga fitowa kuna salla tare da yan uwanki kullum ba?" gyadamai kai tayi hawaye kaman anbude dam tace "kacemini Abba" cikin kakkausar murya Abba yace "laifin ki nawa kenan?" cikin kuka tana kara mikama Mummy dake tsaye gefen Abba hannu tanaso tariketa tace "laifina hudu Abba" shiru Abba yayi ayanda yakejin haushinta inyace yamata hukunci da fushin nan zai iya yimata illa, he is just trying to calm himself down, ajiyan zuciya zuciya yasauke yace "jeki dauro alwala kizo nan kiyi salla agabana inkinga dama ki kara dawomin nan da towel, tashi daga nan, will you get out of my sight ko saina saba miki!" ya daka mata tsawa da gudu ta tashi tai ciki tana kuka sosai, cike da kunan rai Mummy tace "Alhaji dan Allah kadinga yimata ahankali...." "don't tell me rubbish Maryam!" Abba yadaka mata tsawan da saida yasa tai shiru da sauri, cikin fushi yace "I said don't tell me rubbish Maryam! while kullum ina fita nema dan na wadataku keda yayan mu, nabarmiki duka yaran nan namu amana, ke kina nan kina lalata Rahima, babu wanda Rahima ke gani da daraja aduniyan nan, bata ganin kowa da gashi, could you imagine saidai mai gadine zai kwaso mata kayan data shanya which am sure bama ita ta wanke suba, kina gidan nan tareda dukansu kin kasa sata tai salla me amfanin kito eh amatsayin ki na mahaifiyarta? An gayamiki Rahima yarinya ce har yanzu? Allah zai tambayeni dagani harke kan yanda muka bama wayan nan yaran tarbiyah" yanuna mata duka su Siddiqa da kansu ke kasa ganin ran Abba yau yabaci yanama Mummy fada which of course sunsan she deserves it, Abba yacigaba yace "yaran nan matane, idan bamuba Rahima tarbiyah ba intai aure me zata bama nata yayan iyye? Wani irin hali kikeso taje tana nunawa agidan mijinta, angayamiki zata dawwama tana rayuwa damune? Dazu da rana awurin aiki Aminina yasamen da magana dayamin zafi yamin ciwo amma nasan alkhairi yake nufi dani da bazaizo yamin maganan ba" yadanyi shiru yana sauke ajiyan zuciya sanan yace "yau zai taho aiki yabiya ta school dan ijiye su Aisha da Hafsat a school yaga driver ya sauke Rahima tana sanye da Jean fa da t-shirt sai dan ficicin gyale akanta rabin gashinta awaje agabanki yarinyar nan tai shiga kaman yarinyar arna ta tafi makaranta haka baki hanata ba, idan kinsan bazaki iya bama yarana tarbiyah ba zanje na auro wacce zata basu, this children are my life, gift din da Allah yabani ne inhar zan fita nema nabarki dazu bazaki koyamusu abinda yakamata ba wlh zan iyasaka konawane na auro wata matan inhar ta yarda tai na'am zata bama yarana tarbiyah nagayamiki" faduwa gaban Mummy ya shiga yi, tasan halin mijinta tsaf kaifi dayane wlh kuma zai iya aikata hakan, babu abinda ta tana aduniyan nan kaman kishiya, ahankali ta tsugunna tareda kama hannunshi tashi Siddiqa tayi daga wurin hakan yasa sauran yaran ma duk suka tashi sukai dakinsu, cikin damuwa sosai Mummy ta damke hannun Abba ahankali tana kallon fuskarshi tace "nai kuskure baban Siddiqa, amma kayakuri, ka gafarce ni zan gyara, ka gafarce ni dan girman Allah karkace zaka karo aure sabida tarbiyah yara, bagasu Siddiqa ba banine nabasu tarbiyah ba duk nice ko, to kayakuri dan Allah" tai shiru tana kallonshi ganin yaki kallonta har lokacin bala'ine bayyane karara akan fuskarshi yasa ta fashe da kuka mara kara sosai ta yanda yaran bazasu jisuba irin kukan nan mai karya zuciyan miji, cikin kuka tace "nayi kuskure, na yarda nai kuskure, Alhaji inason Rahima dayawa ne, ina son yarinyar nan sama da tunanin ka, saisa bana iya mata fada, burina aduniyan nan shine kome yarinyar nan keso tasameshi shikenan burina, banson naga tana

cikin damuwa ko cikin bakin ciki, yayyunta kyaranta sukeyi taita kuka, kaima fada kake mata kullum taita kuka, ni inban jata jiki ba abin zaimata yawa she is too small, kowa Rahima, kowa Rahima, komi Rahima, Rahima tai kaza tai kaza, ni kadai Mummy ta ke lallabata najata jiki, na sanyata murmushi amma kayakuri bazan karaba nai kuskure mijina kayafe mini" tafashe da kuka sosai, ba karamin sosa zuciyan Abba kalaman ta sukayi ba kasa daurewa yayi yajuyo ya kalleta ganin yanda take kuka yasa yasa hannu yadago ta yace "tashi kiga bar kukan hakanan, yi shiru" ya zaunar da ita gefenshi, hannunshi yasa akan fuskarta ya share mata hawayen tasa kafin yakama hannayenta yahade su waje daya, cikin wani yanayi na damu yace "you are getting me wrong Maryam, baki fahimce magana taba, listen I appreciate irin son gaskiya na tsakani ga Allah dakike ma autan mu, nima inason Rahima sama da tunanin ki fadan danake mata danta gyara dabi'un tane, yaro bazai dinga kuskure ba kadinga mai dariya kana nunamai yay daidai ba, inkai hakan cutar da yaron kake, I know daman u as the mother yakamata tadinga samin kwanciyan hankali da happiness a wajenki wanan bakiyi karyaba, abinda nake kokarin nunamiki anan shine ki dinga sata tanayin the right thing, Rahima tadena fita babu hijabi, babu mayafi, haramun ne a musulunci tana bayyana surarta, idan wani abu yasameta fa? Idan surarta ya burge wani da baida niyya mai kyau yay mata fiyade fa? Kinyi wanan tunanin? Ki hanata rashin kunya, sanan kidinga sata tana salla akan lokaci, aduk lokacin dasu Siddiqa zasuyi girki kidinga sasu dukansu ba ita taje ta kwanta ba suje suyi girkin tare, gyaran gida tare, wanki tare, su dinga all house chores tare, yarinyar nan babu abinda ta iya kinga hakan bai daceba kin gane nufina yanzu?" yay maganan yana shafa kumatun ta yanadan murmushi, gyadamai kai tayi itama tana murmushi tace "hakane zan gyara i promise you dan zinare na zakaga chanji" dan dariya yayi yace "ina sonki sabida kina daukan gaskiya, am sorry namiki ihu gaban yaranmu kinji, kiyakuri I was angry then ne yar Zinariya ta" girgixa mai kai tayi tace "bakomi yawuce" motsi dasuka ji yasa suka waiga Rahima ce tafito sanye da wani dogon pink hijabin ta da dadduma a hannu idanun nan sunyi jajir fuskarta duk ruwan alwala, daure fuska Abba yayi yace "shimfida dadduman kihau kiyi sallan kigama kizo" wasu sababbin hawayen dasuka zubomata ta share tana kallon Abban tace "dan Allah Abba karka dakeni kaji dan Allah, please Abba na" wani bakin kallon dayamata batasan lokacin data shimfida dadduma da guduba tahau kai ta kabbarta salla, ganin bamata da natsuwa yasa Abba yace "ki natsu kiyi sallan nan da kyau" kallon Mummy dake gefenshi yayi duktai wani irin kala tana kallon Rahima dake salla, hannu yasa yajuyo da fuskarta ta kallai dan murmushi yamata yasan ta damune yace "kawomin abinci naci, kiramini yarana sufito muci tare, dazaran naci zanyi wanka natafi study room yau zanyi kusan rabin dare achan akwai wani case danake aiki akai" gyadamai kai Mummy tayi ta shiga tai ciki dan kiran yaran shikuma Abba yamaida hankalinshi kan sallan da Rahiman keyi ganin tanayi komi da kyau yasa yadan sauke ajiyan zuciya ya shiga yimata addu'an shiriya  da chanza wa a ranshi.

Fitowan su Siddiqa yasa yajuya yana kallonsu kitchen duk sukayi harda Mummy suka shiga fito da kulolin abinci da tray, bajewa sukayi akasan babban falon Mummy tafara serving Abban su kafin ta zubama yaran, sallame sallan Rahima tayi ta jingina da kujera tana kallonsu duktai kalan tausayi, taba Abba Mummy tayi tace "dan Allah kayakuri Abban su aikin tubako Auta

bazaki karaba ko?" gyadama Mummy kai tayi tana share hawaye tana turo baki, murmushi Mummy tayi ta kalli Abba tace "kagani bazata karaba, oya bama Abban ki hakuri" ahankali cikin muryan kuka tana kallon Abban tace "kayakuri Abba bazan karaba" murmushi Mummy tayi tana washe hakora tana kallon fuskan Abban daya daure batare dayace mata komiba tace "yauwa Auta na dena kuka Abban ki yahakura, bama yayyin naki hakuri suma" kallonsu tayi kaman yanda suke kallonta hawaye ne yazubo daga idanunta ta share sannan tace "kuyakuri" murmushi Siddiqa tayi tace "yawuce" murmushi Mummy tayi tace "yauwa oya zo wajena" kaman jira take da sauri ta tashi tazo tafada jikin Mummy tana rera kuka ahankali, Abba bai kara cewa komiba yacigaba dacin abincin shi yanajinsu yanda Mummy ke lallashinta, saida yagama sanan yatashi yafita daga dakin motarshi yaje yabude baya wani babban leda yadauko na Teems Pestry shop gabaki daya bacin ran da Rahima tasa shi yasa yama manta da tsaraban daya sayo musu sanan yadawo daki, Mummy yabamawa sanan yay corridor dan zuwa wanka ganin ana gab da kiran magrib, ice creams ne aciki Mummy tabude, murmushi tayi taciro biyu ta mikama Rahima dake jikinta tace "iyye kinga ice cream dinku jekisaka a freezer yay kankara kaman yafara narkewa anjima sai kidauko kisha" ahankali tasa hannu ta amsa ta tashi tai wajen fridge sanan Mummy ta cicciro daya daya ta mikama sauran yaran duk karba sukayi basu cemata komiba dan inda sabo sun saba kome Abba yakawo na Rahima double ne nasu dai dai, sawa a freezer tayi tadawo zama tai kusa da Mummy tai lamo akan hannunta, ahankali Mummy tace "nazuba miki rice kici" girgiza ma Mummy kai tayi tana yatsine fuska ko kadan batason cin abinci, abinci ma baya mata taste abaki yanzu, shiru Mummy tayi tana kallonta sanan tace "ankira magrib yi saikije  dakina ki jirani zanje wajen Abban ku" gyadamata kai tayi ta tashi ahankali tai dakin Mummy duktai wani irin yaushi.

****

💫 _*BIN ABINDA ZUCIYA KESO*_💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favour you always💔

✍️ M Shakur

5️⃣&6️⃣

Wani babban bedroom ne hadadden da everthing looks absolutely neat dakin sai kamshin turaren wutan yan maiduguri dakin yake. Mata biyu ne sunci gayu sosai wearing wani material iri daya da aka musu irin gown dinan da ake kira da dinner gown mai ruwan gold sun daura

head black shima sunyi kyau kowacce na sanye da makeup akan fuskarta. Tsaye suke kan wata magidanciyar mata dake zaune kan kujeran gaban makeken hadadden mirror kwalliyan dake dakin, daya daga cikinsu namata daurin kallabi, murmushi matar tayi tana kallon matan biyun ta madubi yanda suka dage dauri sukemata, daya daga cikinsu ne dake left side din matar tace "Ummi kinyi kyau wlh sosai" murmushi matar da aka kira da Ummi tayi cikin natsassiyar calm voice dinta irin na kamilallun manyan mata tace "nagode Nabila" karasa daurin dayan tayi ta kalli madubin tana kallon fuskan Ummi ta mirror tace "yauwa angama Ummi" murmushi tamata tace "angaida Yusra sarkin iya daura kallabi" dariya Yusra tayi cikeda farin ciki compliment from Ummi kaman kyautan kudi ne dan Ummi bata fiye surutu ba ko kadan, tashi daga kan kujeran Ummi tayi ta kalli kanta a madubi ba karamin kyau tayiba wani mahaukacin lace tasa mai bala'in tsada mai ruwan gold dakeda tiny zanen flower na Black, tasaka wani sarkan zinare daya dace da shape din wuyanta da warwaron shi a right wrist dinta, ta daura fine agogo mai kyau a left wrist dinta, purse dinta tadauka Black tazura takalmi na vinci irin mara takurawan nan mai dadin tafiya tadauko wani hadadden mayafin ta yafa tadaga kai ta kalli babban agogon bangon dakin cikeda dan masifa tace "me suke bata lokaci haka ba 9 za'a faraba this is past nine shine har yanzu basu fitoba, bari naje na tattaro su su fito mutafi" tai hanyar kofa harzata fita saita juyo ta kalli matan guda biyu tace "Nabila kun tabbatar kun fadama Nani komi banson jikokina suyi kuka, makesure you set everything and tell the Nani all she needs to know" gyadamata kai sukayi atare, Nabila tace "to Ummi, ba zasuyi kuka ba matar ta iya kulada su sosai, yanzun nanma na dubosu har sunyi bacci kuma basa tashi cikin dare in sukai bacci sai gab da asuba dinan" gyadamusu kai tayi batare datace komiba tafice, fita daga flat dinta tayi tai wani flat dake bangaren wanda tafito daga ciki, shiga tayi bayan tai sallama babu kowa a falon hakan yasa tai bedroom kai tsaye tun kafin ta shiga takejin hayaniya, muryoyin maza suna surutu, bude kofa tayi ta shiga da sauri, tsit sukayi kaman basu ke uban surutu ba da akejin hayaniyar su har falo, maza hudu ne adakin, uku ne atsaye duk suna sanye da Black suit da bakaken cover shoe sunyi masifan kyau da covers kaman wanda zasuje dai wani babban occasion, sai dayan dake zaune kan  gado yana sanye da wani green wando dakeda layi jaa tagefe kafarshi sanye da farin safa sai jikinshi sanye da singlet. Agogon hannunta ta kalla kafin ta kallesu duka one after the other tace a"hiranku kawai kuke tayi daman ba shiryashi kukeyi kuda kuka cemin zakuzo tayashi shiri, kunsan karfe nawa? Oya kuwuce kufita kuje falo matan ku najiranku kufito dasu kuwuce mota gamunan zuwa" ta matsa daga jikin kofan ta nuna musu kofa alamun suzo su fita, sadaf sadaf sukazo suka fice one by one har dukansu ukun suka fita sanan ta maida kofar tarufe tayo inda dayan yake zaune yana kallonta murmushi shimfide kan fuskarshi, karasowa gaban gadon tayi tasa yatsa ta dungure mai kai tareda zubamai harara tace "biyema kannenka kayi kunata surutu instead of kashirya gashi lokaci yayi" murmushi yayi batare dayace komiba hakan yasa tasake watsamai harara taja ledan dake gefenshi wanda rigan sojoji ne keciki, hannu tasa ta zaro rigan tana balle maballin tace "oya stand up" tashi yayi ahankali dogone sosai dan yamafi mahaifiyar tashi tsawo, murdadde ne bana wasaba, ga wasu shati shatin six packs dayafito ta white singlet din dake jikinshi, baki ne shi very dark, yanada wani irin bright white idanu da gashin ido sosai bakake gasu dogaye yanada cikan gira gawani siririn hancin shi dogo dayakara ma fuskar nashi kyau, bottum lips dinshi is so so pinkish sai upper lips dinkuma baki hakan yabama bakin nashi wani irin alluring kyau baida gemu ko daya hakama saje baidashi kodan sabida anhana sojoji

ajiyewane saisa oho. Yanada cikan jiki dan ko kadan he is not skinny one element dayasa aka dauke shi a soja shine tsayin shi dake karamai kyau koyana cikin mutum dubu zaka ganeshi sabida cikan haibanshi da kwarjini.
Ahankali yamika hannushi ya zura cikin hannun rigan kaman yanda Ummi tabashi sanan yamika dayan hannun yasaka yana kallon fuskanta yanda take rufemai boturan rigan, Murya chan kasa yace "Ummi yaushe zaki dena treating dina kaman baby wai?" batare data kalleshi ba tana sakanmai boturin tace "inka girma"

zama abakin gado, da wani irin sauri Rahiman ta taho ta zauna agefenta kaman zata shige jikinta tana kallon kulan abincin, ahankali ta bude kulan marfin ta cire ta mikamata da sauri ta karba ta yar akasa yay kara, cikin fushi Mummy tace "wai bazaki natsuba kosai kintaso kowa na gidan? Wlh zan fasa bakifa tom" maida hankalinta kan yar takardan tayi ta shiga warwarewa, wani irin bude baki Rahima tayi tana kallon takardan kaman idanunta zasu shige ciki, warwarewa tass Mummy tayi wani dagargajajjen ganyen weed ne ya bayyana, dan murmushi Mummy tayi takai hancinta ta shinshina kafin tasa yatsunta tadan debo tana murzawa feeling the texture tace "kin ganshi very fresh from farm wlh mai kyau daga wani kauye a yola nasa aka kawomin, inda kinsan kudin danake kashe miki da zaki dingajin magana na jibi yanda kikama CODE9 sha daya dan Allah bayan kinsan jinin ki baida karfi, uhmm nama fasa baki gwara na sayar nasan sayarwa nayi" da sauri kanta kaman zai cire tace "n......no p....l...." tama kasa magana miyau har fitowa yake daga bakinta tsabagen yanda take kwadayi, dan murmushi Mummy tayi tace "always do as I say kinji, kema kinsan duk randa Dady bayanan har ci kike kisha kiture dan kanki, karki karamin abinda kikayi dazu kinji" gyadamata kai tayi da mugun sauri tana kallon abun burinta kawai Mummy tajuye mata a abinci dan yunwa takeji sosai, ganin yanda ta kosa yasa Mummy ta shiga zazzaga mata akan abincin white rice da stew da plantain din, saida tajuye tass dawani irin sauri ta fizge abincin tazauna akasan dabas, hannu tasa tajuya abincin kafin tafara debowa cikin hannu tanaci, hannu baka hannu bisa kwarya kaman wacce tai shekara uku bataci abinci ba, Mummy sai murmushi take tana kallonta tadau bottle water gefen gadon ta tana budemata, in less than 2min ta cinye tass ta yarda kulan awurin da sauri Mummy ta mikamata ruwan, karba tayi ta kafa abaki saida tai kusan rabin ruwan sanan taja wani irin gyatsa, dariya Mummy tayi tace "yauwa Alhamdulillah, su yarinyar Mamanta ankoshi, yanzu anci abinci, jebayi ki wanke hannu kidawo sai bacci ko naga idanunki harsun chanza kala" gyadamata kai tayi tanaji duk wata matsalanta yakau hankalinta ya kwanta ta tashi bayi tayi feeling super happy, ruwa tabude a bathtub din Mummy ta tsaya tana kallon ruwan da idanunta dasuka fara wani irin lumshewa, saida ruwan ya cika tap yafara zuba sanan ta washe baki kafin tawani irin fada cikin bathtub din da kayan jikinta tai resting head dinta a inda akesa head ta lumshe ido tasa hannu tana wasa da ruwan kanta nawani irin juyawa, she is feeling happy, she is feeling exotic, feeling exceptional, feeling out of this world, shiru tayi tareda dena wasada ruwan tana lumshe idanunta da sukai fici fici tana budewa har na kusan 2min sanan tai murmushi daya bayyabar da white teeth dinta cikin wani slow voice and in a very slow tone tace "nima I hate you, you are a bad person, kuma bazan kara kiranki ba wicked kawai" shiru tayi kafin ta ciko hannayenta da ruwa takai bakinta tai kurururururu da ruwan tana wasa kaman yanda yara sukeyi tawani irin fuzar da ruwan akasa cikin fushi tana kallon towel din Mummy dake ahange kan hanger tace "I hate youuu!!!" jin ihunta yasa Mummy tawani zabura tareda buga salati tace "innalillahi yarinyar nan zata tonamin asiri" da sauri Mummy tafada bayin salati tayi ta kashe tap din dahar lokacin ke zuba da gudu tawani jawota daga cikin ruwan hakan yasa ta bude ido kadan tanadan turo bakinta zatai masifa ganin Mummy ne yasa tawani irin rungume ta tace "Mummy naaaaaa, Mummy you are the best Mum, Ke kadai kesona, su Abba su Ya Siddiqa da wanan wicked din are all cruel people, Mummy na I love you sosai sosai" tadago kanta daga jikin Mummy ta kalli fuskarta tanadan lum lumshe ido tace "I love you Mummy naaaaaa" dan murmushi Mummy tayi tace "naji to cire kayan ki daura towel kije ki kwanta banson drama" Mummy tai maganan tana zage mata zip din bayan rigan tasake ta tareda jawo

towel, sanan taja mata rigan kasa ta daura mata towel din kafin ta kamo hannunta sukafito, kan gado ta kwantar da ita tace "oya sleep now don't make anymore mess, am tired jiki da jini" tajuya zata tafi hannunta takama cikin tsantsan maye tace "Mummy tell me what you use to tell me" shiru Mummy tayi tana kallonta saikuma tadawo kan gadon ahankali ta zauna hakan yasa da sauri Rahima ta daga kanta ta daura akan cinyarta tareda lumshe ido tana sauke ajiyan zuciya, ahankali Mummy take shafa kananun kitson dake kanta murya chan kasa tace "Autana I always give you what you want for that sake no one should know our little secret koda za'a kasheki ne right?" da sauri ta gyadama Mummy kai tace "ri..........ght" murmushi Mummy tayi tace "nasanki Rahima na kuma San duk cikin yarana babu wanda yakaiki rike amana da keeping secret, nobody should ever know that you and Mummy use to smoke kinji" da sauri ta gyadama Mummy kai tana murmushi, Mummy tace "always keep it cool, I will always give you what makes you happy and painless, in the night but during the day time babu shan komi so that nobody will know at home dan mutane suna ganin abun baida kyau, but mu munsan anything that makes you happy ai yanada kyau ashashi ko Auta?" gyadama Mummy kai tayi tace" yes Mummy, murmushi Mummy tayi sosai tace "salla inkinga dama kiyi inkinga dama karkiyi am an advocate of kowa yay abinda ke sashi farin ciki, live your life to the fullest kome kikeso let me know okay, I will give u har rayuwata ba duniya kadai ba, am your best friend kome zai sameki kome zakiyi let me be the person you will always meet first and tell kome zakiyi aduniyan nan bazan taba miki fadaba daidai ne awajena kinji" gyadama Mummy kai tayi kafin tajuyo ta bude idanunta da sukai danja ta kalli Mummy da itama ita take kallo, cikin murya yar kankanuwa tace "Mummy wanan powder white dinan kaman dakakken chalk yaushe zaki banishi?" dariya Mummy tayi tace "in an kawomin" shiru tayi tana lum lumshe ido hakan yasa Mummy batasake cemata komiba, ahankali bacci yay awon gaba da ita hakan yasa Mummy ta kwantar da ita tareda tashi ahankali tawuce bayi inda tabata ta gyara sanan tai wanka tafito tana kallon Rahima datai dai dai agado tana tikan baccin ta, shiryawa tayi cikin kayan bacci tawuce tafice daga dakin tai dakin Abban su dudda yana study but inya dawo zai samsta anan dan batason anything dazaisa yaje dakinta.

Around 5:02 ta tashi jin muryan Abba na kiranta, a firgice ta bude idanunta dasukai jajir dan kowani gaban jikinta najin kiran Abba ta kallai tanadan sassauke kai, babu alamun wasa kan fuskarshi yanuna mata kofa yace "wuce kije ki dauro alwala kiyi salla" gyadamai kai tayi ta tashi ahankali dan jiri take gani sosai bacci bai isheta ba, ganin tayi hanyar bayi yasa yajuya yafita dan sauri yake antada salla, bayin ta shiga ta wanko fuskarta tadauro alwala tafito tana kallon ko ina na dakin tadanji dama dama dan jirin yaragu sabida wanke fuskar datayi, wurin wardrobe din Mummy tayi tana kallon kofa da sauri tabude wardrobe din, hannunta tamika ganin hannunta baikai safe din dake chan sama ba yasa da tai wajen mirror, kujeran wajen ta dauko tahau kai ta tsaya hakan yasa takai safe din, password din da taga  Mummy tasa jiya ta shiga

sawa dan tana gani ta haddace shi tsaf akanta, bude safe din tayi jikinta har rawa yake, one bottle of codeine ta dauko gudun kar Mummy tagane sanan tasauko kara daya na wiwi tana waigen kofa, gyara zamansu tayi tsaf gudun kar mummy tagane sanan ta maida safe din tarufe tasauko tadau kujeran ta maida inda yake gaban madubi, sanan tadawo tarufe wardrobe din taboye abubuwan a jikin towel dinta sanan tabude kofa tafita tai dakinta, da sauri ta maida kofar tarufe jakar makarantan ta ta dauka ta zuba su aciki sanan ta rufe ta ijiye tana murmushi har wani murna takeyi kafin tai bayin ta, brush tayi sanan tai wanka tafito daure da towel, mai tadauka tafara shafawa saida tagama tsaf sanan tasake fadawa kan gado taja bargo ta lumshe ido ko minti biyu ba'ayiba bacci yasake awon gaba da ita.

Cikin bacci taji ana shafa mata fuska bude ido tayi da kyar tana turo baki ganin Mummy ne yasa ta mirgino ta daura kanta kan cinyar Mummy cikin muryan bacci tace "Mummmmm niban tashi ba" dagata Mummy tayi tace "tashi kafin Abban ki yakara tambayan ki, kinyi salla?" girgiza ma Mummy kai tayi ashagwabe, hakan yasa Mummy tace "toki barshi basai kinyiba, tashi ki shirya school, kinga yau zaku riga baban ku fita saisa naciro miki wanan abayan da gyalenshi ki saka banso kisa jean baban ku yahau miki fada" saukowa daga gadon tai da sauri tadau doguwan rigan da Mummy ke nunamata data ijiye kan kujeran mirror ta warware doguwan rigan tana daure fuska, hadadden doguwan rigane mai bala'in kyau na Dubai bakine complete babu kwalliya ajikinshi sai hannun doguwan rigan da aka bishi da wasu silver kullatai da akai musu design din flowers yay mugun kyau rigan. Cikeda rigima sosai ta kalli Mummy tace "Mummy nine zan sa kayan nan? Ni wlh bazan saba so ake zafi yakasheni eh" cikeda lallabawa Mummy tace "haba Auta na, Ke kinfiso ayita miki fada na yaune kawai gobe baban ki zaiyi tafiya yabar mana gida zakiyi yanda kikaga dama kinji" wurga rigan tayi chan wajen kofa tace "wlh ni banaso ni english wears zansa" dafakai Mummy tayi ta kalleta yanda ta zauna akan kujera ta juyamata baya tana kumbure kumbure, tasowa Mummy tayi takaraso har gaban madubin ta bayanta ta tsaya ta dafa kafadarta tana kallon fuskarta ta madubi tace "haba my fine princess, Princess Rahima na, yar lelen mamanta, duk gidan nan babu wanda zai nunamiki kyau wlh kai duk Abuja ma, beauty yar gidan Judge, yarinya inba dandan president ba sai rijiya adanmini murmushin nan mana" Mummy tadan chakuleta hakan yasa tafashe da dariya, ganin tafara dariya yasa Mummy tadauko rigan tace "imaza shiryo kici gayu kifito ina jiranki kizo kiyi breakfast kinji" gyadama Mummy kai tayi Mummy tawuce tafita.

Shiryawa tayi cikin dogon rigan tadau gyalen ta yane kanta dashi tadau wayarta tajefa cikin jakanta sanan ta giya jakan tabude kofa tafito tai falo, zaune taga duka yan gidan nasu a dinning, tunda tafito Abba ya tsareta da idanunshi dake cikin fararen glasses hakan yasa takaraso ahankali tayi kusada Mummy, da hannunta shiga wasa kafin murya chan kasa tace "ina kwana Abba" tea Abba yakai baki ba yabo ba fallasa yace "Ipy" juyawa tayi ta kalli su Siddiqa da suma duk sun shirya zuwa makaranta dan hararan su tayi ta gefen ido sanan tace "ina kwanan ku" Siddiqa ce kadai ta amsa dan sauran basuda lokacin dan iskan gaisuwanta. "kin tashi Ipy Rahima" ko amsawa batayiba tazauna kusada Mummy suka faracin abinci, tea

kawai ta iya tasha dan ko kadan bata iyacin abinci inba Mummy ta samata abinda tasaba samata ba, batajin dadin cin normal abinci saida suka gama tsaf sanan suka tashi, 5k Abba yaciro daga pocket yamikama Siddiqa yace "gashi nan dukanku, adawo lpy" sanan ya kalli Rahima da nugayen ido yace "kibari akawomin karanki kiga abinda zai faru yau, kuwuce kutafi" wucewa sukayi suka fita, gaba Rahima tayi fuu tabarsu tana zuwa tabude gaba ta shige ta rufo kofar da karfi, da sauri Luba tace "iyye Ya Siddiqa bakene ke zama agaba ba, bari naje nafadama Abba" hannunta Siddiqa tarike da sauri tace "kubarta, muje inada hot presentation this morning, banda lokacin Rahima yanzu" duk shiga bayan motan sukayi direba ya shiga yajasu har zuwa University of Abuja, Siddiqa yafara saukewa agaban department dinta na Accounting tana 400 level, dubu dai dai tabama Zeena da Luba, duk suka mata godiya sanan tajuya tagaba tabama Rahima nata 1k din ta hanyar ajiye mata akan jiki, cikeda tsiwa Rahima tadau kudin ta jefar ta window tace "mezanyi da kazamin kudin ku? Mummy na tabani ×2 of your chicken change, 10k dan haka banso" cikin tsananin fushi Siddiqa ta kalli kudin data jefo mata akasa tace "ni kika jefa da kudi Rahima?" "baki fasamata baki bane saisa har yanzu take mana iskanci" cewan Luba, ganin abin na neman zama rigima yasa Idris direba yace "dan Allah ayahakuri, bakuyi fada agida bane zakuzo kuyi a makaranta gashi anata kallonmu, kinga Siddiqa wuce ajinku kiyakuri yarinya ce" cikeda tsiwa Rahima tace "wlh ka kara cemin yarinya saina katsama mari hala nama kala da yarinya" bude marfin gaban motan Siddiqa tayi ta fincikota waje ta bala'in tsorata hannu tadaga zata wanketa da mari da sauri tarufe fuskarta tafashe da kuka jikinta na rawa tace "wlh kika dekeni saina gayaki da Mummy" sakinta Siddiqa tayi ta matsar da ita gefe ganin duk yanda ta tsorata sanan ta kalli direban tace "kaisu Lubabatu department katafi tajama kanta da kafarta zata taka tundaga nan har Vet wlh" tai maganan tana rufe marfin motan, direba yaja yay gaba, buga kafa ta shiga yi akasa tana kuka sosai Siddiqa tai tsaki tace "sai girma ba hankali, katuwa dake kina kuka cikin makaranta gashinan sai kallonki ake, ki kwana anan" juyawa tayi tai tafiyanta cikin department dinsu tabarta awajen sai kallonta ake.

Sauke jakanta tayi daga baya tana kuka tabude ta ciro wayarta ko tsayawa rufe jakarma batayiba tarike adayan hannun ta shiga neman layin Mummy, horn taji an danna mata da sauri ta daga kanta da idanunwanta dasuka rine da hawaye, kallo daya tamishi ta dauke kai wani shegen yaron ajinsune Chriss sunanshi Christian ne dayasamata ido, ajinsu daya shima Veterinary medicine yakeyi, duk inya ganta saiyace Hi beautiful amma ko kulashi batayi, fitowa yay daga motan da sauri hadadden guy ne yaci gayu sosai da wandonshi dayay ass down gawani hadadden sneakers akafarshi da katon sarkan cross yakaraso gabanta, cikeda damuwa yace "Hey Beautiful what happen? Why are you crying like this? Who was that Goddamn gurl that drag you out of the car?" yay maganan cikin fushi, daure fuska tayi tasa hannu tana share hawayen daya gama wanke mata fuska, cikin bala'i tace "is none of your business, leave me alone" "noo I can't, I can't leave you alone, u don't look good beautiful, let's go we have class by 9, and is to 9 now" kallonshi tayi da dara daran eyes dinshi, murmushi yamata yadan daga mata gira daya tareda cije lips dinshi yace "please beautiful let's go, I know u can't walk from here to our department, so let's go okay, plsss her majesty, plssss " yawani ja please din, dauke kai

tace "okay" murmushi yayi cikeda jin dadi yana bala'in son Rahima tun rana na farko data fara attending lectures, batama uban kowa magana a ajin dudda yanda kowa yake shigemata gashi sai mahaukacin kokari da inba kaga tana amsa tambaya ba baxaka taba cewa tanada kokarin ba. Hannu yamika yace "lemme help you with the bag beautiful" murmushi tadanyi dan haka takeso ana treating dinta kaman sarauniya ta mikamai karba yayi da sauri yataho yabude mata shiga tayi sanan yarufe yazagaya ya shige shima yatada motar.
💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favor you always 💔

✍️ M Shakur

1️⃣2️⃣&1️⃣3️⃣

Shiga cikin motar yayi ya rufo kofar sanan yadaura jakan nata akan jikinshi ya tada motar yaja ahankali, baya wani gudu dan baiso sukai department dinsu dawuri, soyake yadanyi hira da ita yanda yaci sa'a takula shi yau dinan, dan satan kallonta yayi sanan yace "who is she?" yadan kalleta itama kallanshi tayi wani iri yaji sabida yanda dara daran idanunta suka sauka akanshi da sauri ya kalli hanya yace "I mean who was that girl that made you cry?" daure fuska tayi cikin dan fushi tace "my sis, elder sis" dan yatsine fuska yayi cikin isa yace "tell her Chris yace today should be the last day dazata saki kuka haka inba hakaba saina rama miki" wani irin murmushi tasakinmai ta mugun ji dadin yanda yay maganan, kallonta yayi ganin tana murmushi yasa shima yay murmushi baisake cemata komi har sukakai department dinsu na Vet, tun kafin yayi parking suka hango lecturer ya shiga ajinsu kuma ka'ida ba'a barinsu shiga in lecturer ya shiga, dan ajiyan zuciya yasauke yace "wat a day! We are late" daure fuska tayi tamiko mai hannu tace "give me my bag I want to go, thanks for the ride" zare key yayi daga jikin motar ya kalleta yace "beautiful let's chat a bit now, lecturer yariga ya shiga please" harara ta watsamai cike da rashin kunya tasa hannu zatadau jakan da sauri ya fizge jakan hakan yasa bottle din codeine yafado kan kafarshi dan dama bata rufe jakarba bayan tadauko waya dazu, wani irin kwalalo ido tayi cikeda mugun tsoro ta kalli kafarshi kaman yanda shima yake kallon kafar kafin ahankali yamika hannu yadau kwalban dudda yasan codeine sosai danba bakonshi bane but yanaso

yakara tantancewa shine yake gani bawai gizo idanuwanshi kemai ba, dago kai yayi zai mata magana takawo hannu zata fizge kwalban da sauri yadauka da hannunshi harda jakan yay sama hakan yasa karan wiwi shima ya fado kasa dagawa yayi tareda ajiye jakan agefe ya kalleta yanda yaga tai zuru zuru yasa yagane natane ita kesha bawani ba, ahankali yace "so you do drugs beautiful?" girgiza mai kai tayi ahankali muryan ta har rawa yake tace "n....no....banawa bane ba" fashewa yayi da dariya sosai harda rike ciki saikuma yadago kai yace "alright naji, lemme take them then" yashiga bude marfin zai kafa abaki kaman zatai kuka tace "karka shamin abuna wlh" sake kyalkyace wa da dariya yayi kafin yasauke ya kalleta yace "you don't have to lie to me am your friend and your secret is safe with me, besides codeine ai na yarane, will show you abubuwan dat will make you feel kaman kina heaven" dan kaiwa baki yayi yasha kadan sanan ya janye ya mika mata rufewa tayi ta fizge jakanta ta zuba ciki ta rufe, kallonta yake tayi shidai tana bala'in burgeshi ga shegen kyau kaman ita tai kanta, dago kai tayi ta kallai hada ido sukayi hakan yasa ta danyi murmushi tace "zantafi" murya chan kasa yace "before you go, how about I give you invite to my birthday is in two days Beautiful, you know I will feel honored if a beautiful girl like you will grace my occasion, please Beautiful" yay maganan yana ciro katin invite din daya hadu iya haduwa kallo daya zakama Chris din kagane shima iyayenshi nada dan kudi ba laifi, makemai kafada tayi tana kallon katin tace "once I live school bama fita again" da sauri yace "how about you attend the pre birthday party" da sauri tadan yatsine fuska tace "and when is that?" "tommorow 2pm, then ai muna school u can come and leave by 4 kitafi gida, and is just few people, please do dat for me My beautiful Friend kinji" shiru tayi tadan juya ido saikuma tace "okay I will think about it, to if I decide to go who is taking me to the place?" da sauri yace "give me your number Beautiful, I will enter school tomorrow just for you saimu tafi tare kinji her majesty" murmushi tayi yanda yake lallabata namata dadi tace "Tom" ta mikamai wayanta, karba yayi ya sassaka numbers dinshi yay saving da sunanshi sanan yabata, karba tayi tajuya tafita daga motan tanata waige waige harta sami kasan wani bishiya ta zauna, hango ta dayayi all alone yasa yafito yay wajen haka yadinga janta dahira harta saki jiki suka dinga hira yanata sata dariya cikinta har yana kullewa kaman dama chan sunsan juna daga wani wurin, kusan zaniya cewa Chris is the first friend datayi tunda ta shigo makarantar nan 100level 2months ago.

Karshe ma batai attending aji kodaya ba ranan motar Chris ta shiga yasauketa a unguwarsu tamai waving bye sai gobe sanan tawuce gida, sai murmushi take Chris is really funny and such a sweet guy yana treating dinta like a queen, duk duniyan nan banda Mummy that treat her like a queen shine second person that treat her like a queen tana zuwa xatabama Mummy labarin shi tayi friend a school yau.

***************

Washe gari.

Cikin full shiganshi na kayan sojojin shi ya shigo Barrack din da motarshi Bentley da plate number kana gani xakasan na sojane, parking yayi a inda aka tanada dan parking kafin yabude motar wasu sojoji da aikin su shine gadin wajen sukazo da sauri daya daga cikinsu yabude mai motar tareda saramai. "Sir!" ahankali yafito daga motar bakaramin kyau kakin sukamai ba, yafito cikin shi ganshi na sojoji, lips dinshi sunyi pink sosai kaman wanda ke mura, hannu yasa yazare bakin glasses din dake kan idanunshi sanan ya maida kofar yarufe yasa key a wando yajuya ya shiga building din, lift ya shiga dayakai shi 4th flour sanan ya shiga wani office da aka rubuta Lieutenant ajiki, shiga office din yayi yana kokarin zaro wayarshi dake aljihu data fara ringing, wayar yaciro ya kalla ganin Ummi ke kiranshi yasa yakarasa ya zauna kan hadadden kujeran shi sanan ya amsa wayan.

"Soja na ankai office Ipy?" dan murmushi yayi da muryan shi mai natsuwa da dadi irin muryan full cikakken namijin nan yace "Ummi na, yes nakai inama cikin office yanzu haka, inaso nai some paper work ne yau, gobe ne zandanyi supervision na various post din mutane" cikeda jin dadi Ummi tace "Masha Allah karka manta katofa addu'a, Allah yakare ka daga shairin makiya, Baffan ku kana fita yana shigowa, yakawo ma rubutu wai kadinga sha" dan lumshe ido yayi irin na gajiya da zancen Baffan nan kafin yadan yatsine fuska yabude ido yace "okay" jin wani kira na shigowa wayanshi yasa yacire wayan daga kunnenshi ya kalli wayan ganin Mu'az ne yasa ya maida wayan kunnenshi yace "Ummi bye, Mu'az na kirana bari na amsa naji" "oh ba jiya jiyan nan yakoma school ba hope badai kudi yakeso ba, karka sake kabashi kudi Sameer kuna bata yaron nan da kudi dayawa jiya babu wanda bai bashi kudi agidan nanba harda Baffan ku" dan murmushi yayi yace "okay Ummi naji bye" "alright son bye" katse wayan yayi yana kokarin kiran Mu'az din kiranshi yakara shigowa hakan yasa ya amsa da wuri. "Mu'az" ya kirashi kai tsaye dan bai fiye wanan wasan ba, daga ta chan bangaren cikin dan dari dari wanda yadau wayan yace "Yaya Sameer Salisu ne, Uhnn Salisu abokin Mu'az na school ajinmu daya" dan shiru Sameer yayi dan Mu'az hardly bama wasu wayanshi meya faru yau abokinshi ya kirashi, kai tsaye yace "uhum Salisu" irin alamun yanajinshi, cikin tsoro tsoro da fargaba yace "Yaya Sameer Mu'az baida Ipy, yanzu haka muna sick Bay tun jiya da daddare baisan inda kanshi yakeba, we tot he will feel better tun jiya saisa bamu kira kowaba but munga har yanzu ciwon kaman ma is getting worse ne" sosai yaji zuciyarshi tabuga dudda all his brothers he is not into them like that dan bayason raini ko kadan but yana sonsu sama da tunanin kowa barinma Mu'az da kusan shine ya raineshi dan lokacin Ummi was battling da rasuwan babansu which Mu'az was a year old daya rasu saisa yakeson yaron danshi yakemai komi a lokacin, natsuwa yayi dan part of training dinshi da akayi tun yana sabon soja shine dakewa and not to panic kodakan mutuwan iyayensu ne, su sojoji ne they're meant to protect lives not to sober, soja jarumi ne maikuma dakakkiyar zuciya, anatse yabashi tambaya kai tsaye. "meke damunshi?" cikin wani irin murya kaman Salisu zaiyi kuka yace "ciwon ciki ne, terribly ciwon ciki" shiru Sameer yayi yana sauraronshi. "juyi kawai yakeyi kaman ana zaremai rai yana kuka sosai shine naga yana yawan mana maganan ka kaine babban yayan su shine nafara kirana danna sanar

dakai" ahankali yace "don't leave his side, ganinan zuwa" katse wayan yayi yatashi ya kalli agogon bango this is 8, akwai meeting dayake dashi by 5 Allah yasa bazaiyi missing meeting dinba, key motarshi yadauka yafito daga office din yasauka kasa, motarshi yabshiga yatada yaja motar da mahaukacin gudu yadau hanyar zaria.

Sha biyu saura minti uku ya shigo Ahmadu Bello University tsabagen mahaukacin gudun dayayi, cikin sickbay ya shiga yay parking yafito sai wani irin kallonshi both yan mata da samari dake shige da fice ake ganin soja real soja ba security ABU ba, wayarshi yadauka yay dialing number Mu'az din ringing daya Salisu yay dauka. "am outside d sick Bay come out" yay maganan authoritatively as usual, ko one minute ba'ayiba wasu samari biyu suka fito kana ganinsu kasan bazasu wuce sa'onin Mu'az dinba, suna hango Sameer da kayan sojoji suka ganeshi, gabansu sai faduwa yake ganin babba ne sosai ashe yayan nasu, ga tsawo ga cika ga kyau dan yamafi Mu'az kyau, yana tsaye inda yake dudda shima kallo daya yamusu yagane sune har suka karaso gabanshi, cikeda girmamawa Salisu yace "Sannu da zuwa Yaya Sameer nine Salisu damukai waya, wanan kuma" yanuna nakusa dashi yace "shine Abdul shima abokin Mu'az ne duk ajinmu daya, muje kaganshi" yay maganan tareda dan satan kallon fuskarshi dan all this while dayake magana yakasa hada ido dashi sabida yanda yake da mugun kwarjini, gaba sukayi yana biyeda su abaya har wani daki dakenan emargency, bude kofa sukayi suka shiga gadaje uku ne adakin amma Mu'az ne kadai on admission ana karamai ruwa sai wani irin juyi yake idanunshi a rufe gam hawayen azaba nafita ta gefe baimasan inda kanshi yakeba, karasawa sukayi ciki ahankali yaja kujeran gaban gadon ya zauna tareda folding hannunshi akirji yana kallon Mu'az din kaman mai shirin gano wani abu yakai almost 3min ahaka sanan yajuyo ya kalli su Salisu dake tsaye agefe yace "bayan ya iso school jiya medame dame kukayi?" Abdul ne yace "bayan ya iso bamuyi komiba munje munyi sallan magrib saina dafa mana abinci zamu faraci kenan wata yar ajinmu takirashi" yanuna Mu'az tace "wai yabata ganmu ba, Mu'az was like bataganmu a inaba? Wai birthday party wata friend dinmu Zee Zainab, wai ancika Zainab nema tace mata takira mu taji, nan tabamu address din inda ake party mukai wanka muka shirya muka tafi......" yay shiru, wani mugun kallo yamusu da saida cikinsu both ya kulle yace "continue, what happen bayan kunje party?" sunnar dakansu sukayi atare Abdul yace "it was a very naughty party, Zainab din dama tadade tanason Mu'az shine shine....." yakasa magana hakan yasa Salisu yay jarumta yace "shine tazo tazauna kan laps din Mu'az , she kissed kumatun shi agaban mu, yana tureta taki sakinshi she hugged him ta zauna duka kan laps dinshi tafara rawa tana twerking ana ihu anamata manni tana gogamai kirjinta akan nashi, mudai muna gefe babu halin muyi magana but naga yanda yake ta keto zufa harta gamamai idanunshi yacika da kwalla sanan ta tashi tatafi shikuma yamike tsaye da sauri yana kokarin samo natsuwarshi yafice muka bishi abaya, sosai yake tafiya da sauri muna kiranshi yaki amsasu the next thing dat we know was ya yanke jiki yafadi ahanya rike da cikinshi and we ended up here" yadade yana kallonsu har suka gama labarin sanan yajuya ahankali batare dayace musu komiba yajuya yay facing Mu'az din dahar lokacin yake nonnokewa idanunshi a kulle hawaye nafita, ahankali yakai both hands dinshi yadaura kan saman goshin shi dayay zufa

ya shafa goshi, Murya chan kasa yakira sunanshi. "Mu'az" wani irin motsi yayi kafin ahankali yabude yan fici ficin idanunshi dasukai mugun ja yadaura su akan Ya Sameer dake sanye da kayan sojoji, ganin Ya Sameer ne da gaske Yas yawani irin tashi ya rungume shi ya fashe da kuka kaman irin yaron dayaga maman shi after a very long time, juyawa su Salisu sukayi suka fita daga dakin dan basu space, sunkai wajen minti biyar kuka yake a jikin Ya Sameer yana pating bayanshi kafin ahankali yadago kai cikin ciwo sosai yace "yaushe kazo Ya Sameer?" tashi Sameer yayi yakarasa wajen new bottle water dayagani yabude batare daya kalleshi ba yace "not quite long" wani katin magani yaciro daga aljihun wandonshi sanan ya ballo guda daya tak dan karami yadawo gaban gadon ya mikamai, karba Mu'az yayi yasha sanan ya karbi ruwan ya ijiye, yasake zama akan kujera yana kallon agogon bango it takes less than 5min ciwon ciki zai sakeshi, ware ido Mu'azu yayi yana shafa cikinshi jin yarage ciwo sosai yace "laaaa Yayan mu ciwon yadena" cikeda surutu irin nashi yace "Ya Sameer wlh nazaci mutuwa zanyi kaji yanda cikina da marana keyi kuwa kaman ana yaki awurin, kaima yana maka haka?" ya tambayi Sameer daya tsareshi da ido yana share fuskan shi dan har yanzu akwai ruwan hawaye kan fuskan dama dama.
"Mu'az" Sameer yakirashi da dan kakkausan murya hakan yasa yadan kalleshi a diddire, "aure kakeso? Tell me the truth, idan aure kakeso zan maka aure after all one semester yarage maka a school kagama, aure kakeso?" da sauri ya girgiza mai kai yadan sunnar dakai dan maganan ta mugun bashi kunya yace "a'a" "then what happen last night?" ahankali yace "Ya Sameer nima bansani ba" cikin yanayin jin haushi yace "don't lie to me Mu'az, I hate lies, kasan I already know everything, so just tell me the truth" murya chan kasa yace "Yaya Sameer Zainab ce, she...she..." yakasa magana yadanyi shiru kafin yace "rawa tayi ajikina, ayanda tayi yasa naji wani mugun sha'awa yakamani kaman zan mutu, saikuma tasakeni shine cikina yafara ciwo daganan kuma sai yanzu dana ganka anan" shiru Sameer yayi yarasa maisa yan gidansu keda wanan masifar ciwon cikin part of abinda yasa Muhammad da Nuru sukai aure kenan, kallon Mu'az yayi yace "you have problem Mu'az, banson kabata rayuwanka, inhar bakada dauriya is better you get married kasami wacce zaka dinga saukar da bukatunka akanta, hakkina ne nakula daku kuma am just like you guys father, that Zainab avoid her any day data kara zuwa inda kake let me know, no more partying you take care of yourself understood?" gyadamai kai yayi ahankali tareda yin murmushi hawaye nataruwa akan idanunshi, ganin haka yasa ahankali Sameer yadaura hannunshi kan goshin shi ya shafa yana kallon fuskarshi, ahankali yace "Ya Sameer kaima haka cikin ka kema ciwo?" dan daure fuska Sameer yayi kafin yatashi daga kan kujeran yace "lemme call your friends u need to see your Doctor kafin natafi" wucewa yayi yabude kofa yafita hakan yasa Mu'az yahau dariya yace "laaa Ya Sameer kunyana yaji wai hahahaha" yahau dariya kaman wani mara lpy, yana cikin dariya aka bude kofa aka shigo hakan yasa ya tsayar da dariyanshi su Salisu ne suka shigo da Ya Sameer dakuma Dr dake magana daya Sameer, musabaha sukai da Dr sanan yabashi prescription sanan yakalli Mu'az yace "atashi atafi gida patient" murmushi Mu'az yayi yadauko daga gadon ahankali da taimakon su Salisu binshi da kallo Sameer yayi ganin yanda yay wani wawan rama this ciwon da baima kai 24hrs ba, fitar da shi waje su Salisu sukayi hakan yasa shida Dr sukai waje suma, sallama sukai da Dr sanan yabude motar ya kalli su Mu'az yace "get in" shi shiga sukayi sai kallonsu ake yakoma gaba ya shiga yatada yaja motar suka fita daga ABU chan wani gida a off kay aka kamamai kasancewa hardly dan 400 level ke samin accommodation a school parking yayi a

kofar gidan duk suka fito kudi mai yawa yaciro ya mikama Salisu yace "thank you, mun gode" sanan ya kalli Mu'az yace "do you need anything Kiddo" turo baki Mu'az yayi ya kalli su Salisu dasukai murmushi jin an kirashi da kiddo da sauri suka juya suka shiga gidan hakan yasa ahankali yazo yay hugging Ya Sameer din yace "I love you Ya Sameer" kanshi ya shafa yace "love you too Kiddo, stop crying whenever you are sick, crying is for the weak and my brother is not week or are you?" dagokai yayi ahankali ya kalli Sameer kafin yya dariya yace "No am not weak" "guud boy, if you need anything always call me okay" gyadamai kai yayi ahankali ko kadan baiso yatafi, hannunshi yakama yarike yace "Ya Sameer kazo muje ciki nadafa ma Indomie" da sauri Sameer yadan yatsine fuska yace "Indomie? Indomie is for children, kune Indomie generation daman" da sauri Mu'az yace "to zan dafama rice and stew" ganin yanda yadamu yasa yace "don't worry next time okay, yanzu I have a meeting to attend by 4, bye" hannu yadagamai hakan yasa ya shiga mota yatada Mu'az namai bye haryabar anguwan, awani masallaci ya tsaya yay azahar a masallacin sanan yafito ya cigaba da journey.

*******

Wasu kyawawan dankunne Mummy ta dauko ta makala mata akunne tace "wow Masha Allah, Autana kinga yanda kikai kyau kuwa yau kowa awurin birthday dinan keza'a dinga kallo" kallon kanta tayi a madubi yanda tai wani mahaukacin kyau dan zama tayi ta chanchara ma kanta makeup dan ta iya yima kanta makeup sosai, tama saman idanunta wasu black smoke eyeshadow daya karama fuskarta kyau abunka da fara, lips dinta tasaka musu wani pink lipstick daya karamusu karanta sukai kyau, tayi eyebrows masu kyau idanunta dudda batasan lashes ba zaka zaci lashes tasa sabida yanda ta taje gashin idon da massacre hakan yasa sukai tsayi sosai, hannu Mummy ta nuna mata alamun komi yayi 👍 sanan tace "to tashi kisa kaya nasan yakusan isowa" tashi tayi da sauri takarasa gaban gadonta inda taciro kayan dazata saka, wani blue jean tadauka tasaka.💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favor you always 💔

✍️ M Shakur

1️⃣5️⃣

Kunna motar yayi yaja yana tafiya ahankali yazo yawuce su ko lura basuyi dashi ba yay gaba da gidan yana hango asalin mutanen cikin gidan dake main rawan dan anbude Gate, rawa kawai suke na hauka definition of real clubbing suke yi abunsu, ga drinks tako ina sunasha, wata mace dan wandon datasaka mai kama da pant ne ta zameshi kasa zuwa wurin gwuiwa ta shiga rawa da bare duwaiwai ta hakan yasa mazan sukayi ihu suka taru akanta suna zuba mata kudi suna shasshafa ass din suna ihu suna DJ DJ give us shake up your bombom, duksun rude, ganin haka wata tafito itama da nonuwanta waje ta hanyar tuge bra ta yar akasa dan attention din yakoma kanta da mugun sauri Sameer ya dauke kai yace "subhanallah!" txt message daya shigo wayanshi ne ya kalla _we are close Lieutenant at kaduna kano express road already_

dan gaba yayi sanan yay reverse yasake wucewa ta kofar gidan yafita daga layin yafito hanya ta yanda dazaran sunzo zasu ganshi ya kashe motar ya saukar da tinted glass din motarshi kasa yana kallon hanya, ko minti biyu baiyiba ya hangosu sun taho motoci biyune na gaban golf ne da maza kusan takwas ke ciki mutum uku a gaba hudu a baya suna fanfala uban gudu kaman motar ambulance, sai dayan vehicle dinkuma nakama mutane ne, horn ya danna musu sau daya hakan yasa suka gane suka karyo kwana suka shiga layin da gudu shima ya kunna motar ya shiga, ta baki bakin layin sukai parking dan basuso su gudu, kashe motar yayi yabude yafito kaman yanda suma suka fito suna sanye da normal kayan gida sai bullet proof jacket maroon color da aka rubuta NDLEA ajiki, musabaha sukai da Sameer kafin yace "musu let's go, no shooting no maltreatment, just catching them dat is all what we are up for" atare dukansu sukace "yes Lieutenant" wani mugun respect suke bashi dan Sameer yayine kawai arayuwa, sukai wajen da gudun su, wata yarinya dake kiss da saurayin ta agaban gate dinne idanunta a lumshe kaman ance ta bude ido tabude ta hango maza da soja na dumfaro su da sauri, fizge bakinta tayi tawani irin kurma uban ihu. "policeeee, everybody runnn!" dudda dukansu are drunk kalmar police kalma ce da duk wani dan shaye shaye is so caution of, sunan kaman kararrawa yake in the mind so it always ring and alarm to their ears, kaman an zubamusu wani irin dawowa hankalin su, firgigit idanunsu ya washe diddirkowa sukai daga motan sukahau gudu wasu suka yanka dajin wajen yayinda yan NDLEA din suka chapke na chapkewa suna dannesu suna kulle musu hannu da disposable plastic handcuff, some na dagasu suna kaisu mota suna rufe su aciki su dawo su kwashi wasu, all this while masu rayen cikin gidan bamasu saniba, cikin gidan Sameer yashiga wasu yan NDLEA guda hudu biye dashi, ihu gidan ya dauka kowa gudu yake, Djs dinma sukabar kayan kidan sukai tatayi, wasu sun rasa inda zamasuyi hakan yabasu ikon kamasu, wasu are running to the fence jumping suna shiga dajin baya suna guduwa, karasawa Sameer yayi yasa hannu ya cisge wayoyin kidan hakan yasa gidan yay tsit.....

Ihun da Chris yaji tako ina da kuka wanda matayen da aka kama keyi yasa yasaki Rahima daya danne ta suna kaukawa dadan ragowan karfin daya rage mata yatashi da sauri dagakan jikinta jin ihu da sahun gudu ga music da kida dake tashi tun dazu shima yay shiru kaman an kashe, labulen window yadan kama ya yaye kadan ya leka wani irin dallo idanu waje yayi hango abokanenshi maza da mata su kusan 15 da aka kamasu an daure musu hannu da disposable plastic handcuff ansasu kneeling down agaban gate ana fitar dasu daga gidan one by one, wasu yan NDLEA guda biyu kuma tsare dasu gudun karsu gudu, dawani irin mugun sauri yasaki labule window jikinshi har rawa yake ya kalli Rahima dake kwance yanda ya barta duk riganta ya chukwuikuye idanunta a lumshe tasaki baki abude tana bacci, hannunta yakama yadaga ta zaune yace "Beautiful stand up let's run" wani irin luuu Rahima tayi takoma kwance tana buge hannunshi cikeda masifa, tsaki yaja da sauri yadauki key motarshi daga kan table yabude kofan ahankali gudun karyay kara asirinshi ya tonu sanan ya leko da kanshi kadan dan duba ko akwai mutane a falon, ganin babu kowa a falon yasa da gudu yafito yay hanyar kitchen sabida yabita backyard fence ya dirka ta baya ya arce daidai lokacin Sameer ya shigo flat din, ganin Chris yafito daga wani daki da gudu yayi ta kitchen yasa yabishi da gudu, daidai ya shiga kitchen wani officer NDLEA dayaji fitowanshi ya labe abayan kofan gudun karya ganshi yafito ya tadiyeshi yafadi timm akasa, ihu Chris yayi dan yaji zafin faduwan yace "officer I didn't do anything naaa, we are just having birthday party fa, why u wan arrest me en? Wetin I do naaa?" dagashi officer yayi bayan ya kulle hannayen nashi cikin tsawa yace "my friend shut up, we we are busy having sleepless night to make sure youth like you stop all this kind of life and be serious with your education so that u guys will have a bright future but you guys are here busy taking what is killing you and killing your future as well, let's go my friend" ya fincikeshi sukabi ta gefen Sameer dayay irin tsayuwan sojojin nan yana kallonsu suka fita sanan yadaura idanunshi akan dakin dayaga Chris yafito daga ciki kafin ahankali yadaga kafa yafara tafiya daidai boot dinshi na making sound yakarasa wurin dakin da Chris yafito daga ciki, yadade yana kallon kofan yanabin rubuce rubuce da Zane zanen dake jikin kofan da kallo zanen shisha pot dasu cigarette ne a jikin kofan katakon da akai da biro, ahankali yazare hannunshi daga bayanshi yakama handle din kofan yabude kofan wani irin warin wiwi da sauransu ne suka dakanmai hanci hakan yasa ya yatsine fuska kafin idanunshi su sauka kan Rahima dake kwance tana dirkan baccinta hankalinta kwance, kallo daya yamata yagane musulma ce ita, ita kadaice musulman dayagani tunda aka fara fito da matayen dake wurin, wani officer ne ya shigo dakin yana tahowa wajen Sameer yace "da saura ne Lieutenant?" gyadamai kai Sameer yayi kafin ya nunamai cikin dakin dayake tsaye a gabanshi da sauri officer ya shiga cikin dakin yay inda Rahima ke kwance, hannu daya yasa ya fincikota hakan yasa ta tashi tsaye luu kaman zata fadi, turo baki tayi sosai idanunta arufe cikin fushi da shagwaba in a very slow way tace "leave me aloneeeeeeee Chris" tai baya luuu takoma zata fada kan kujeran a mugun buge, sake fincikota officer yayi yana kokarin kama hannun ta tabaya ta fizge kaman zatai fada dashi tana layi, cikin slow tsiwa irin na wanda ya bugun nan tace "leave me kona dalla maka mari, I want to shower, uhmmmm wanka nake kadena damuna, kawomin ruwa in sirka ruwan zafin Ya Siddiqa" tawani irin zube akasa wurin kafin ta daura kanta kan table din dasu shisha pot kekai tacigaba da bacci, officer zai kara kamota akaro na Uku Sameer yace "wait!" tsayawa chak officer yayi ya kalli Sameer din dahar lokacin bai shigo dakinba, takowa yayi ya shigo cikin dakin, babban bottle water Swan daya gani kan side drawer gadon dakin yadauka ya shiga budewa yana

tahowa inda take kwance gaban kujera ta daura kanta kan table tana bacci tana surutai kasa kasa, matsamai Officer yayi yakoma baya, tsayawa Sameer yay akanta ya cillar da marfin goran gefe, daga goran sama yay da hannu daya ya shiga kwararo mata ruwa kaman ana mata fitsari akai yana sauka saman dankwalinta, dudda she was damn high amma saukan ruwa dataji akanta yana sauka kan fuskarta wasu na shiga kunnuwanta, wasu na gangarawa wuyan ta zuwa cikin riganta yasa ta mugun zabura kaman wacce ta zare ta mike tsaye tana shashare fuska tana wanan nishin da mutum keyi in ruwan sanyi na tabashi tana sauke ajiyan zuciya tana share fuska tana kokarin ta bude idanu takasa sabida yanda ruwan ke saukowa, dudda ta tsaya agabanshi tana shashafa fuska trying to open her eyes baisa yadena kwara mata ruwan ba harsaida ya juyemata ruwan goran tass sanan ya tsaya, wani irin ajiyan zuciya ta sauke tasa hannayenta duka biyu ta share fuskanta ruwa na diddiga harta cikin riganta, ahankali ta janye hannunta daga kan fuskar nata cikeda bala'i tace "uban wayace kazubamin ruwan sanyi ajikinta eh?" sanan tabude idanun nata tass ta saukesu kan fararen kafafun ta dasuka jiku da ruwa tana kallon wani boot army green dake gab da kafafun nata ga dilli dillin ruwa akan boot din shima, tundaga kan takalmin shi take binshi da kallo har zuwa kan cikinshi zuwa kirjinshi da a iya nan tsawonta ya tsaya kafin ta daga kanta da fararen idanunta dat look moist tsabagen ruwan dasuka sha ta daura dara daran idanunta akan fuskarshi kaman yanda shima yake kallonta fuskarshi babu alamun Rahama balle dariya, wani irin faduwa gabanta yayi ganin wani babban soja a gabanta gashi da tsayi bakin mutum, kasa motsi tayi balle ma tasake yunkurin magana batare daya janye idanunshi daga kanta ba yawani irin cillar da goran ruwan dayagama juyemata cikin kakkausar murya yace "take her away Officer" da sauri officer yakaraso wajen yana kama hannunta ta baya yana handcufff nata Sameer kuma yajuya yana takun nan kaman wani bijimin zaki yafita daga dakin, saida yafita daga dakin kaman anbude mata baki ta shiga kokawa da officer tace "me haka kakesamin a hannu ina zaku kaini? Su waye ku mena muku? Ina zaku kaini eh? Chris" ta kwalama Chris kira.

_Zan baku another page anjima koda bayawa, ina bimuku book din daki daki ne VIPs, I've been busy yau wlh, sababbin kajina nata mutuwa, guda goma shadaya sun mutu yau, cuta takamasu, nakira Dr wai sanyine, sauran ma don't look good at all, wlh kaman zanyi kuka, dan Allah kumusu addu'a banso nai asara, gobe fa zamasu cika sati daya da sayosu😭 innalillahi wa innailaihi raji'un_
💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favor you always 💔

✍️ M Shakur

1️⃣6️⃣

Janta officer yayi suka fito daga dakin yace "Chris can't save you lady, u are arrested sabida ankamaki kina shaye shayen miyagun kwayoyi da gwamnati tahana sha sabida cutar da halakar, da wulakantar da rayuwar dan adam datakeyi, headquarter mu zamu kaiki yanzu haka" wani irin uban ihu ta kurma tace "wlh kasakeni ni baza ka kaini ko inaba Mummy" tafashe da kuka sosai tana kokarin fizge kanta tana turje turje tana kiran Mummy. "wlh kasakeni nibabu abinda namuku, leave me alone, Mummyyyy" tasake kwalama Mummy kira tana kuka sosai, janta yayi da karfi da yaji yafito da ita compound din tana kuka tunda aka haifeta bata taba shiga tashin hankali irin wanan ba, bama tasan cewa akwai tashin hankali hakaba aduniyan nan daga zuwanta birthday yan sanda ne koyan menene sunwani kamata, Sameer dawasu officer guda biyune kawai a compound din yana musu magana, sauran suna waje wurin mota tsare da yaran dasuka kama, yanda Rahima ke kuka sosai tana kurma uban ihu tana kwalama Mummy kira yasa yadago kanshi ya kallesu, ko'ina na jikinta bari yake har lokacin dan kwalin kanta da riganta duk ajike ne sabida ruwan daya kwaramata tana kuka, babu abinda take tunawa sai maganganun Mummy karta sake tai abinda zaisa aganosu kokuma tai abinda zai tonamusu asiri idan Dady yaji ankamata ai saiya luma mata wuka aciki tamutu dama bayasonta yafison su Siddiqa. "dan Allah kasakeni natafi wurin Mummy na, ni wlh banmuku komiba, please please karku tafi dani kaji Abba na zai kasheni ne" zufa officer ya share da hannu daya tsabagen yanda take bashi wahala yasa yake zufa yace "ashe kinsan abinda kikeyi baida kyau, muje" janta yayi ya fitar da ita daga gidan zuwa inda sukai parking yay mota da ita, jefata yay cikin motan ganin irin mutanen dake cikin motan da aka kakkama sai warin shaye shaye suke yasa ta kifa kanta akan cinyarta tahau kuka sosai kaman za'a kasheta, Chris da batama lurada shi bane yanachan gaba tsaye yakutso kai yazo ya tsaya akanta yana kallonta tabashi tausayi dan yasan tadamu duk ta tsure, ahankali yace "Hey Beautiful a......." "don't call me beautiful I hate you Chris" tafada tana tashi tsaye daga kan kujeran cikeda masifa tana kuka sosai, tace "just thank God my hands aren't free da wlh saina waska maka mari mai gishiri, a dog like you" cikeda masifa dan shima he feels furious and frustrated as well  yace "I love and respect you beautiful but I won't have you calling me names, I am not gonna tolerate that am 25 nasan nabaki nothing less than 5yrs so pay some Goddamn respect u lousy hausa spoilt brat" cikin kuka sosai da shegen muryan ta mai bala'in zaki da dadi tace "u are the lousy one hypocrite kawai and I said it you are a dog" azuciye yawani irin bugamata kanshi a goshi da karfi sabida yanda hannunshi suke a daure, baya luuu tayi tafadi a daidai baki bakin motar kaman wacce

iska ya diva tai wani irin tumble kafanta ya malkwade tafado daga motar zuwa kasa daidai lokacin Sameer da all the eight NDLEA officers sun karaso wajen akan idanunsu ya bugamata kai a goshi, daidai kafan Sameer tafado tai wani irin kara goshinta na jini bayanta ya mugun bugu tafashe da kuka idanunta na juyawa, daya daga cikin officers ne ya shiga cikin motar, finciko Chris waje yayi ya zubamai Mari yace "how dare you hit a woman?" cikin fushi dajin haushin yanda officer ya marai agaban all his friends yace "Sir is personal issues besides she's my girlfriend you don't have to interfere" daya daga cikin officer ne  yace "ahhh yaro kaidan iskane naga alama kanka na hayaki, kafasama yarinya goshi sanan kama fadamana we don't have to interfere" kulkin dake jikinshi ya zaro shima dayan haka suka shiga dukanshi yana ihu saida sukamai lilis yana ihu duk Sameer na kallonsu baice musu uppan ba sanan sukazo inda Rahima take agaban Sameer tana zaune tana kuka sosai, tana taba goshinta dake jini tana kallon jinin a hannunta tana kara kecewa da kuka kaman zata shida, daya daga cikin officers dinne yace "ke tashi ki shiga mota mukakai head quarter za'a dubaki?" makemusu kafada tayi tana kuka tace "ni yanzu zakuyi treating dina I can't feel my leg at all, am bleeding I don't want to die now pls" bushewa da dariya all the 8 officers sukayi daya daga cikinsu yace "you don't want to die shine kike shaye shaye kina shan su shisha da codeine that kills faster than anything you could think of, my friend stand up" yay maganan yana mikar da ita tsaye, wani irin ihu jin yanda kafarta yamata mugun ciwo tai tangal tangal zata fadi akasa ta daga kafarta daya sama tai baya hakan yasa Sameer dake bayanta yatare ta tafado in his arms, atsorace ta juyo dakai ta kallai tana kuka  hawaye na bulbulowa ta gefen  idanunta gabanta nafaduwa kaman zata mutu, dauke idanunshi yayi daga kallon datakemai kaman wacce keson karanta abu ahankali yadauketa kaman yadau paper da sauri tai wrapping hanuwanta around his neck, yana kallon gabanshi yake tafiya daidai harya karasa da ita wurin motar dasuke ciki, da ido daya yama wayanda aka kaman alamun su matsa, matsawa sukayi ya ijiyeta akan dan kujeran bencin wajen tana kuka ciki ciki hawaye na bulbulowa kaman famfo, kafarta na dama ya kama, hannu yasa yazare White takalmin dake kafarta dakeda dan tsini ya ijiye agefe yana kallon yanda ankle looks so reddish gawani leg chain data daura a kafar daya zubama ido for a while sai kyalli take abinku da farar fata, kafan harya kumbura kashin gefen ankle din yadawo tagaban kafan, wani irin fashewa da kuka tayi tana kallon kafar tace "innalillahi kululun kafana yadawo gaba shikenan zan mutu yau" ta fashe da kuka sosai, dariya officers din suka shigayi suna mata dariya, daga kafar yayi yarike kowa na cikin motar na kallonsu barinma Chris dayasan aikinshi ne, wrist din kafan yarike gam kafin yakama foot dinta yay wani irin twisting dayasa ta kwala mahaukacin ihu kaman ta sume tafado daga kan kujeran tana dukan hannun Sameer din tace "kabari dan Allah, wayyo Allah na Mummy na"  sakin kafar yayi ahankali batare daya kalletaba yajuya ya kalli officers din yace "Dr should check the leg when u get to the headquarter, see you guys next time" yajuya yawuce ya shiga motarshi, shiga motocin su suma officers din sukayi, Officer biyu suka tsaya abaya tareda yan shaye shayen gudun karsuyi jumping su shiga titi in attempt to excape sukai headquarter dasu shikuma Sameer yay gida dan ya mugun gaji.

Parking yayi a compound dinsu yana kallon motar Nuru alamun yazo gida kenan baiyi mamaki

ba dan yasan dukansu daga Nuru har Muhammad kullum da yamma insun taso daga aiki saisun biyo sun gaida Ummi dan da safe basa iya zuwa sabida zuwa aiki, bayan sunyi magrib saisuma Ummi Sallama su tafi gidajen su, motar Nuru dayagani yasa yagane Muhammad bai riga yataso daga wajen aikinshiba, flat dinshi yawuce dan he wants to shower kafin yaje wurin Ummi, wurin fridge dinshi yayi dake falon budewa yayi yadauko bottle water yabude yakafa abaki, bude kofanshi da akayi yasa yadan juyo while drinking the water ganin Nuru ne yasa yacigaba da shan ruwan, zare goran yayi daga baki hakan yasa Nuru daya karaso wajen yace "sannu da dawowa yayan mu ya aiki?" "Alhamdulillah fine, Muhammad bai dawoba?" gyadamai kai Nuru yayi yace "eh baidawo ba, wurinka nazo Ya Sameer amma naga you want to shower yanzu ka shigo bari na jiraka" dan murmushi yamai yace "alright give me just 5min okay" gyadamai kai Nuru yayi hakan yasa yawuce yay bedroom dinshi Nuru yabishi da kallo yana mugun son wanshi Sameer saidai bakajin cikinshi tun yana gani kaman kawai Ya Sameer baiso yay aurene har wakan Ummi shima yasoma zama a kunnenshi to the extend yanzu yasoma believing maybe wani matsala yakedashi saisa baya sha'awan auren according to Ummi.

Bude fridge din yayi yadauko vita milk yasa opener ya bude yamaida fridge din yarufe yadawo kan kujera yazauna yanasha yana kallon news.

Almost 10min Sameer yabata sanan yafito falon sanye da bathrobe fari ya zauna kusada Nuru yace "je kitchen ka hadamin coffee Noor" tashi Nuru yayi da sauri yace "to yayan mu" kitchen dinshi ya shiga that is so clean kana ganin kitchen din kasan ba'a cika amfani dashiba, cikin 5min yahada mai coffee yazubamai a mug yasa spoon da sugar yafito yakawo mai, karba yayi yace "thank you" ya ijiye dan yasan da zafi, kafin yadauka sipping kadan yayi ya ijiye yadan daga gira daya sama yace "not bad" fashewa da dariya Nuru yayi yace "kai Ya Sameer nai kokari fa sosai" shima dan murmushi yayi yace "yeah was just kidding, its actually taste good thumbs up" murmushi dukasu sukayi sanan yace "alright, let's talk, what is the matter?" dan shiru Nuru yayi kafin ahankali yace "Yaya Sameer yesterday I was busy inata nazarin abubuwa da dama" gyadamai kai Sameer yayi yana sake kai Coffee bakinshi giving him his fool attention, ganin haka yasa Nuru yace "uhmm Ya Sameer why don't you marry Asiya? Naga tana sonka"

Wani irin kallo Sameer yamai saida gabanshi yafadi da sauri yace "I mean bawai tana sonka ba but naga kuna shiri taku tazo daya please understand me kaji yayan mu, she is our cousin and tanada natsuwa, tana 300 level a school ga ilimin islamiyya what else?" "get out!" yadakama Nuru tsawan da saida yasa ya firgita, cikin fushi yace "u think sabida kai aure kanada gut din tunkarana kamin maganan aure harda fadamin wanda zan aura my sister Asiya, yaushe aka haifi Asiya? Is Asiya even ripe for marriage, you know me you know what I hate banson raini Noor, watch your tongue, now get out" tashi Nuru yayi ahankali dukyay wani iri he feel awful duk laifin Ummi ne saida ya gayamata yafi so tamai maganan da kanta bata aikoshi in disguise ba,

ahankali yace "I'm sorry Yaya Sameer kayakuri" da yatsa Sameer yanunamai kofa babu alamun wasa kan idanunshi hakan yasa yajuya yafita da sauri, jingina yayi da kujera ya lumshe ido yana sauke ajiyan zuciya ranshi yabaci sosai. Karan da wayanshi yayi na shigowan sako yasa yadau wayar NDLEA ne yaga sunmai message.
" _Lieutenant Chairman asked us to call you, something come up u have to come to the headquarter please_ ".
💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favor you always 💔

✍️ M Shakur

1️⃣4️⃣

Wani top dinta na Dorothy perkins white and sky blue ne shima long sleeve tazaro daga hanger tasaka, rigan yadan saukar mata dan yarufe mata bombom, wani long fashion necklace tasaka daya saukar mata kan rigan, sanan tadau veil dinta white zata yafa da sauri Mummy tace "no kiyi wanan hadadden daurin nan dakika iya" murmushi tayi harda dan gudunta takoma gaban madubi ta zauna ta shiga daurin, tsaf tai daurin dayadan bada v shape ta gaban goshinta ya mugun mata kyau, wani takalmi mara tsini sosai Mummy ta dauko mata white karba tayi tace "laaaa Mummy na ya akayi kikasan shi zan sa" dariya Mummy tayi tace "I know your dressing humor" murmushi tayi ta shiga saka takalmin Mummy sai kallonta take harta gama ta mike tsaye Mummy tabita da kallo ba karamin kyau tayiba kaman wata celebrity, ita kanta jikin Rahima na mugun burgeta batada wanan girman jikin, she looks small, batada wani tsayin kirki bata da kiban kirki but her organs are so full, bumpy and super package, tanada hips da boobs bana wasaba gatada yar karaman kafa, ga karamin jiki, irin matayen nanne da ake kirada too perfect yan charass chass, wayarta ne yay ringing hakan yasa Mummy tadauko wayan dake kan gado tana kallon screen din tace "gashinan ya iso, yi sauri feffesa turarukan ki" fesa turare ta shigayi masu bala'in kamshi sanan ta karbi wayan daga hannunta ta sa akunne. Cikin wani murya mai dadi Chris yace "Hi Beautiful, am outside" ayangance tadan murguda baki tareda juya ido tace "okay am coming" baki Mummy takama tace "Autaaaa" fashewa da dariya tayi tafada jikin Mummy, Mummy tace "kinga shida tamiki agidan nan dudda yau Abban ki baya gari

amma dai kidawo da wuri kinji, muje narakaki nima naga Chris dinan da babyna ketamin maganan shi tun jiya" tana rikeda wayanta suka fito tareda Mummy, mayafi Mummy tadauko afalo sanan suka fito tare su Siddiqa na falo binsu sukayi da kallo barin Rahima dataci shegen gayu kaman zata gasan kyau tana balla musu harara, har wajen Gate Mummy tarakata da hannu tanuna ma Mummy motar Chris dake pake a gab da gate dinsu karasawa sukayi ganinta tareda wata yasa Chris yabude mota yafito yaci gayu na bala'i dan gemunshi da ajiyan tagani bakine yau taga yakoma dark blue yama gemun tiri kalan sneakers din kafarshi yasa wani crazy wando daya babbarke gawata shegen sarkan Cross awuyan shi yayi askin nan dakalin shaidan yana dan tauna cingum yana murmushi, hannu yamikama Mummy yace "watsupp Mummy, afternoon" gyadamai kai Mummy tayi ta rungume hannunta akirji kaman mai shirin salla tace "sannu Chris birthday boy, see my daughter, you guys should have maddd fun okay, but bring her back before 6" wani irin dariya Chris yayi harda dan juyawa ya kalli Rahima daketa kallonshi yace "your Mummy is a sabi woman, alright Mum we will have fun Chris promise you that" kashemai ido Mummy tayi batare da Rahima ta luraba dan kallon Chriss take, murmushi yayi ya kalli Rahima yace "let's go beautiful muje nabude miki ki shiga" gaba ta shiga yana biyeda ita hakan yabashi daman juyowa shima ya kashema Mummy ido tareda lashe lips dinshi, saida yasata ciki sanan ya zagayo yana dagama Mummy hannu ya shiga ciki ya kunna motar yaja duk sunama Mummy bye, ajiyan zuciya Mummy ta sauke sanan tajuya takoma cikin gida da Siddiqa taci karo awurin Gate idanunta sunyi jaaa sosai tsabagen fushi, babu ko alamun tsoro tace "wlh Mummy saina fadama Abba duk abinda kikeyi, keke bata Rahima bakowa ba, yanzu Mummy ba abin Rahima takawo miki katon arne, arnen ma wanan dan iska ne amatsayin saurayi ki fatattake shiba shine zaki barsu yafita kinsan inda zai kaita? Mummy mufa matane, Rahima mace ce, very fragile ma kuwa, batada hankali wat if yamata wani abu? Wat if yay raping nata? Me zaki cema Abba eh? Mummy! " takirata da karfi looking so pain, wani banzan kallo Mummy tamata tace "ki rubuta ki ijiye duk randa zaki gayama baban ku wlh wlh aranan kika fita daga sahun y'ay'ana na cikina saidai kije kinemo wata uwar" tai tsaki tawuce tabar wajen.

Sundanyi nisa a hanya yajuyo ya kalleta kaman yanda itama ta kallai yace "beautiful you look very pretty today, I love every bit of this dressing" wani irin juyamai idanu tayi tace "thank you kaima kai kyau no banda wanan blue beard din" murmushi yayi yacigaba da tuki sai danne dannen waya takeyi kusan tafiyan minti arba'in sukayi suka kai wani gida dake nan kan titin kaduna express road za'ai kwana adan shiga dajin but ko tafiyan minti uku bazakayi da shigaba zakaga tafkeken gida, gidane mai white gate, parking yayi akofar gidan yabude mota yafito sanan ya zagayo ta side dinta yabude mata kofan, fitowa tayi ta tsaya tana kallon ko ina, hannunshi yamika zai rike nata da sauri ta janye tace "ni karka rikeni" dan juya ido yayi sanan ya rufe motar yakarasa gaban Gate din bude Gate din yay ya shiga ciki tana biye dashi, babban

tsakar gida ne da aka gyara ga kayan dj duk anyi setting up ga balloons ga kujerun da aka jera dayawa na baki, turo baki tayi dan yasoma dama zama jikinta yin hakan tace "ina mutanen to?" murmushi yayi yace "just few of my friends are inside with their babes chilling you know, the dj sun tafi cikin gari dauko some stuff, the main party zai fara dan anjima insun dawo let's go" binshi tayi ciki tana kallon ko ina har zuwa dan flat daya kachal dayake big compound din tun kafin su shiga sukejin warin wiwi, bude kofan yayi ya shiga yana mata alamun ta shigo itama shiga tayi wasu mazane guda uku tareda yan matan su dasukaci uban attachment suna smoking weed ga shisha pot agabansu dawasu kwalaban abubuwa, yatsine fuska Rahima tayi ta juya zata fita da sauri yakamo hannunta yace "No beautiful don't go, I promise you will have fun today, beside we we are not sitting here am taking u inside" yay maganan yana janta ahankali zuwa ciki batare daya kalli abokan ba suma suka share shi basu cemai komi ba, wani daki yabude dakin gado ne da kujera a gyare tsaf ga TV dake aiki, zaunar da ita yayi kan kujera yace "sit here, bari naje na kawo mana abubuwan mu let's have fun, don't worry I will take care of you kinji beautiful, now smile for you" dan murmushi tayi ganin duk yanda yabi yadamu sabida yaga ta daure fuska, tashi yayi yafita zuwa mota, wani babban basket yadauko dake dauke da shisha pot guda uku dawasu kwalabai ya shigo gidan, yay dakin datake, aijiyewa yayi a gabanta sanan ya maida kofan yarufe yadawo kusada ita ya zauna ya fito da shisha pot daya ya daura akan table din dake gaban kujeran dasuke kai yace "do you do shisha Beautiful" girgixa mai kai tayi hakan yasa yay dan dariya yace "what! kinyi missing, Shisha tsabagen dadinshi jizakiyi kaman kimutu barinma yanda na zuba harizona aciki hulala baby, yay maganan yana ciro wasu kwalabe guda biyu suma yadaura agabansu yace "this are mixture of codeine and a lil bit of crack, crack din just half teaspoon da kyar my guy yabarmin shi 50k" kallonshi tayi tace "menene crack din?" cikin gurbataccen hausan shi yace "Yayan Cocaine ne Crack, Cocaine elder brother kenan Beautiful in kinsha crack inspiration ne kawai zaita zuwan miki baby, wani irin dadi da murna zakiji, feeling kaman ke kadaine aduniyan nan, bakida matsala ko daya, have a sip a feel it" yamika mata kwalban daya bude karba tayi tana kallon bakinshi kafin ahankali ta kurba, lashe baki tayi tadanyi murmushi tace "laaaa dadi kuwan" murmushi yayi yace "yes da madara madara acrack din sanan ga codeine saisa kikaji yay dadi but don't take much this is your first time" sake kurba tayi, zata sake maidawa baki yace "wowowo is okay, gwara kima shisha wanan shan, this is big for you dan crack can kill you wlh, oya let's see how many kalan buso hayaki kika iya let's play a game" yay magana yana bata mouthpiece din shishan, shima ya rike nashi mouthpiece din, yace "let's do it in one, two, annndddd three" atare suka zuko shishan kafin su janye daga baki, shiya fara mata alamu ta kalleshi hakan yasa ta kallai yawani irin huro hayakin daga hancin shi in style din circle circle, ware ido tayi kafin ta huro nata hayakin ta baki yay wani irin saman dakin kaman an bude teargas tafi ya shiga mata yace "yayyy beautiful u are really smart, ya kikaji shishan strawberry flavour ne yahadu ko" murmushi tayi bamata kulashi ba tsabagen yanda shishan yamata dadi takara kaiwa bakinta, murmushi yayi ya dauko kara daya na weed yaciro lighter daga aljihun shi ya kyasta sanan ya maida lighter yakai weed din bakinshi ya zuka hakan yasa ta kallai tana huro hayakin shishan, karan weed din yamika mata yace "zaki sha?" hararan shi tayi tace "give me a new one" dauko wani yayi ya kunna mata yabata karba tayi tashaka ta fuzar sanan tasha shishan tana murmushi today is just the best day of her life, inda ace su Ya Siddiqa sundan dadin abin nan da saisun saye duka weed da codeine din duniya gaba daya, lumshe ido tayi ta wani irin jingina da

bango bacci nawani neman kwasheta dan abubuwan sun soma bugar da ita tun tana bashi amsar maganan shi harta zo bamataji da kyau, zata karakai dan gutsuren weed din bakinta Chris ya karba da sauri da mouthpiece din shishan ya ijiye su kan table yace "hey beautiful, you have had enough, don't want you to pass out is okay" dan turo baki tayi cikeda rashin jin dadi murya chan kasa da bata fita sosai, very slow tace "give me the shisha" hannunshi yasa ya shafa soft kumatunta yana kallon yanda take lumlumshe ido murya chan kasa cikeda sonta yace "you are the first Muslim girl I've ever loved in my life my god u are so beautiful, so pretty" dan bude ido tayi kadan ta hararai kafin tasa hannu ta kabar da hannunshi dake kan kumatun ta, cikin magagin bacci da maye tace "stop touching me" dan kara matsowa kusada ita sosai yayi yanajin tashin kida alamun mutane sun fara zuwa kenan dayake ansan yana tareda babe saisa ba'a zo an tadashi ba, matsowa kusada ita sosai yayi ya manna ma kumatun ta kiss ahankali yace "baby stand up mu kwanta akan gado, your Mum said we should have fun so let's have fun" yay maganan yana kokarin daga ta tureshi tayi batare data bude idoba tace "leave me alone" ganin tanada gardama and she is a lil bit stubborn yasa yawani irin fizgota jikinshi, da sauri ta bude idanunta dasukai jajir tana kokarin tureshi amma yaki barinta wani irin ihu ta kurma amma ko kadan ba'a jinta sabida karan kidan dake tashi agidan, kama fuskarta yayi tana kokarin kwancewa ya manna mata kiss abaki ya shiga laluban boobs dinta da tuntuni suke idanunshi baida burin dayawuce yaga yataba........

Wuraren four ya shigo Abuja hakan yasa yakara gudu sabida yakamata yay attending meeting dinan is his first meeting as lieutenant, kuma meeting ne da harda Chief of staff din Nigeria akan how to ensure security a Nigeria, yakai ta wuraren express road din Abuja wayarshi ya shiga kara, kallon wayan yayi while driving ganin Marshal barobaro kan screen yasa yarage gudun motarshi yagangara gefen hanya yay parking tareda daukar wayar yay answering call din tareda kamewa yace "Sir!" daga tachan bangaren Marshal yace "Lieutenant that meeting is not going to hold, am in the airport going out of country right now, until I get back" anatse yace "I wish you journey mercy sir" "thank you Lieutenant" ya katse wayan, ajiyan zuciya ya sauke tareda sauke ajiyan zuciya Allah nasonshi sosai dudda ya iso Abuja inda ace akwai meeting din babu yanda zaiyi yakai Barrack batare dayay latti ba, yin latti kuma is considered as unethical aspect of his profession, wani mahaukacin sauti daya daki dodon kunnenshi yasa yabude ido da sauri motace dake dauke da saurayi guda daya sai yan mata biyu akai dasuka sha attachment suna cikin wanan motar mara marfin sama, saurayin na driving da hannu daya yana shan shisha da hannu daya, bin motar yay da kallo hartai dan gaba kadan sanan tawani sha kwana, shi mutum ne dazaran mind dinshi yabashi yay abu yake, hakanan suna wucewa yaji kawai yanaso yabisu, tada motar yayi yakarasa har daidai inda yaga sunyi kwana ya kalli layin motoci yagani pake a wurin daban daban hakan yasa yay kwana ya shiga layin tayoyin motarashi sai taka kwalban su tutolyin yake, kashe motar yayi bayan yay parking abayan wata mota camry dayagani awurin yanajin tashin kida ga samari cike a awajen wasu kan saman

mota suna zukan taba, wasu kuma na shan shisha ga mata gefensu, wasu rike da kwallaben giyoyi, ga ihu dayaji yana tashi tako ina, kashe motar yayi yana kallon yaran yace "why are all this Indomie generation so stubborn? Me sukeji a shaye shaye bayan clearly yana rubuce ajikin taba and other stuff cewa shaye shaye na kisa da wuri? Why are children taking what is harmful to their health" dan tsaki yaja yadau wayarshi ya shiga turama number dayay saving da NDLEA sako.
_"am at kaduna-kano express road, some bunch of gang are partying with loud music on and using hard substances and other illicit drugs which according to constitutional law of Nigeria clearly state that they're illegal and as such anyone caught on such act must go for six month rehab, you need to invade into this premises and investigate properly with immediate effect, let's all come together and make Nigeria great again"_.
*Lieutenant Sameer Simran Sameer*

Ko minti daya baiyi da tura sakon ba sukayo reply "stay there lieutenant, we are on our way", gyara zama yayi yana kallonsu dudda su hankalin su bayama kanshi shaye shayensu kawai suke suna rawa suna wasa da yan matansu dabasu da banbanci da karuwai suna turenci.💫
*_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favor you always 💔

✍️ M Shakur

1️⃣7️⃣

Tashi yayi yawuce bedroom dinshi ranshi abace wasu kananun kaya ya dauko, Black jean yasaka sai wata Ash color riga short sleeve mai gajeren hannu yasaka, rigan nada V neck daya bayyanar da kwantaccen gashin kirjinshi, rigan ta kamashi sosai, kaman rigan zata barke ajikinshi sabida yanda ta bayyanar da kiranshi na full packs man, Black jacket yadauka yadaura kan rigan yasaka wani boot baki yadau car key dinshi, kana ganinshi kaga soja yafito daga flat dinshi yaso ya shiga wajen Ummi but no Inya dawo yaje, he don't want to waste anytime, motarshi ya shige yaja tareda danna horn mai gadi ya budemai gate yabar gidan.

Tashi Ummi tayi daga jikin window bayan taga taga fitanshi jikinta ya mugun yin sanyi takoma kan gado ta zauna ta buga uban tagumi cikeda damuwa ta daga hannayenta sama tace "wanan wani irin jarabawa ne Ya Allah meke damun Sameer ne dako kadan mace bata gabanshi?" tai dan shiru tasa hannu tai maza ta goge hawayen dake shirin zubomata, tasowa Nuru yayi yazo kusada ita yabata side hug cikeda damuwa yace "Ummi kidena damuwa okay, kidinga mai addu'a in sha Allahu har jikokin shi zaki gani nan bada jimawa ba kuwan" fuskar Nuru ta kalla tace "anya? Kaduba pa am sure sabida maganin dana gayamishi Baffa shi yakawomai ne yau da safe yasa yaki shigowa dan baisoma yasha, Noor ya zanyi da raina eh? Yayanku fa Noor duk ya girmeku nesa ba kusa ba, yabaka almost 8yrs but look at you now da Nabila batai having miscarriage ba da kanada yara biyu aduniya, I tot yanda na kawo maganan Asiya he will accept da gudu sabida cousin dinshi ce kuma naga suna shiri yarinyar na sonshi sosai, bazai wani sha wuyan neman aure ba dan da gudu Baffa zai bashi ita amma kalli abinda yama" ahankali Nuru yace "Ummi kibar maganan Asiyan nan, it won't work, ai dama tun kafin kiturani na gayamiki kice Yaya Sameer ya auri Asiya ai kaman kin kara koranshi daga zancen auren ne, Yaya Sameer dason girma tsiya inya auri Asiya ai kaman ya yankin ma kanshi ticket din raini ne, ni nasan dama bazai taba koda da wasa he will not accept maganan nan, kawai kiyitamai addu'a Ummi what goes around comes around, Yaya Sameer zaiyi aure one day one day" cikeda damuwa sosai Ummi tace "Ya Allah, Ya Allah kadubi lamarin nan nawa, Ya Allah ka karkata zuciyan Sameer zuwaga wata mace, Ya Allah kahadashi da wacce zaiso sosai, Allah ka aurarmin da yaron nan badanni ba badan halina ba" tasake share hawaye daya zubo mata rungumeta Nuru yayi yace "is okay Ummi ya isa hakanan" haka yacigaba da lallashinta har Muhammad shima yadawo duk suka taru suna bama maman nasu baki harsuka samu ta dawo normal tadan wartsake tabiye musu sunata hira.

Tunda aka shigo dasu headquarter anan reception aka zubesu duk wanda zai wuce saiya kallesu, gabaki dayansu akasa suka zauna bama abasu kujera ba, Rahima tai kuka har idanunta sun kumbura kaman zaka taba jini yafito, daukan sunayen su akayi gabaki dayan su saiga wata mata ta taho da kayan first aid box a hannunta tareda daya daga cikin officers din dasuka kawo su suka taho gaban Rahima.  Rahima yanuna mata yace "ga wacce batason ta mutun nan amma take shaye shaye, duba kafan Dr, tai targade Lieutenant ya gyara mata dazu" murmushi Dr tayi ta tsugunna a gabanta tana tattaba kafan ahankali kafin ta bude first aid kit din tadauko wani man zafi ta shafa mata sama sama tace "ya gyaru kamai muscles pain take having, wanan balm din kuma will kill it nan bada jimawa ba" sakin kafan tayi auduga ta dauka ta daura kan goshin nata tana share mata jinin wajen tace "what is your name yanmata?" shiru Rahima tayi batare databata amsaba tai banza da ita hakan yasa Dr din ta kalli fuskarta tacigaba da aikinta tace "young girls kaman ke always think shaye shaye is a gateway to having fun, inspiration, zero worries da sauran, aganinku shaye shaye wayewa ne irin kema kin isan

na, but my dear is a lie bahaka abin yakeba, yes nasan shaye shaye nasa ka manta da matsalolinka, ka manta da bakin ciki da duk wata damuwa data addabi zuciyarka, kaji kaman kai kadai Allah ya hallita a duniyan nan, kaji yes a yanzu u can stand up to anybody kodakam babanka ne, inkayi you can stand up against anyone and anything in fact u can even stand against the world, shaye shaye nabaka wanan karfin da boldness din da jarumtar aganin ku but my dear is not true, duk ba hakabane, shaye shaye is mess with the heart and mess with your brain the IQ dinki, baya komi illa destroying dan Adam, tundaga na lafiyan shi harda sauran su and kill u wulakantaccen killing ma, but you know you still have time, u are young, you are too beautiful karki bata rayuwanki akan wanan shaye shayen da kikejin dadinshi nayan mintoci, see duk abinda dadinshi ba dawwamamme bane den babu amfani yi, dadin da last for few hours ko for a day dadi ne? Ki natsu kituba Allah zai yafemiki kisan me kikeyi kokya samu rabauta" tana maganan tana shafa gyaramata injury din goshin nata sanan ta shiga hada kayanta, ahankali Rahima tasa hannu ta share hawayen dasuka cika idanunta suka sake zubowa sharr, ganin Dr looks friendly yasa murya chan kasa tace "I want to use the restroom" dagokai Dr tayi ta kalleta jin tamata magana for the first time, murmushi ta sakin mata tace "stand up muje na kaiki" ahankali ta tashi tana dafa bangon wurin tanadan dingishi suka wuce itada Dr din, officer yace "kuma two minutes nabaki" da Dr suka tafi daidai sunkai wajen bayin wani yafito daga wani office ya kwalama kira yace "Dr you are needed here" da sauri ta kalli Rahima tace "shiga this is the rest room, zakiga ladies side inkin shiga" tai magana tana tafiya, bude kofan Rahima tayi ta shiga rest room din, dan passage ne awajen dakeda two pathways dama da haggu da akwai kofofi,  ko kadan bata lura da sign din ladies da gentlemen ba take nuna Wannene bayin maza dana mata ba tabude kofar dama ahankali tanadan dingishi ta shiga, maida kofar tayi tarufe tai ciki, saida tai dan tafiya sanan ta iso main falon bayin wasu jerin bayi guda shida ne sai wash hand basin da manya manyan mirror a bangon, da sauri takarasa tabude bayin farko ta shiga ta mayar ta rufe, bayin so clean babu datti kodaya kodan bayin maza ne saisa oho, but bayin mata dai always yacika datti, mayar da kofan tayi tarufe tasa sakata sanan ta daga riganta sama tasa hannu a aljihun bayan wandon ta taciro wayarta da tuntuni take wurin Allah yaso ta babu wanda ya kirata da asiri ta yatonu sun kwace dan duk an karbe wayan sauran, maida wayan silent tayi da sauri sanan taciro number Mummy tana goge kwallan datake yi tai dialing number har wayan ya katse ba'a daukaba, haka tasake kira shima ba'a daukaba fashewa tayi da kuka tayi mara kara tana taushe bakinta, ba karamin tashi hankalinta yayiba takira mummy sau 17 times bata dauka ba bakaramin tashi hankalinta yayi ba yanzu kwana zatayi a wurin nan, gashi an fara kiraye kirayen sallan magrib, share hawaye tasakeyi, ahankali tasa hannu ta sauke cover bayin, zama tai kan sitter ta rufe fuskarta da duka hannayenta tana kuka tajima ahaka sanan tai shiru ta share idanunta tana kallon wayan sanan ta shiga saka wasu nambobi tadanyi jimm tana kallon number kaman mai tunanin wani abu kafin ahankali tai dialing number tasa hannu ta share hawayen daya zubomata takara wayan a kunenta, har wayan tagama ringing ba'a dagaba hakan yasa tasake dialing number akaro nabiyu, wayan na gab da tsinkewa aka dauka batare da ance komiba, ajiyan zuciya ta sauke mai kara kafin cikin muryan ta dake rawa sosai tace "h......he.....hello" hannu tasa tasake share hawayen daya zubomata tareda jan majina irin na wanda yaci mugun kukan nan, ahankali cikin kuka tone  tace "In..i.....ina police station ankamani dazu, please come and get me Mama, am so scared, please come and get me kinji" tafashe dawani irin kuka mai tsuma zuciya, katse wayar akayi batare da ance komiba hakan

yasa ta kifa kanta abangon bayin tafashe da kuka sosai, tai kuka na kusan minti biyar sanan tadago kanta tasake dialing number, ringing daya wayar tayi akai picking call din kafin ma tai magana muryan wata mata tarigata tace "I told you time without numbers karki kara kirana in your life, I don't have anything to do with you, an kamaki a police station what is my business with that? Mahaifinki judge ne so call him up not me, banda alaka dake or anything yarinya, stop calling me Mama mamaki kin barota achan gidan ubanki, in danta ninema rot a police station din ko agefen yatsana stupid girl, mtsww" ta katse wayan tareda jamata dogon tsaki, wani irin kuka tafashe dashi she is feeling kaman ta shake kanta ta mutu why did she even call this woman? takai almost 10min tana kuka kafin tadago kanta ranta yay mugun baci, cikin fushi tasake dailing number matar ringing daya aka dauka kafin matar tai magana tarigata tace "you know what calling you was the biggest mistake danayi sama da mistake din dayasa aka kamani aka kawoni nanma, how can I think a wicked woman like you can help me? Your heart is so black and dark da baisan menene help ba in this life, I hate you nima, I hate you with every single heart beat dina, My Mummy is better than you sau miliyan she can't never ever stand and watch me in pain, she is the best Mummy in the world, best Mummy, the absolute best, and I love her, I love her with all my heart, I can ever rot here saidai in Mummy na bata duniya, inhar nakara sa wanan hannun nawa nakiraki ba sunana Rahima ba, trust me inda ace Allah na laifi dazan iya cewa laifin dayayi shine yabama a wicked woman like you ciki harta haihu you deserve to be a barren cus you don't have soul saidai Allah baya laifi, I hate u, I hate......." katse wayan da akayi dip yasa tazare wayan daga kunnenta ta wurgar da wayan a kasan bayin ta shiga rera kuka tana kiran Mummy, she is so sad, she is so so sad, how can she even think if calling this woman mema yakaita eh? Mema yakaita, buga kofan bayin datake ciki taji anyi.
"open the door"

💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favor you always 💔

✍️ M Shakur

1️⃣8️⃣

Muryan mace taji, azabure ta tashi tsaye ta shiga kalle kalle bayin tana neman inda zatabi ta gudu, dan karamin window dake wurin babub abinda zai mata dudda rashin kibanta bazata iya wucewa tawajen ba hakan yasa ta tsaya tana kallon kofan tana share hawaye batare data bude kofan ba, cikin tsawan matar tace "I said open the door Lady, da uban wa kike waya abayi haa, and maiya kawoki bangaren maza, open the door!" aka mugun daka mata tsawa da yasa ta matso kusada kofan tasa hannunta kan sakatan tabude, turo kofan officer tayi batai wata wataba ta dauke ta da mari tass! Rike kuncinta tayi tana dafa bango, tsugunnawa officer tayi tadau wayar data yar akasa tasa  hannunta agaban riganta tawani irin finciketa tajata tareda bude bayi suka fita, suka fito main waje daidai lokacin Sameer ya shigo wajen shida wani dake rike da byro da wani paper dayake nunamai.

Ganin yanda ake kallonta yasa ta hadiye kukan datake yi ta dage ta ture hannun officer data kama mata gaban riga tace "dalla malama kidena jana tunda ni ba akuya bace muguwa kawai" da hannu officer ta nuna kanta tace "ni kike cema muguwa?" hararanta tayi da idanunta dasukai jajir suka kumbura tsabagen kuka tace "eh ance muguwa azzaluma m....." tass! Officer ta dauke ta da mari saida Sameer dake duba list yadago kanshi ya kallesu, fashewa da kuka sosai Rahima tayi tana shafa inda ta mareta tace "ance muguwa azzaluma, uban mena miki zakiyi ta marina kina jana, what have I done, banza kawai wacce tai kwantai ba miji" wani dan gajeren murmushi Sameer yasaki da gefen baki, ya maida kanshi kan list din da aka bashi yana dubawa zagin ya mugun bashi dariya ne tayaya akai tagane tai kwantai batai aureba, ohhh this Indomie generation children are damn hilarious.

Cikin fushi matar ta waiga ta kalli all the staff dake aikinsu abinsu dan irin wanan fadanne tsakanin yan shaye shaye dasu sun saba gani is not a new thing, hannu tasa tadau kulkin dake kan desk din Kusada su tace "zanci ubanki ne yau" cikin tsiwa tana kuka tace "ubana yafi karfin kicishi wlh, a inda ubana zai ubanki bai isa ya tsayaba saidai yazo bara" bugamata kulkin officer tayi a kafada hakan yasa tafasa wani wawan ihu da saida kunen kowa ya amsa, sake dago kai Sameer yayi ya kallesu ganin haka yasa officer dake nunamishi list din yajuyo yace "officer!" batare data kalleshi ba tace "officer I caught this gurl tana waya abayi shine on top of that takemin rashin kunya tana zagina, tana....." juyowa officer tayi zatai magana chairman yabude kofar office dinshi yafito yana kokarin sanya glasses dinshi a ido yace "Laraba enough! Lieutenant come with me please, officer give him the list" bama Sameer list din officer yayi yakarba yataho yawuce ta gabansu batare dayama kallesu ba yay upstairs, bude office din chairman yayi ya shiga, zama yayi akan kujeran da chairman ke nunamai yabashi hannu gaisawa sukayi, cikin harshen hausa Chairman yace "welldone Sameer am proud of you wlh, kasan mesa nakira ka, acikin yaran nan akwai mutum daya da I really don't know what to do about, am a leader you know Sameer and I don't want to be bias during the course of my work, bansan mezanyi ba I had to call you, kanada hankali sosai duk girman mutum sometimes idan zakadau hukunci dolene ka nemi shawara koda wajen dan cikin kane" yadanyi shiru kafin yamikama Sameer din hannu yace "kawo list dinan kaga" mikamai list din Sameer yayi ya karba yace "sunan yaran nan ne dakuka kamo, wanan yarinyar da officer ke bugunta yanzun nan she is the daughter of Chief judge of the federal High Court na nan Abuja, Rahima Sambo

Rikadawa, da farko danaga sunan I was like maybe is just a random person dat happens tanada surname na judge din garin nan, saida na kira wani friend dina lawyer danasan yasan Chief Judge sosai and asked him about yaran Chief judge nawa yacemin four and call the names for me which wanan yarinyar dakake gani happens to be his last born, kana hango abinda nake hangowa Lieutenant?" ya tambayi Sameer daya natsu yana kallonshi gyadamai kai Sameer yace "a Chief Judge is someone that is very vulnerable, mutum ne da kusan idanun kowa na kanshi, aikinshi aikine dakesa kai makiya dayawa sanan kai masoya dayawa abin kanzama kaman 50-50, ko 60-80, cikin makiyan harda nakusa dashi wanda kawai neman abinda za'ai amfani dashine atunkudeshi wani ya gaje kujeran shi na Chief judge din babban birnin tarayya, inhar press zasu samu koda gutsuren information ne kan yarshi na shaye shayen illicit drugs abin can cost him alot to the extend da zai iya tarnishing image nashi and his reputation a society mu, bayan haka, yanadaga cikin mutane masu yankewa drug dealers hukunci yau ga yarinyar shi na drugs" dan ajiyan zuciya Sameer ya sauke ya gyara zama tareda ijiye hannayenshi akan table yace "me kakeso daga gareni Chairman?" ajiyan zuciya Chairman ya sauke yace "bakaga nasa akai yarinyar dinning ba, all the staff anan babu wanda yasan abinda nasani, I want to isolate the girl from the rest of the gang sainai contacting mahaifinta yazo dakanshi ya dauke ta kaita rehab yarage nashi, mun bashi itane yanzu dan kare shi dakuma aikinshi daga bakin Al umma amma in muka kara kama yarshi akaro nabiyu ni I will release d information nabar press suzo su gudanar musu da interview kafin atattarasu akaisu government rehabilitation centre koya kagani?" gyadamai kai Sameer yayi yace "sauran yaran fa?" cikin dan damuwa kadan Chairman yace "what do you think Lieutenant?" dan shiru yayi kaman mai tunani yace "they have to go for rehabilitation, rayuwan su zai taimaka, Nigeria muna so muyi eradicating shaye shaye idan aka samu yara kusan talatin suka dena shaye shaye cigaba da Nigeria ne sosai, yayinda idan ka barsu baka kaisu ba ka kaddara mutane talatin dinan zasuje su koyama wasu mutane talatin din shaye shayen ne, kaga rate of shaye shaye yasake increasing kenan" gyadamai kai Chairman yayi yana yaba fikran Sameer yace "hakane, za'a kaisu, bari na nemi mahaifin nata abokina yabani contact dinshi dazan iya samun shi" gyadamai kai Sameer yayi, dialing number Abba chairman yayi harta gama ringing ba'a dauka ba, hakan yasa yacigaba da kirashi har sau biyar ba'a dagaba, knocking kofar akayi hakan yasa ya ijiye wayan yabada izinin shigowa, wanan officer data daddaki Rahima ne ta shigo rike da wayan Rahima dake ringing tace "Sir wayan yarinyar chan ne her Mother has been calling, I want to ask for your permission idan na amsa na sanar da ita mun kama yarta kokuma na kashe wayan" hannu chairman ya mikamata alamun tabashi wayan hakan yasa ta mikamai ta juya tafita, sake daukan ruri wayan ta shiga yi ganin Best Mum akan screen yasa Chairman yay pikin tareda sawa a speaker kafin yay magana Mummy tariga shi. "Autana where are you, sorry dakika kira ina kitchen dasu Siddiqa, wai har yanzu baku gama birthday party bane da Chris I think I asked you to come back kafin 6 gashi yanzu ana kiran magrib......." dan gyaran murya Chairman yayi yace "this is Alhaji Muhammad Mustapha Abdullahi the Chairman of National Drug Law Enforcement Agency (NDLEA) in Nigeria, please madam is your husband there I will like to speak to him" sosai gaban Mummy yafadi hakan yasa tace "innalillahi Malam please ina y'ata take? Ina Rahima na? Ina Autana? Yarinyar dataje birthday maiya badaku da ita kuma?" yanda duk take maganan a hargitse yasa yace "calm down madam, I asked is your husband there I want to speak to him" arude tace "no, no, bayanan yay tafiya yace port Harcourt

this morning, please ina y'ata? Me takeyi awurin ku?" shiru Chairman yayi yana sauraron yanda Mummy tarude ahankali yace "I am sorry to announce this sad incident like this Madam, but your daughter Miss Rahima Sambo Rikadawa has been caught taking Illicit drugs, Codeine, Crack, Tramadol, Weed, and shisha, she has been detained here according to the constitutional law, after some inevitable steps da we must carried out akanta, we are going to hand her over to rehabilitation centre inda zatai spending period of 6 months, thank you Madam for your time and do have a wonderful night rest" ya katse wayan tareda kashe wayan gabaki dai ya ajiye kan table Tareda danjan tsaki yace "mahaifinta yay tafiya Yaya kenan? Kaga tashi muje muyi salla" tashi sukayi suka fito daga office din suka sauka kasa inda suka tarar su Chris duk nacin abinci anbasu abinci a takeaway faran shinkafa da stew da dafaffen kwai, duk sunyi zuru zuru sunaci kaman ance in basuci ba za'a kashe sune.

Magrib sukayi suka fito daga masallaci suka shigo cikin premises dinsuna dan tattaunawa, reception suka shiga wata mata suka hango sanye dawani bakin dogon riga dayaji stones tayafa wani mayafi milk color na manyan mata akai tarike wani handbag na LV tana magana da receptionist din wurin tana fada tace "ina kuka kaimin y'ata where is Rahima? Kubani y'ata natafi da ita shairi ake mata Rahima batashan komi saidai in wanchan yaron Chris shine ya koyamata taga yanasha ta dandana dan dama shiyay inviting nata to birthday party shi" cikin masifa Chris yace "No dey lie Madam, your daughter sabi everything so tey she dey carry for bag go school, no dey lie for my head ha'a see me see gbese o" cikin fushi Mummy ta juya zatai magana taga wani magidancin mutum tareda wani cikakken dogon bakin yaro dake sanye da jacket baki dabai ja zip dinba, rigan dayasaka mai ruwan toka ya bayana da kirjinshi hartana hango kwantaccen gashin kirjinshi baki sidik, dan girgiza kanta tayi ta saita idanunta kan Chairman kafin ta kalli wasu manyan hotunan frame dake jikin bangon reception din na president, da vice president saikuma hoton shi da aka rubuta chairman NDLEA, cikeda masifa tace "good ka iso Chairman, I guess you are the one I spoke to a while ago, ina y'ata take? Kubani y'ata natafi gida, shairi kuke mata Rahima babu abinda tasani, she is my last born, yaushe na haifeta duka duka da zaku kamomini yarinya daga taje birthday coursemate dinta kucemin shaye shaye take? How on earth is this possible?" anatse Chairman yace "Madam until your daughter's father is back and come here dakanshi I'm not releasing Rahima nor giving her to you" yana maganan yay hanyar office dinshi binshi Mummy tazo zatayi security suka tareta hakan yasa ta tsaya daga wurin, ganin bala'inta bazai yi komiba burinta shine tasamu su saki Rahima su koma gida asirinsu arufe batare da Abban su yasani ba amma taga ina wayan nan basuda mutunci hakan yasa ta shiga rokon security su barta taje taga Chairman sukaki.

Shiga office din sukayi daidai wayar chairman yahau ruri karasawa table din yayi yadau wayan ganin Mahaifin Rahima ne yasa yay picking yasa a kunne ya nemi waje ya zauna yace "good evening to you Sir, this is Alhaji Muhammad Mustapha Abdullahi Chairman din NDLEA, I've been calling you na sanar dakai wani muhimmin abu, mun kama yarka awani gida nan hanyar Kaduna kano express road ita da wasu yara maza da mata su talatin da daya da sunan birthday party tana shaye shayen miyagun kwayoyi da gwamnati tabada umarni duk randa muka gani yanayi mu kamashi sanan mu aika dashi rehabilitation centre, ganowa damukayi Rahima yarka ce mukuma dan matsayin ka akasar nan munkuma san yanayin matsaloli da fitintinu dazaka fuskanta in duniya tasan me ake ciki yasa mukace bari mu maka alfarman kiranka mu sanar dakai shima badan komi ba saidan labari dakuma yanda ake yabata akan aiki bisa gaskiya dakake yi ne" shiru Abba yayi na kusan minti takwas tunani yake Rahima shaye shaye, party da maza ahanyar wajen gari, shaye shaye, innalillahi wa innailaihi raji'un, Chairman ne jin shiru yasa yace "kana jina" ahankali cikin murya datai rauni sosai Abba yace "innalillahi wa innailaihi raji'un, innalillahi wa innailaihi raji'un, innalillahi wa innailaihi raji'un" saida yafada sau uku yasake yin shiru yama rasa maizaice, Murya chan kasa data nuna karara alamun bacin rai da tsantsan damuwa yace "Chairman banda abinda zan cemaka sai Allah nasaka da alkhairi, wlh bazan maka karyaba wutan kaina ta dauke dib I don't know wat to think, alfarma daya zakamin kawai yanzu zan kira mahaifiyar ta tazo ta dauke ta sutafi gida, first flight zan biyo nadawo garin nan gobe dasafe zanzo har office dinka nasameka zamuyi magana da kyau, nakumayi alkawari binciken case dinan da kyau nagode" ahankali Chairman yace "mahaifiyar yarinyar is already here badai mubata yarinyar bane daman munce dole sai munyi magana dakaine, yanzu kuma tunda munyi zamu sa abata ita sutafi gida" ajiyan zuciya Abba yasauke yama kasa magana hakan yasa Chairman ya katse kiran yana girgiza kai yace "rayuwa kenan saikaga a good man ya haifi boka, jarabawan Allah kanzo tako ina, please Lieutenant help me tell them sukaima matar yarinyar nan sutafi gida" tashi Sameer yayi yafita daga dakin ganin babu kowa a upstairs din yasa yay dining din dayake anan sama dama dining din yake yasaba zuwa NDLEA din so ba bakonshi bane babu inda baya  shiga saidai in baisoba, bude kofan dining dinyayi tana zaune kan kujera ta kifa kanta kan table tana kuka ga takeaway din rice da stew dinta agefe ko kallonshi batayi ba, hannayenshi yazuba a aljihun wandonshi yay wani irin tsayuwa irin na sojojin nan yace "Ke!" da kakkausar muryan shi da sauri ta dago kanta gabanta na faduwa sabida yanda ya kirata, dauke kai tayi daga kallonshi ganin wanan mugun bakin sojan nanne daya mata wankan ruwa dazu. "zoki fita ur Mum is waiting at the reception" dawani irin mugun sauri ta juyo tareda ware jajayen kumburarrun idanunta tace "Mummy na kace?" shiru yayi bai amsata ba sai zubamata manyan idanunshi masusa mutane shakkan shi dayayi yana kallonta, dawani irin sauri ta tashi gabanta nafaduwa ta taho tana dingishi tabi ta gefenshi tafita da sauri tai hanyar stairs, ahankali yajuya yafito shima ya tsaya a daidai bakin benen har lokacin hannayenshi na cikin aljihun wandonshi yana kallon yanda take tafiya tana dingishi da sauri tana sauka, saida tagama sauka daga benen sanan tafashe da kuka sosai tana yarfe hannu kafin ta kwalama Mummy data juyama stairs din baya tana waya kira. "Mummy!!!" da sauri Mummy dake waya  tajuyo ganin Rahima ga bandeji a goshi tabi tai daka daka kaman ba yarinyar data bar gida fess fess ba yasa ta zare wayan daga kunnenta tana kallonta, dawani irin gudu Rahima ta taho tana dingishi takarasa tawani fada jikin Mummy tareda fashewa da kuka sosai mai tsuma zuciya, bayanta Mummy ta shiga shafawa tace "ya isa, ya isa, am here now

stop crying" dagota tayi tasa hannu tana sharemata hawaye tareda shashafa goshinta inda taga bandeji tace "maiya sameki anan maisa kike dingishi" cikin kuka tanuna Chris ashagwabe tace "wanchan matsiyacin ne Mummy mai kama da jaririn kunkuru shine ya fesamin goshi" wani mugun kallo Mummy tamai batason tai magana dan tasan yariga yasan few things gameda Rahima batason ya tona musu asiri hakan Yasa tace "barshi yama kanshi, let's go" security ne suka tare musu kofa bazasu barsu su wuce ba, Sameer dake gaban stairs a sama yana kallon komine cikin husky voice dinshi yace "let them pass" da sauri Mummy ta dagokai tareda juyowa hada ido sukayi da Sameer wani wawan faduwa gabanta yayi, chak ta tsaya tana kallonshi harsaida Rahima ta kalleta cikin muryan kuka tace "Mummy mutafi" ajiyan zuciya ta sauke takalleta tace "okay Auta muje" fita sukayi daga wurin security zasu maida kofan su rufe takara juyowa ta kalli Sameer daya fara tafiyan shi nan dai dai yay office din Chairman.
💫 *_BIN ABINDA ZUCIYA KESO_*💫

_CHASING THE HEART CRAVINGS_
Doesn't favor you always 💔

✍️ M Shakur

1️⃣9️⃣

Mota suka shiga Mummy taja motar suka tafi, saida suka shiga titi Mummy tace "what kind of matsala kika sani Rahima yanzu? Yanzu wani irin karya zan shiryama baban ki dazai yarda eh? Mezan cemai, kai! Innalillahi wa innailaihi raji'un, wanan Chris anyi dibabben yaro mai bakin jini da badluck mtsww" taja tsaki tana gudu ahanya, Rahima ba tace mata komiba gabanta faduwa kawai yake babu abinda take tsoro aduniya yanzu haka kaman haduwanta da Abban ta ahaka suka kai gida, su Siddiqa duk suna daki, dakin Mummy suka tafi direct wanka Mummy tasa tayi tabata abinci, kasaci tayi tace "Mummy bazan iya ciba, in Abba yadawo gobe kasheni zaiyi ko Mummy?" zama Mummy gefenta kanta takama ta daura akan kirjinta ta rungume ta tace "Hey am ur Mum ko, so kibar komi a hannuna, now eat ko kadan ne saiki sha paracetamol dinan karkiyi zazzabi kije ki kwanta kinji" gyadama Mummy kai tayi tasa chokali cikin abincin zata kai baki ta yatsine fuska tadago kanta ta kalli mummy, murmushi Mummy tayi tace "ina zuwa" tashi tayi tai wurin safe ta bude kara daya na wiwi ta dauko tazo ta juyemata a abincin juyawa tayi ta shiga ci da sauri dan yunwa takeji rabon ta da abinci tun rana, tana gamaci Mummy tabata paracetamol tasha ta kwanta ba'a wani dau lokacin ba bacci yay awon gaba da ita, tsayawa

Mummy tayi tana kallonta barinma goshinta dake sanye da bandeji har lokacin da kafadarta dayadan kumbura sabida kulkin da matarnan tabuga mata sai wrist din kafarta, wani irin murmushi tayi ta tashi daga inda take tadau kulan tajuya tafita daga dakin.

Sai wuraren 10 yakoma gida sabida tsareshi Chairman yayi sai hira yakemai, shidai chairman arayuwanshi starting from rana na farko daya fara ganin Sameer yake bala'in sonshi, gabaki daya yama maida Sameer din wani abokinshi dudda ya girmeshi amma yana son yaron, jan Sameer din yayi har zuwa gidan shi sukai dinner mai rai da lafiya sanan wuraren 10 Sameer yamai sallama yarakoshi waje saida ya shiga motarshi yafita daga gidan sanan yakoma cikin gida yana murmushi.

Wuraren 10:30 ya isa gidansu Gate aka budemai yay Parking yafito, flat dinshi yawuce direct dan yasan Ummi tariga ta kwanta, sabida hawan jini dakuma matsalan kafanta yasa Dr yace tadinga kwanciya da wuri, yasan ta kwanta saisa bayason yaje yatadata, part dinshi yawuce ya shiga ya maida kofan ya rufe bathroom ya shiga yayi wanka yafito daure da dan towel a waist sanan yadawo falo agogo ya kalla so yake yakira Mu'az he has been busy da tubda yadawo daga zaria baisamu ya kirashi ba, sanin yay bacci yanzu yaja ya kunna laptop dinshi ya shiga yin some work da yakamata ace yayi, almost 1hr yabata sanan ya kashe ya ijiye agefe yay addu'an bacci ya kwanta.

Aka'ida dama ana kiran sallan asuba yake tashi, tashi yayi yashiga bayi brush yayi yay wanka tareda dauro alwala yafito jallabiya yasaka ya feshe kanshi da turare yafito, mai gadinsu yatada sanan yawuce masallaci.

Wuraren 6 na safe ya shigo gidan flat dinshi yawuce ya shirya cikin wasu sport wears, bubu short ne daya tsayamai iya gwuiwa sai wani riga mai kama da singlet da wani karamin towel a wuya na goge zufa ya saka sport sneakers dinshi na Nike yafita gudu haka daily routine dinshi yake kullum ka'idane saiya motsa jiki da safe na 1hr, da yamma inya dawo daga aiki dawuri saiya shiga gym dinshi yay work out har zuwa gab da magrib sanan yay wanka yatafi masallaci.

Around 8 na safe ya shigo gidan, shashin shi yawuce yay wanka ya shirya cikin uniform tsaf sai uban kamshi yake yafito yay flat din Ummi, tana zaune kan dogon kujera sanye da dogon riga tana lazimi, tana ganinshi ta zuba mai harara hakan yasa yay dan murmushi yakarasa inda take, kusada ita yazauna yace "good morning Ummi" addu'a ta shafa sanan ta kalleshi tace "Sameer dama ido kanga ido" kaman zaiyi kuka yace "Ummi am sorry nowww please kidena

magana haka" dan tabe baki Ummi tayi tace "toya kakeso Sameer kanunamin kafi karfina" da sauri yace "Ummi dan Allah kiyakuri please forgive me, I've been busy jiyan nan koda nadawo was late saisa ba shigo ba banso natade ke, am sorry kinji Mamana" yanda yay magana cikin kwantar da murya danko kadan baiso yaga Ummi na fushi dashi yasa tace "to shikenan yawuce, tashi muje kaci abinci".

Tashi yayi sukai dining, kunun gyada Ummi ta zubamai da kosai da aka soya sanan tawuce dakinta, faracin abincin yayi dan he loves all this natural local food, he is not a fan of all this abincin yan gayun, bai wani jima da faraci ba Ummi tafito dawani 5liter jarka dayake cike da ruwan rubutu akan dinning table ta ijiye tadau cup ta bude ta tittila ruwan ta cika ta ijiye a gefe sanan ta rufe jarkan tace "maganin da Baffan ka yakawoma ne, ruwan rubutu ne akama na ayoyin Allah koma menene ajikinka dake hanaka aure zai kone ne da izinin Allah, ungo karba ka shanye" tamikamai cup din, dan murmushi yayi dan baiso yasami matsala this early morning hakan yasan ahankali yamika hannunshi ya karba yay bismillah yakai bakinshi ya shanye yabata cikeda murna tace "yauwa ko kaifa, Allah yamaka albarka soja na, Allah kuma yahadaka da matarka kwanan nan" baice mata komiba yacigaba dacin abinci dan bai wasa da cikinshi yanada ci sosai dama ance dogo nada dogon ciki, sanan duk soja nada ci , saida yagama ci tass sanan yatashi tareda goge bakinshi da tissue yace "thank you Ummi na koshi, natafi" kanshi ta shafa tace "adawo lpy, Allah yabada sa'a Allah ya tsaremun ku duka" ahankali yace "Ameen" sanan yawuce yafita saida ya tsaya yabiya mai gadinsu salary shi dan on 25th of every month yake biyansu sai murna Gate man yake yanamai godiya sanan yawuce ya shiga mota yatada yatafi office.

Karfe sha biyu da minti ashirin jirgin su Abba ya sauka a Airport din Abuja, yariga yafada driver yakawo mai mota, key motar kawai ya karba yabama direba kudi yahau taxi yakoma gida shikuma ya shiga mota yatafi kallo daya zakamai kagane yanada damuwa sosai, a parking space din headquarter NDLEA yay parking yafito, ya shiga ciki Chairman yariga ya sanar dasu zuwanshi hakan yasa cikin girmamawa sukamai iso har office din Chairman shiga ciki yayi cikeda girmamawa Chairman yatashi kan kujeran shi tareda bashi hannu yace "barka da zuwa Alhaji" karban hannunshi Abba yayi cikeda murmushi yace "barkan mu dai ya aiki yakuma fama da jama'a" "Alhamdulillah please sit" Chairman yanunamai kujera hakan yasa ya zauna ahankali tareda sauke ajiyan zuciya yace "bakomi yakawo ni nanba nazo namaka godiyan karamcin dakamin ne nagode Allah ya rufa naka kaima haka" girgixa kai Chairman yace "wlh is all thanks to Lieutenant Sameer, konima jiya kaina ya kwance he was the one that advised me

yacigaba da tafiya saida yaga wani babban pharmacy sanan yay parking ya shiga yasa yo duka magunguna ciki harda na wanda zata shafa a inda kuraje ya feso mata da kuma reddish din allergies din sanan yafito ya shiga wani super market another set od cloth yasaima kanshi da takalmi itama yasai mata takalmi sanan yawuce yakoma mota ya ijiye komi sanan ya shiga wani masallaci that is at the road side yay sallan la'asar yafito ya shiga mota yaja awani eatry ya tsaya yaci abinci sanan yaja mota yakoma hotel din, har lokacin tana bacci ajiye komi yayi yadau kayayyakin sawa su yasa a wardrobe din hotel din sanan ya zauna ya cicciro magungunan daya siyo mata yana karanta leaflet dinsu, maganin maleria ne dakuma na allergies din sai multuviate dazai bata apatite yakuma sa taci abinci, aijiyewa yayi yatashi yafita. Duk wacce takaranta min book dinan bata biyaba ban yafeba.
How to subscribe
Pay 300 to 3107021073 aisha Muhammad first bank saiki turo evidence of payment to my watsapp number 070121814621
49&50

Bayan sallan magrib suka shigo Hotel din tareda Dr din sunadan taba hira, knocking Sameer yayi tana zaune kan gado rike da rice din dazu data kasaci mugun yunwa takeji but dukta yanda taso ta chusa abincin acikin tane takasa sai kallonshi take akan kafafunta knocking da akayi yasa ta dago kanta batare datace komiba dan batada karfin magana bata dade da tashi daga baccin bama, bude kofan Sameer yay ahankali suka hada ido ahankali ta saukar da kanta kasa duk in suka hada ido sai gabanta yafadi juyawa yayi ya kalli Dr yace "come in" shigowa Dr yayi yana kallon Rahima yace "iyye patient ke kadai wanan delicacy din ba tayi?" dan murmushi tayi batare data dago kantaba yakaraso gaban gadon yace "to kishi abincin mana" girgixa mai kai tayi tasa hannu ta share hawayen daya zubo mata ahankali tace "nakasa ci" cikeda damuwa Dr yace "ahh sorry bakida apatite ne, don't worry tunda yanzu kin tashi akwai magun gunan dazaki sha zaki sami apatite nan da zuwa gobe zaki warke ok, mezakici yanzu?" murya chan kasa kaman wata marainiya tace "sliced fruits" dan juyowa Dr yayi ya kalli Sameer dayay kaman baya jinsu yace "call the kitchen officer akawo mata fruits, she can't take those drugs on empty belly" landline Sameer yadauka ya shiga kiran su shikuma Dr yajuyo ya kalleta yace "ban hannunki ruwan yakare nacire miki" mikamai hannun tayi ahankali yacire mata sanan ya shiga dubata temperature ta yasauka sosai ba kaman dazu ba, knocking akayi Sameer yabada izinin shigowa fruits din aka kawo mata acikin wani bowl da aka daura akan tray aka rufe takawo har gaban Sameer da hannu yanuna mata Rahima takaimata tareda mata sannu da jiki ganin batada lpy sanan tajuya tafita Dr yace "farasha" farasha tayi ahankali shikuma Dr yajuya yaje wurin Sameer ya karbi magungunan sanan ya ballo wanda zatasha yadau bottle water yace "gashi sha" karba tayi gabanta na faduwa watsawa tayi abaki sanan tadau ruwa tasha tana tabe fuska Dr yace "good gurl, shanye fruits din to" cigaba da sha tayi bata wani bata lokaci ba ta shanye tass, Dr ya karbe plate din yadaura kan tray sanan yadau balm din tube din da Sameer yasayo a pharmacy yace "kinga wanan maganin kije kiyi wanka sanan ki shafe duka jikin ki dashi duk wanan kujeren da kaikayi da tashi da tsigan jikin ki keyi zai dena saikizo kiyi bacci, in

sha Allah nan da gobe da safe kin warke tatas saidai cigaba da shan maganin harsai kin shanye dan ba'a wasa da maleria dose", gyadamai kai tayi yajuya yahada kayan shi ya kalli Sameer yace "to officer saikuma idan nazo dasafe inhar babu wani matsala da safen shikenan nagama da ita saidai kuma tacigaba dashan drugs dinta" tashi Sameer yayi suka fita daga dakin tare.

Tadade zaune awurin tana sauke ajiyan zuciya, sosai taji dadin jikinta dan yan ciwuwwukan datakeji sun ragu, sanan kurjewan datayi sun dena mata zafi kaman an zare zafin, yanzu burinta kawai ta ganta a jikin Mummy ta, tashi ahankali tayi dan fitsari takeji ta rike maganin da Dr yabata ta shiga bayi, brush tayi sanan tasake wanka da ruwan zafi kaman wata mai jego sanan ta goge jikinta duka da towel ta bude balm din ta shiga shafawa, tass ta shafe ko ina na jikinta dashi sanan tadau rigan data cire tasaka tafito daga bayin ta zauna kan gado tana kallon wayan Sameer daya bari kan kujera kaman taje ta dauka takira Mummy but tsoro take yakamata ahaka har gyangyadi yadan soma dibanta, bude kofan da akayi yasa tadan firgita tabude ido hada ido sukayi da Sameer daya shigo, maida kofan yayi yarufe sanan yajuyo babu ko digin wasa kan fuskarshi yace "kinyi salla?" yanda ya tsareta da idanu yasa ta girgiza mai kai ahankali batare datai magana ba yace "tashi kidauro alwala" ahankali ta yaye bargon datadan rufa dashi ta mike tsaye hartakai bakin kofan bathroom din saikuma ta tsaya ta juyo ta kallai hada ido sukayi da sauri ta saukar da kanta tana wasa da yatsunta cikin siriruwan muryanta tace "unnnn ai banda hijabi" batare daya kalleta ba yace "akwai hijab, jeki dauro alwala" bude bathroom din tayi ranta ko kadan ba dadi ta dauro alwalan sanan tafito taga harya shimfida mata dadduman daya dauko daga cikin motanshi ya fuskanci gabas shikuma yana zaune kan kujera daga zaune yanuna mata wardrobe yace "there's hijab inside" ahankali take tafiya kaman wacce kwai yafashe mawa aciki ta wuce shi tabude wardrobe din taga hijab ko sabo fil maroon, dauka tayi taciro daga ledan tazura yay mata kyau sosai gashi har kasa yakai mata yanaso yamata over yawa ma wani abu tahadiye sanan ta maida wardrobe din tarufe tajuyo tazo ta gabanshi zatahau kan dadduma remote yadauka ya kashe TV duka dake kara dan inda TV ke kallo ne gabas baison TV yay distracting nata, ahankali tahau kan dadduman, ahankali yace "turn around" dan juyowa tayi duktai zuru zuru ta kallai yace "daga sallan zuhur zaki fara, ahh kinyi subhi?" ya tambayeta without an atom of joke a magananshi, girgiza mai kai tayi hakan yasa yace "okay dana subhi zaki fara, kiyi zuhur, asir, magrib da isha'i" wasu hawayen bakinciki datake kokarin dannewa ne yazubo da sauri ta share sanan ta juya takabbarta tai subhi sanan ta tashi tai azahar da kyar kaman yasata aikin duniya gabaki daya takeji, sallamewa tayi tajuyo ta kallai hada ido sukayi dan yanabin yanda take sallan ne daki daki sallan ma akwai kuskure ciki sosai, hawayen daya cika idanunta ne ta share da hijabin sanan ta janye hijabin daga kan fuskarta ta kallai cikin irin muryan wanda ya cika yay fam gab take da fashewa dinan tace "nai sallan asuba da azahar dan Allah inbar sauran gobe sainayi? Kaga banda lpy" without any sign of remorse ko alamun yaji tausayinta yace "stand up kicigaba" fashewa tayi da kuka kaman dama jira take ta tashi tsaye ta kabbarta tana salla kuka, haka tai sallolin har isha'i kuka take tana sallame isha'i zata cire hijabi yace "remaining shafa'i da wuturi" jitayi dama wajen Wugugaga yabarta dayafi mata da uban sallolin nan dayake sata haka tai shafa'i da wuturi sanan ta sallame ta tashi tacire hijabin tai wurin wardrobe din tana goge kwalla sanin zai iya

magana yasa ta linke hijabin tasa acikin wardrobe din tarufe tana share hawaye tazo tahau gadon takifa kanta kan gadon tana kuka ahankali, yana jinta bai kulata ba takai almost 1hr kuka take sanan yajita shiru bacci yay awon gaba da ita.

Wuraren shadaya yatashi bathroom ya shiga wanka yayi ya chanza kayan jikinshi zuwa wani pyjamas daya sayo yay brush shima dan baya iya bacci batare dayay brush ba sanan yafito yana kallon yanda take bacci, gashin kanta ba dan kwali sai kyalli yake dudda ba gyara, yariga yay shafa'i da wuturi a masallaci hakan yasa ya kwanta kan kujera inda ace yanatare da system dinshi dayay wasu ayyuyyuka da yawa amma babu, kujeran yamai kadan tsawo hakan yasa ya saukar da kafafun shi kasa dan yatsine fuska yayi yaja pillow case din kujeran ya wuwwurga akasa sanan ya sauko kasan ahankali ya kwanta tareda yin addu'an bacci ba'a wani dau lokaci ba bacci yay awon gaba dashi ance jiki da jini dole akwai gajiya.

"ki kasa yayanki yamin duka, yajimin ciwo ko kinga wayan nan burma hancin da kadan garun" ta kalli burma hancin da kadangarun da sunfi guda dariya biyu chakude cikin wani farin botikin tallan bons yace "saina juye mikisu acikin ki su burma cikin ki su cinye miki kayan ciki ki mutu kaman yanda nima namutu" yana maganan yana daga riganta ya zazzage burma hancin da kadangarun kan cikinta da dukansu suka hau gudu kan jikinta suna neman wurin buya, wani uban ihu Rahima tayi tai jumping ta dirko daga kan gado tana tattaba cikinta tana juye juye bama ta gani ko kadan dan dakin duhu tace "wayyo Allah na cikina Wadugaga, wayyo Mummy" tama rasa inda zatasa kanta bamatasan inda hankalinta yakeba, cikin duhu sosai taga kaman Wadugaga take gani yana binta fashewa da kuka tayi wani mugun tsoro takeji ta kwasa da gudu bugewa tai da kujera tafadi akasa tacigaba dajan duwawu tana komawa baya tace "dan Allah kayakuri, karka samin lizard banso, please please wayyo Mummy na" jinta a jikin kofa yasa ta shiga tattaba kofan tana kallon mutum dake zuwa cikin idanuwan baccin ta, bude kofan tayi hasken corridor dakinsu dakenan akwai wuta ya hasko hakan yasa ta rarrafa da gudu zata fita tana kuka sosai, riketa taji anyi chak, juyowa tayi suka hada ido da Sameer dataga yakoma mata Wadugaga baki ta bude zata kurma ihu da sauri Sameer yadaura hannunshi dakeda lema lema dan ya shiga bayi dauro alwala ne ya chanza kaya daga pyjamas zuwa normal kayanshi dan sallan dare yake so yayi yadaura hanunshi akan bakinta tareda dagata yace "Rahima, ke" fashewa da kuka tai sosai tanaaon ta fizge hannunta ta gudu amma takasa, jawota yay cikin daki ya maida kofan yarufe tareda saka key yakawo ta cikin dakin da karfi da yaji hannunshi nakan bakinta har lokacin ya zaunar da ita kan gado tareda dan jijjigata yace "Rahima is me, are you okay?" ware manyan idanunta tayi ta kallai cikin duhun tana dan kyafta ido, ahankali ya janye hannunshi daga kan bakinta yace "menene?" fashewa da kuka tayi sosai tana kallon ko ina adakin tace "wanan mutumin ne zai kasheni wai, shine yazuba min lizard dayawa acikina" tai maganan tana kallon saman kan cikinta jin cikinta yay motsi yasa tace "wayyo Allah na Yaya Sameer zan mutu suna ciki kasheni zasuyi wlh banso na mutu kaji" tashi tayi dukta rude tana

kokarin cire rigan da sauri yakamata tareda zaunar da ita yadan tausasa murya ganin duk cikin bacci take abin nan yace "look at me Rahima" kallonshi tayi atsorace hawaye nabin idanunta yace "it was just a dream babu wanda yazo nan" dakin tasake kallo dan dakwai dan haske dan yabar kofan bayi kadan abude sanan ta kalli fuskanshi ahankali tace "a dream?" gyadamata kai yayi yace "yes just a dream, now sleep okay and relax, kwanta" kwantawa tayi saikuma ta tashi arude takama hannunshi tarike gam hannunshi data kama yabi da kallo takoma ta kwanta jikinta narawa tana cigaba da kuka zata rungume hannunshi a kirjinta da sauri ya karbe hannun yace "just sleep bari naje nai salla" yatashi daga kan gadon da gudu ta tashi itama tafashe mai da kuka juyowa yayi ya kalleta cikin danjin haushi yace "I said kije ki kwanta" dawowa kusadashi tayi da sauri kaman zata shige jikinshi dadan tsawonta da baigama kaiwa kirjinshi ba tace "akwai lizard on the bed they're everywhere, am scared take me to my Mummy please" shiru yayi yama rasa yanda zai mata ganin yay shiru yasa tafada jikinshi ta rungume shi tsam tsam tana kuka sosai tace "please take me to my Mummy am so scared" wani irin yarrr yaji ajikinshi da sauri yature ta yace "o....okay naji zan kai...ki in gari yawaye" kin barinshi tayi zata kara shigewa jikinshi yace "muje ki kwanta" kafadarta yakama sukai gado ya kwantar da ita kan gado yaja bargo ya lullubeta yace "sleep am right here okay" fashewa dawani irin kuka mai tsuma rai tayi tace "zai kasheni wlh please ka kwanta inba hakaba zaizo kaji kuma kasheni zaiyi" dan jim yayi yana kallonta saikuma ya zauna abakin gadon ahankali, dago kanta tayi da sauri ta daura kan cinyarshi kaman yar mage ta runtse idanunta gam cikin tsoro tareda kama hannunshi tarike duk dan karya gudu, zufa yaji yaketo mai jikinshi yahau rawa yanajin wani sensation dan jikin Rahima is way too soft kaman na yar jaririya, zirr zirr yakeji ta cikin jikinshi sosai dan daurewa yayi saikuma yatureta da sauri ya daka mata tsawa yace "ki kwanta, I said ki kwanta!" sake firgitata yayi ta tashi daga kan gado zata kara fadawa jikinshi kaman wacce ta zare tana kuka da sauri ya matsa, matsowa kusadashi tayi tana kuka ahankali tana gyangyadi tana hamma, dan juyowa yayi ya kalleta saiyamaji tabashi tausayi, ahankali yakama hannunta ya kwantar da ita yace "matsa chan" matsawa tayi sanan ya kwashe pillows din yasaka a tsakanin su sanan ya kwanta adayan gefen matsowa tayi da sauri zata cire fillon yamata mugun kallo yace "kika cire filon nan saina bar miki dakin koma menene yazo ya kasheki" kankame fito tayi ta daura hannunta kan filon tai lamo tana kallonshi tana hawaye tana sauke ajiyan zuciya, juyamata baya yayi da sauri cikeda takaicin all what children do is to give you headache, me abin tsoro a dream yanzu, jin tana sheshekan kuka yasa batare daya juyoba yace "Allah kika baremin baki saina bar miki dakin nan, so kika akoremu daga this hotel ko" yanda yaji tana nishi yasa yadan juyo tareda sassauta murya yace "am here just sleep kinji" gyadamai kai tayi batare datai magana ba tana kuka, sake juyamata baya yayi sukai shiru yanajin yanda take numfashi da sauri da sauri kaman wacce ake kwashewa ana miya, ahankali tasa hannunta tacire filon ta wurga bayanta duk yana jinta, matsowa tayi kusadashi sosai tasa hannunta tarike bayan riganshi gam gudun karya gudu sanan tasa fuskarta ata wuyanshi har goshinta nataba fatan wuyanshi sanan tasauke wani ajiyan zuciya mai karfi hankalinta ya kwanta jinta gab dashi sanan ta lumshe ido, duk Sameer najinta kaman zai kurma ihu yakeji har bacci ya shigeta sosai cikin bacci ta matsoshi sosai ta yanda har tudun boobs dinta na rubbing back dinshi, wani irin desire ne yataso mai da sauri ya lumshe ido, bare boobs dinta dayagani dazu dasafe ne dazu ya shiga gani da sauri ya girgiza kai kaman wani mai ciwon kai inda zakuga zufan da Sameer yake zaku zaci faskare yakeyi kokuma wani aikin wahala, wani mugun shock yakeji daya dade

baiji ba ga cikinshi dayaji yashiga murdamai kafafunshi na rawa yana having a very strong boner, dawani irin sauri yajuyo ya fuskance ta tareda mika hannunshi ya kunna bedside lamp dakin yadanyi dim haske ya kalleta kawad dakai yayi da sauri dan almost half of her boobs na waje dan yanda ta kwanta yasa rigan ya kwanta akasa, wani wawan strong erection yaji yana having, batare daya sake bata second look ba yatashi daga kan gadon da kyar ahankali yaja blanket yarufe ta cikinshi namai wani mahaukacin ciwo yadaura hannunshi kan belt din wandonshi yay hanyar bathroom, bude bathroom din yayi ya shiga ya maida kofan da sauri yarufe ya jingina da kofan yana zare belt din gabaki daya ya yar akasa, ya bude maballin wandon tareda jan zip din wandon kasa yanda boxer dinshi yadaga kaman ya boye beredi family size ciki, wani azababben kara yasaki kadan. "auuchhhh!!" yadade baiyi ciwon cikiba ko having erection haka yana mugun kula da kanshi dan ciwon cikinshi har suma yana sashi yayi kuma baya tareda maganin shi yana gida balle yasha, jan boxer dinshi yay kasa wani huge fat and long erected joystick ne ya bayyana, gaskiyan Mummy ne tace daga ganin Sameer akwai kafiyayyen manhood ga tsawo dan yanada tsayi kam, baki ne sosai abinku dashi kanshi Sameer din is black ga kaurin bala'i and huge, kan crowns din is very big kaman wani baban hula ga one yorky water din sha'awa nadan diddiga daga kai ta mike sambal kan har lankwashewa yake yana wani mimmikewa searching for food dan is starving, joystick din Sameer sune joystick din da ake cema _Destroyer the naughty mama dream_ jajir idanunshi sukayi kaman gauta da kyar ya iya daga hannu yasa sakata abayin gudun karta shigo dan yasan wats about to happen to him, yama rasa yazaima kanshi sai sauke ajiyan zuciya kawai yake yana zufa yana  taking deep breath manhood din namai ciwo maranshi namai ciwo harya soma raina kanshi, baiso yay ihu ko kara hakan yasa da kyar ya iya daga kafa brush dinshi ya dauka daga wajen ma'ajiyan brush yasa jikin brush din a bakinshi ya datse hakoranshi akai yana nishi manhood dinshi na springing jijiyoyin kanshi na fiffitiwa kaman wanda zai mutu karya brush din hakoran shi sukayi  tsabagen ciwon cikin dayakeji ya fuzar, wani mahaukacin murdawa da cikin yamai yasa yasaki wani kara da ikon Allah ne kawai zaisa Rahima bazataji ba yafadi akasan bayin asume batareda yasan inda kanshi yakeba.

Ahankali Rahima ke bude ido sabida knocking kofar dataji anayi, tass tabude ido tana kallon dakin ganin hasken rana ta qibdo yasa tagane ashe gari yawaye, tashi tayi ahankali ta zauna tana kallon ko ina na dakin dataga babu Sameer sai wayanshi dake kan throw pillows a kasan dakin, cigaba da knocking akayi hakan yasa ta tashi ahankali ta karasa wajen kofan tace "waye?" daga waje Dr yace "nine Dr".51 & 52

Bude kofan tayi jin bai budeba yasa ta murza key kofan yabudo ahankali tace "good morning" batare da Dr ya shigoba tace "morning patient, ina Soja? Inata kiranshi in cemai am coming very early bai daukaba" kallon dakin tayi tace "ga wayan chan bayanan" gyadamata kai Dr yayi yace "akwai any ciwon dakikeji?" girgixa mai kai tayi tace "shikenan, Allah kara sauki ki cigaba

da shan maganin ki kifadamai nazo zai kirani inya dawo" gyadamai kai tayi ta maida kofan ta rufe ta dawo ciki tana sake bin wayan nashi da kallo sanan takoma kan gado ta zauna bude kofan bayi taji anyi da sauri ta dago kanta Sameer ne yafito sanye da kaya ajikinshi da karamin towel a hannunshi yana share gashin kanshi cikeda mamaki tabishi da kallo dama yana nan, agaban wardrobe ya tsaya sanan ya juyo ya kalleta da sauri ta sauke kanta kasa gabanta na faduwa tace "ina kwana" batare daya amsa taba yace "go and shower kiyi alwala kizo ki salla" tashi tayi ahankali tabude bayin dataji yana kamshi Sameer din ta shiga koda tafito bata ganshi adakin ba babu kuma wayanshi sai Dadduma daya shimfida mata shiryawa tayi cikin wani black doguwan riga tai salla tana zaune room services sukazo suka gyara dakin tsaf suka mata yajiki sanan suka kawo mata breakfast kaman yanda Sameer yabasu izini dan fita yayi.

Around 4 Sameer yadawo Hotel din rike da dan wani box a hannunshi kaman na working tools, knocking yayi sanan yabude dakin nasu ya shiga tana zaune kan gado tana murmushi ita kadai da TV, carton take kallo ta sanya daga daga cikin dogayen rigunan daya sai mata daya mata bala'in kyau kanta babu dan kwali, daidai da ciwon kai bataji taji sauki sosai jin anbude kofa yasa ta dago kai da sauri ta sauke kan tuna abinda taitayi jiya ahankali tace "ina yini" bai amsata ba sai wani mahaukacin daure fuska dayayi yadawo sojanshi tsaf ya maida kofan yarufe tareda murda key yazaro key yajefa a aljihu ya shigo dakin ko takalmi bai cireba, karasawa gaban gadon yayi yasa hannu yadau remote din TV data ijiye a wajen ya kashe TV, ahankali tadago kanta ta kallai dan faduwa gabanta yayi ganin yanda fuskan shi yayi yau babu ko dingo rahama, gaban bayi yaje ya kulle yacire key yasa a aljihu tasake binshi da kallo sanan kujeran dakin ya jawo yay kwana dashi kujeran ya fuskanci gadon datake kai, da yatsa yanuna mata kan kujeran yace "sit here" wani irin faduwa gabanta yayi ahankali ta tashi ta zauna awurin da yanuna mata tsakiyan kujeran tana kallonshi kaman tasami tv, aljihu box din yayi kan gado sanan yabude kadan yajawo wani seletep yamayar ya rufe sanan ya juyo kanta da jajayen idanunshi ya kalleta da sauri ta tashi jikinta narawa tace "Yaya Sameer wlh nai salla fa, me zakamin eh?" cikin wani black voice yace "sit" komawa tayi ta zauna sanan ya tsaya akanta ya warware seletep din yazo ya manne bakinta bam dan baiso tamai ihu kafin yakoma kan gadon yabude box din da kyau, set din wasu miyagun wukake ne da bamata taba ganin irinsu ba sharpness din bakinsu datagani yasa tagane wukake, wata gajera yadauko yajuyo ya kalli Rahiman kafin ya zauna abakin gadon har gwuiwan su nataban juna yadau wani paper Hotel ya kyasta wukan ta yanka paper sanan yakawo wukan saitin fuskanta yunkurin magana ta shigayi ta mike tsaye yamata wani mugun kallo yace "sit" zama tayi yace "kinsan sunana ko Lieutenant Sameer Simran Sameer, wayan nan wukaken dakika gani legal knives dina ne duk wanda na yanke dasu ko na kashe kaman na kashe banza ne, zan iya kashe ki anan babu wanda yasani babu wanda kuma zai taba sani, bana wasa da yara Indomie generation irinku, u always say bakison kimutu yanzu, inhar you want to live to dole ki natsu and say the truth, dan rayuwanki yau depend on gaskiyan da kika fadi ko karya and try me and see" yay maganan babu wasa yana kallon idanunta datake zarowa tsabagen tsoro kaman zasu fadi akasa hawaye nabin idanunta, yace "one more thing, ko tari kikamin anan not just ihu I will shock you Rahima, zan

baki mamaki" yay maganan tareda tashi ya cisge seletep din bakinta ta runtse ido sabida azaba batare datai koda tari ba tana sauke ajiyan zuciya, sanan ya zauna yace "clean those tears" da sauri tasa hannu ta sharesu kirjinta dukan a shirin a shirin kawai suke tsabagen tsoro ita dama harga Allah batawani yadda da abokin Abban nan wanan sojan ba tasan mugune, gyara zama yayi yace "are you ready?" gyadamai kai tayi tana hadiye hawayen dake shirin zuba, yana kallonta right into the eyes irin kallon I dare you to say lies dinan yace "ranan da mukazo gidanku da magrib nida Abban ki, baki fitaba, after basketball Mummyku tace min duk bacci kukayi kece kadai suka bari adaki baki riga kin tashi ba, ya akayi a ina kika samo 3 bottles of codeine da weed dat u were smoking ranan?" wani irin racing heart dinta ya shiga yi zata fashe da kuka yace "this is the last time dazan fada miki karkimin kuka, cry kika idan ban fasa miki tear bags dake cikin idanunki ba" hadiye kukan tayi tai gum tana kallonshi kaman zata cinyeshi da ido yace "answer me!" gyadamai kai tayi da sauri tace "a....kagako..." takasa magana tsabagen yanda kirjinta ke bugawa bakinta kerawa sosai ya tsareta da wasu irin mayun idanu yace "am listening" tace "wlh ina tashi daga bacci na shiga bathroom nai brush na wanko fuska na nafito shi....ne" tai shiru yanda yamata wani kallo yasa tace "shine na gansu akan bedside drawer dina su uku da weed guda uku, wlh baruwana bani na ijiye ba na rantse da Allah" tai maganan bakinta na rawa tana shirin kuka amma yanda ya tsareta da ido da wukake yasa ta hadiye kukan, sosai yake kallonta yasha interrogating criminals so yanada knowledge inhar yama tambaya ka saki karya zai sani kana fadin gaskiya zai sani kuma yasan tambayan nan iyakan gaskiyan datasani tafadi mai hakan yasa yay shiru, puzzle questions zai mata dashi ne zai bama kanshi da kanshi final amsa din, yace "how did you escape from rehab?" rawa bakinta yafara da kyar ta danne kukan tace "ranan I was bathing in the morning all of us muna bayi shine one woman tafado bayin nakusan ihu shine tarufe min baki......" nan tabashi labarin har inda suka kwana da abinda suka bata duka tai maza ta share hawayen daya zubomata gyadakai yayi cikeda gamsuwa yace "who was that Chris your boyfriend me hadinki dashi?" fashewa tayi da kuka kallon daya mata yasa ta hadiye kukan da sauri tace "wlh wlh ba boyfriend dina bane, ajimu daya a vet, kagako ni banda ko kawa daya a school dinmu, I don't talk to anybody a class dinmu shine kullum kullum yayta kallona yanamin magana wlh bantaba cemai komiba, ranan damuka zo school zamu fara sauke ya Siddiqa a accounting department su Yaya Siddiqa da Luba da Zeena sunata xagina, shine direba wai sudena biyemin ni yarinya ce, shine fa naji haushi nace yakara cemin yarinya saina marai shine Yaya Siddiqa ta daddakeni ta fizgoni ta yardani akasan wajen" tafashe da kuka, mugun kallon daya mata yasa tahadiye kuka tace "Ya Siddiqa tacema direba yatafi yakaisu Ya Luba tunda rashin kunya nakemai nai trekking to department dina kumafa duk yafi nasu nisa chan karshen school dibfa muke, shine tai tafiyanta tabarni natashi ina kakkabe jikina saiga Chris ya tayani daukan jakana yace nazo muje da kyar na shiga damuka je har an shiga lecture shine saiyaga Codeine ajakana saiyace......." tabashi labarin tsaf harda yanda Mummy saida tamaga Chriss din tace su tafi, Sameer baice komiba harta gama yana sauraronta yace "Rehab Dr ki ya sanar dani you have been taking drugs 8yrs ago, jikin ki yabasu dat record" ya kalleta kaman yanda take kallonshi yace "your Dad told me baki dade da shiga 20yrs ba, bari namiki simple mass, subtract 8 daga 20" da sauri tace "12" gyadakai yayi yace "you've been into drugs tun at the age of 12, yaran 12yrs bama susan me drugs ba, basusan akwai wani abu shaye shaye aduniya ba, children of 12yrs ko balaga basuyi ba basu mallaki hankalin suba, bama Susan menene duniyan nan ta kunsa ba, listen Girl" ya

gyara zama yace "idan kika kawomin any gargada akan wanan tambayan zan baki mamaki, I need answer tell me ya akayi kika fara shaye shaye at the age of 12, ranan farko and everything" faduwa gabanta yakeyi bana wasaba Mummy tasha fadamata kar wanda yaji tsakanin su, koma menene karta sake ta kira sunanta mutane da society sun dauka shaye shaye is bad but is actually fun, da dadi su basu sani bane. "Rahima!" Sameer yadaka mata tsawa tareda kai wukan kasan wuyanta yasa tafara wani nishi kaman mai shirin mutuwa duka jikinta moving yake yawani zaro red eyes dinshi yace "tell me how did you start doing drugs, who the hell introduced you to drugs at 12yrs old, who! Yasaka mata wani mahaukacin tsawan da batasan lokacin datace "Mummy! Mummy na! Mummy nane!!" kallon kwayan idanunta Sameer yayi kafin yadan koma baya saikuma ya zauna yana kallonta bai bari yanuna mata anything ba, hawaye ta share da sauri saikuma tafashe da kuka tace "Ya Sameer dan Allah karka fadama Mummy, wlh tace duk randa nafadama wani daga ranan zata dena sona tunda ni ban rike sirrin ta amana ba please kaji, dan Allah wlh zan fadamaka amma karka fada kaji" wani mugun kallo yamata shiru tayi tace "kaga ko Ya Sameer duk duniyan nan wlh babu mai sona kaman Mummy tana sona dama dasu Ya Siddiqa data haifa, kaga su Ya Siddiqa kullum suyi ta dukana da ina kwana a dakinsu Mummy tacireni daga dakin tasa home decor tazo aka tsantsaramin dakina yafi nasu kyau, kuma kullum da daddare a dakinta nake kwana dan bana iya kwana ni kadai, kaga bayan Mama na ta karyani tabar gida nadinga ciwo zafi ko ina yakemin anata karyani ana mayarwa mummy in anamin dauri harsai Abba yakoreta dan kukanta harya kanfi nawa sabida yanda take tausayina mu dawo gida inta kuka bana iya bacci wata rana tazo da Abba yafita sallan magrib su Siddiqa basa daki ta zauna tareda rugumeni tana tofama hannun karyan addu'a tacemin zata bani wani abu dazaisa nadaina jin zafin hannun amma karan fadama kowa inaso na gyadamata kai tace kuma abin zai dinga sani farin ciki na manta da mamana muguwa my mum is wicked but she is here now, she is my Mum she loves me more than her banga bata taba dukana ba kuma bata tababa so ma manta da ita zatamin komi, tasa na kulle idona nabude baki ta naji dai wasu kwayoyi guda uku tasamin sanan ta zubamin wani ruwa mai daci nasha, ta kwantar dani ajikinta tanamin tatsubiya nai lamo ina jinta ahaka nai bacci sai washe gari natashi aiko hannuna babuma inda kemin ciwo I was so happy nadinga murna ina tsalle ina rawa itama ta tayani, dazaran naji zai fara zafi zanje dakinta nace tabani abun tacemin nabari da magrib kullum da magrib take Bani lokacin kuma saina rufe ido nadena rigima harnazo na girma, tacemin nai browsing uses of weed nayi, kagako Ya Sameer Mummy duk wani abu dazai amfaneni takemin bamatama yayanta, naga weed na bude brain hakama shisha dan akwai nikotin aciki tundaga ranan tace kullum zata dinga samin a abinci saisa in babu shi a abinci ban iyaci danna saba kuma ko nafi duka su Ya Siddiqa brain because of weed 9As nafito dashi a Waec jamb kuma naci 362, Mummy ko tsinke bata bari na daga anything dazaiban wahala bata bari nayi bana aiki nan shara ban wanki ban girki kuma insu Ya Siddiqa sunkai karana ta dakesu, su kadai keyin aikin suyi abinci su kawomin har kan gado, ran Saturday da Sunday kawai take sani nabisu islamiyya shima sai in Abba na nan sabida karya mata fada amma inhar bayana van zuwa sabida duka akeyi, su Ya Siddiqa kadai ke zuwa, in kanwar Mummy taje dubai ni kadai zatasa ama tsarba kaya dan nine autan ta, kaga yawan kayana yacika wardrobe dina some kayana ma a wardrobe dinta suke, takaini saloon kullum dani take fita, in Abba yadaken taita fushi, insu Ya Siddiqa suka daken takamatsu tace inzo in rama kaga bata bari aci zaluna, batason ta ganni cikin bakin ciki duk wani abu dazai

cireni a damuwa zata bani, Mummy na bala'in sona tacemin that my wicked Mother ta taba sata tai bari bayan ta haifi Luba wai mamana tasata tai barin cikinta na boy amma bata riketa da hakaba yasa taci zaluna ba kota lalatamun rayuwa ba saidai ma tasoni sama da yanda taso nata yaran, kuma bata taba bari Abba kosu Siddiqa sun gane ba da daddare take bani nasha nai bacci, kuma Abba shi yawanci a studyroom yake kwana yana aiki sai tsakar dare yake dawowa kuma wani zubin a sati baufi yay 3daya a gida ba sauran yay tafiya saisa duk basu saniba sai ranan shima nasan Mummy ta ijiyemin ne kawai dantaga bana cikin farin ciki to tazaci da daddare zansha shine nikuma na dauka nasha alokacin nai mistake" tai shiru tana kallonshi kaman yanda yake kallonta, jikinshi yay mugun sanyi jikinshi yay sanyi, all he sees a idanun Rahima is yarinta da mugun rashin wayau, akwai yaran 20 da hankalin su is intact but Rahima kam Mummy tai brainwashing yarinya da bama tasan different between right and wrong ba, tadawo da brain din Rahima a fool, ajiyan zuciya ya sauke ahankali yan abubuwan dayagani couple of times dayaje gidansu nadawo mai, maida wukan yayi cikin box din yarufe box din yana kallon Rahima dake kallonshi har lokacin gabanta na faduwa tace "ai ba zaka fadaba ko" gyadamata kai yayi yadau box din yatashi yafita daga dakin binshi tai da kallo saikuma tafashe da kuka takoma kan gado ta kwanta duk zuciyanta yaki natsuwa.

Tunda Sameer yahadu da Rahima yauce rana ta farko dayaji rayuwanta da ita kanta Rahiman ta mugun bashi tausayi, a mota ya zauna yana tunanin me zaiyi dudda dai bai basani ba for now abu daya dayasani shine zaman bazai kara bari tazauna da Mummy ba, and duk inda maman Rahima take aduniyan nan he will find her kiran magrib da aka fara yasa yafito yatafi masallaci, wuraren sha biyu ya shigo dakin yaga tadade daya in bacci bayan tasha fruits salad ta koshi.

Ranan bacci sosai tai da daddare bata tashi ba har sauda yatada ta da safe yace tai salla tai wanka zasu koma yau faduwa gabanta yayi shikuma yawuce ya sauka kasa dan zaiyi checking out and clear his bills, wuraren nine yadawo yaga tao wanka tana sanye da dayan doguwan rigan tai kyau dudda har yanzu da muguwa raman nan datayi hijabi yanuna mata yace "saka mutafi" dauka tayi tasaka tadau kayanta data hada a ledan suke suka fito sai kallon hotel din take tunda sukazo sai yau tasake fitowa sukai mota, gaba ta shiga shima haka hakanan saita tuna abinda tayi ranan wani kunya yakamata tada motan yayi sukadau hanya sai faduwa gabanta yake kaman akwai abinda zai faru da ita ahaka har bacci ya kwashe ta.

Saida sukai parking a hanya lokacin azahar yatada ta suka shiga wani masallaci kan hanya dudda na maza ne yasa ta koma chan baya tai salla shima yay nashi agaba sanan yasaya mata snacks suka koma mota bamata iyaci ba bacci yakara awon gaba da ita.
Horn dataji yasa tabude ido ganin suna kofar gidansu yasa ta gyara zama tana zaro ido gabanta nafaduwa Gate gateman yabude musu Sameer yaja motar ya shiga da ita ciki sai kallon motar Abba dayake a pake take sanan yay Parking yafito tareda kallonta, bude wa tayi tafito ahankali gabanta nafaduwa sosai sanan yafara tafiya tana biyeda shi, labewa tayi

abayanshi yay knocking kofar sitting room dinsu, Zeena ne tafito tana sanye da atampa da dan kwali bamata lura da Rahima dake labe bayan Sameer ba dayake yanada tsayi, cikeda girmamawa tace "ina yini ya Sameer, Abba na nan amma Mummy taje sunan wata kawarta a Suleja gobe zata dawo...." "wa kika cikada surutu haka Zeenah" cewan Abba dake zaune a falo, da sauri Zeenah ta matsa tace "Abba Ya Sameer ne yazo abokin ka" da sauri Abba ya kalli kofan ganin Sameer yasa wani sahihin murmushi ya bayyana a fuskanshi yace "Lieutenant, bismillah, son shigo" ahankali Sameer yadaga kafa ya shiga dajin da murmushi kan fuskan shi hakan yabama Abba dasu Siddiqa daman ganin Rahima dake tsaye bakin kofan takasa shigowa kanta akasa sai rawa kafafuwanta suke sabida muryan Abba dataji, wani irin mikewa Abba yayi tsaye idanunshi kan Rahima saikuma ya kalli Sameer yace "are you together with this girl?" gyadamai kai Sameer yayi yace "Abba ka zauna is a long story" cikin fushi Abba na danne zuciyarshi yace "wani irin long story Sameer?" ganin yanda Abba ya harzuka he is not even ready yazauna and listen to him yasa yace "Abba sarkin garin dakakai yarinyar nan tried to molest her, he tried rape her, and she called naje and rescued her" cikin wani irin fushi Abba yace "try to rape her?" gyadamai kai Sameer yayi, dan shiru Abba yayi saiyadan yi murmushi kaman wanda yazare, kafin cikin wani irin masifa yace "finally tasami mashinshini" saikuma yay shiru kafin ahankali yafara walking hdown zuwa bakin kofan dakin inda Rahima take tsaye, sauka yayi duk su Sameer na kallonshi sun zaci magana zai mata kawai gani sukayi ya dauketa da mahaukacin mari yace "dan uwaki yau dinan ba gobeba komi dare aurar dake zanyi badai shaye shaye kika saka agaba ba zakiga hukuncin shaye shaye ya fizgi hannunta da sauri Sameer yafito kafin yafito Abba harya kaita motan shi yabude baya yajefata ciki ya rufe Sameer yagani, hannu Abba yadagama Sameer da zaiyi magana yace "quit son" Siddiqa data iso wajen da sauri tace "Abba dan Allah kaya...." shiga motan yayi ko kallonta baiyi ba ya danna uban horn, gateman yabude mai yafita.

53.....

Dafe goshi cikin masifan fushi Sameer yayi ya shiga motarshi kafin gateman yarufe yafice yabi Abban dayaga motarshi yamai nisa danhar yahau kan titi, sosai Rahima ke kuka tace "Abba dan darajan iyayen ka karka maidani kauyen nan, Abba dan Allah, wayyo Mummy na" ko sauraronta Abba baiyiba ranshi tafarfasa kawai yake duk in yatuna shaye shaye Rahima keyi sai yaji he can go to any limit to discipline her, dawani mahaukacin gudu Sameer ke binshi saida sukai nisa sosai saida Sameer yaga babu motoci sosai a express road din dudda yasan wat he is about to do is risky sanan yay wani irin over taking Abba kafin yay kwana yasha gabanshi motar Abba dat was on high speed yataka wani mummunan birki da saida Rahima ta kwala ihu dan tazaci mutuwan tazo kiris yarage baufi tsayin finger ba da motar Abba tadaki ta Sameer, Sameer bai damuba yabude motar yafito shima Abba ya kashe motar yafito yayo kan Sameer cikin fushi yace "so kake na kashe ka Son?" Sameer baimabi takan tambayan da Abba kemai ba cikin fushi yace "where are you taking Rahima to?" sosai zuciyar Abba ke tafarfasa yay pointing motarshi yace "Sameer that girl Rahima shaye shaye take, babu namijin kwarai dazai

yarda ya aureta tariga tama rayuwanta illa, Sameer inhar Rahima tasami wani dake kokarin mata fiyade alamun sonta yake kenan, tunda dai sarkin musulmi ne kuma magidanci zan maidata kauyen, nace mai ni mahaifin tane  he don't have to rape her gani nan nakawo ta nabashi aurenta ko karfe nawan dare nakai gombe saina daurama that stubborn girl aure da sarkin nan" Abba yay maganan yana kumfan baki kaman baisan meyakeyi ba, dawasu red eyes Sameer ya kalli Abba yace "Abba kariga kace am your son, kabani amanan not just Rahima your last daughter but your whole entire family, and you call Siddiqa, Lubabat, Zeenat and Rahima my sisters, as a Son, kasan Son can stand up to mahaifan su su nuna musu sunyi kuskure, Abba you are blind today, ka makance da fushi da anger, children smoke children take illicit drugs but this you are doing will push them suyi drugs din more" yy shiru sanan ya kalli Abban dake kallonshi babu ko tsoro yace "there's no way am going to allow you marry this gurl off to a rapist, kasan hukuncin mutumin nan kuwa, metayi? Wani laifi tayi dazaisa kamata wanan hukuncin dat will affect her life forever, just because of shaye shaye? Eh? Eh" yay ma Abba ihu cikin fushi kafin yakama hannun Abba yadaura kan saman kanshi yana kallon Abba a ido yace "Listen Abba! I Lieutenant Sameer Simran swear to you I will marry her, tunda dai aurar da ita kakeso kayi zan auri Rahima Abba, just give me from now zuwa anjima, I will meet my parents da zancen meanwhile I take her back to rehab centre, anjima around isha'i nida da yan uwana zamuzo muje masallaci ka daura min aure da ita, you will see how I will change the Rahima dakake kokarin wulakanta rayuwanta ayau sabida tana shaye shaye to Rahima da tadena shan komi tadawo that dream daughter da u always picture Rahima to be, and I swear to you, swear to you, wlh, wlh baxaka taba aurar da kanwata to that man ba, you are a judge kafin kowa sanin hukuncin shi amatsayin na mutumin dake raping underage, that pervert of a man, a pedophile but u are too blind da fushi yahanaka gani kana kokarin bama yarka auren shi, as am talking to you now that man is under hot hot interrogation while the whole village government have evacuated them, babu kowa on that village, yaran dayama ciki sama da 15 are under serious check ups, you can check the news channels television news sun dau rahoton komi and see the work of the man u are trying to get your daughter married to, dats all am going to tell u"  yawuce shi cikin fushi yaje wajen motan Abban yabude back sit Rahima yagani takife kanta kan cinya kuka take kaman zata shide, hannu yasa yadagata yakamaa hannunta yarike yafito da ita daga motar sukazo suka wuce tagaban Abba taba kuka sosai yabude motarshi yasata ciki ya shiga mazaunin direba yaja motar yay kwana yabar wajen a zuciya batare daya kalli Abba ba.

54 & 55

Abba yadade tsaye kan titin nan ko motsin kirki yakasa kalaman Sameer kaman sunyi resetting brain dinshi, he can't believe what he just heard, uban horn da ake dannamai ana Malam lafiya sabida yanda ya kashe mota yafito shikadai ya tsaya kan titi tareda rungume ciki kaman wanda yasoma zarewa, horn din suka dawo dashi daidai hakan yasa yajuya da sauri yay cikin mota ya kunna yabi u turn yakoma gida haryaje gida yaran namai magana kasa amsasu yayi sai dakinshi kawai yawuce yarufe tareda zama, ko Allah yasan yana cikin wani farin ciki da mugun mamaki ne abu biyu atare, Sameer, Sameer this well mannered yaro, baligi dakeda cikakken

hankali, da yasan yakamata, yakeda aikinyi, wanan babban mutum dinne zai auri Rahima yasake tambayan kanshi heart dinshi na racing, saikuma yace "ahhh haladai kawai yafada ne dan karna maidata kauye yakaita rehab" wata zuciyan yacemai karka yarda harsai kaga sunzo anjiman shida yan uwanshi da isha'i sunzo adaura auren sanan saika yarda, tayaya ma mutum kaman Sameer zai auri Rahima, haka Abba yazauna ya kwance ya kulla ya kwance ya kulla shi kadai yakasa yarda cewa Sameer zai auri Rahima.

Har cikin Rehab din ya shiga sanan yafito yana kallon yanda take kuka har lokacin, ya zagayo yabude mata kofa yace "come out" fitowa tayi tana goge kwalla dasuka kasa saina zubowa yace "idan kikai mistake din sake guduwa daga nan wlh sainabar mahaifinki ya maidake kauyen" girgiza mai kai tayi cikin kuka da sauri tace "wlh bazan gudu ba, dan Allah banso na koma kauyen nan" tasake rishewa da kuka, dauke kai yayi yace "follow me" office din likitan dayamata registration receptionist takaisu likitan na ganinta yay dariya yace "oyoyo our run away patient, munsan zaki dawo all your things are intact, gadonki ma haka" yana maganan ya kwalama Asabe kira. "Asabe" da sauri Asabe ta shigo sanye da kayan security dinta, Rahima yanuna mata dake gefen Sameer tana share hawaye yace "take her, let her change to uniform" shigowa tayi tai wajen Rahima tareda kama hannunta tace "mutafi" binta Rahima tayi tana waigen Sameer da yabisu da kallo tana kuka sosai mara kara Asabe tarufo musu kofan, kallon Dr Sameer yayi yace "hope babu wani matsala and she's not too late?" da sauri Dr yace "not at all Lieutenant, babu wani matsala ai patient naguduwa haka is not new, adawo dasu and we continue with the treatment, burinmu subar shaye shayen kawai" gyadakai Sameer yayi yace "take extra care of her please, asamata ido sosai, like I don't even mind nai extra payment inhar zaku sata on 247 watch" ahankali Dr yace "you can count on that, basai ka biyaba, normally wayanda suka gudu aka dawo dasu anama chanza musu daki, dakin daza'a mai dasu bazama su dinga fitaba all treatment nasu anan ake musu sunda bayinsu awajen and security da nurses dake kula dasu basa barin wajen, karka damu I assure you baxaka ji bad news din da kaji da ba" gyadakai Sameer yayi tareda mikamai hannu suka gaisa yace "thank you Dr, I'll be on my way now" "alright Allah kiyaye hanya" wucewa yayi yafita tareda shiga motarshi yarufe yafita daga rehab din yadau hanyar dazai kaishi gidan Baffa shi gabanshi nadan faduwa, wayarshi yaciro while driving yay dialing number Baffa yakara akunne, ringing daya Baffa yadauka cikeda girnamawa Sameer yace "barka da rana Baffa" daga tachan bangaren Baffa yace "barka da maraice dai Sameer, abinda yay karfe biyar da rabi ai yay dare" gyadamai kai Sameer yayi kafin ahankali yace "Baffa kana gidane ko wajen aiki inaso nazo na ganka" cikin yanayin magana na manya Baffa yace "too ni gani a gidanku nazo nemanka kaima kana nemana, kazo nan gida kawai ina jiranka, gani nan tareda mahaifiyar ka da kannenka shigowan su kenan ma sun taso daga wajen aiki" ajiyan zuciya Sameer ya sauke yace "to gani nan zuwa" kara gudun motarshi yayi harya shigo anguwarsu dake nan sabuwan GRA, horn yayi aka budemai mota tun kafin yay parking Mu'az yafito dagudu yazo wajen parking space din ya tsaya, parking Sameer yayi murmushi kan fuskarshi yabude motar yafito da gudu Mu'az yazo yace "oyoyo Ya Sameer" yafada jikinshi, kanshi Sameer ya shafa yace "how you?" dagowa Mu'az yayi ya kalleshi ashagwabe yace "fine Yayan mu, Yayan mu I miss you wlh tunda nadawo kai tafiya bakanan, ya hanya?" ahankali Sameer yace "lpy lau" sanin Mu'az cikashi zaiyida surutu yasa yace "Baffa na

falo ko, let's go"

Suka wuce, sallama yayi suka shiga hadadden falonsu inda Baffa da Ummi kadaine ka falon Ummi kan dogon kujera Baffa kuma sanye da manyan kaya kan 1siter suna hira saisu Noor da Muhammad dake dining dukansu suna sanye da suits  sunacin abinci alamun daga aiki suke, shigowa falon yayi anatse yakarasa inda Baffa yake cikeda girmamawa yadan duka yace "ina yini Baffa" murmushi Baffa yayi yace "Ipy lau Sameer, kadawo Ipy yanzu mahaifiyar ka ke cemin kaje gombe wani aiki aiko naga news din ashe kaine behind it, you are good my son haka akeso mutane kuma irinsu Wadugaga Allah yakara kara tona musu asiri aduk inda suke adoron kasan nan, sukuma yaran Allah ya saukesu Ipy Allah yabasu Ipy" atare kowa na dakin yace "Ameen" tashi yayi yajuyo ya kalli Ummi data zubamai ido kaman tana kallon TV ganin dukya rame mata kusada ita yazo ya zauna ahankali yace "ina yini Ummi na" murmushi tamai tace "andawo Ipy soja" gyadamata kai yayi, Noor da Muhammad ne suka shigo falon har inda Sameer din yake kusada Ummi sukazo, Noor yace "sannu da zuwa Ya Sameer ina yini" murmushi yamai yace "Ipy lau Noor, ya office" fine yace yana zama kusada shi Muhammad dake tsaye dan kujeran tacika yace "ina yini Ya Sameer kadawo Ipy, harkadan rame wlh, ni saisa bazan iya aikin soja ba" murmushi Sameer yayi Ummi ta harareshi tace "lazy kawai" dariya yayi yakoma kan kujeran Mu'az yake zaune ya zauna. Ummi ta dubi Sameer tace "go and freshen up Baffan ka wajen ka yazo" girgixa kai yayi yace "nima akwai maganan danake so naida Baffa, anjima I will freshen up" ganin haka yasa Baffa yatashi yana gyara babban riganshi yace "okay bismillah muje sama" tashi Sameer yayi yabishi sukai sama, dakin marigayi mahaifinsu suka shiga Baffa yazauna kan kujera shikuma Sameer yazauna akasa, zama Baffa ya gyara yace "I hope magana zakamin kan zancen da I am sure kasan shine yakawo ni gidan nan this evening" dagokai Sameer yayi jin anbude kofa Ummi ce ta shigo dan takasa hakura so take taji koyasamo matarne, waje tasamu tazauna tareda gyara zama, Baffa ya kalli Sameer dayasake maida kanshi kasa yace "go on Son gani ga mahaifiyar ka we are listening" ajiyan zuciya ya sauke tareda fuzar da iska gabanshi nafaduwa ahankali yace "Baffa nasami wacce zan aura!" babu wanda yay expecting wanan maganan daga bakin Sameer, wani irin murmushi Ummi harshi Baffa sukayi, kafin suce wani yace "Baffa ina neman alfarma daya" da sauri Baffa yace "mecece alfarman Son?" kanshi akasa yace "inaso yau dinan zamuje kudauramin aure da ita I've already promised babban ta from now zuwa lokacin isha'i zamuzo" shiru duk akai a dakin kafin Ummi tace "wanan wace irin magana ce haka? Bikin ka damuke muyi nagani nafada, babban d'ana my first son is getting married kazaci karamin biki zanyi ne eh Sameer" ahankali Sameer yace "that will all come later Ummi, dan Allah Baffa yau dinan nakeso a daura auren" Baffa ne ya wurgomai tabaya yace "why are you so in a rush to get married kaida ba auren kakeso ba, why are you pressuring us muje a daura auren this night?" Baffa ya wurgomai tambayan yana kallonshi, faduwa gaban Sameer yayi yay dan shiru yakasa magana Ummi tace "badakai ake magana ba Soja" dan dagokai yayi ya kalleta kafin yamaida kanshi kasa ahankali, Murya chan kasa yace "sabida inaso na taimaki yarinyar ne" da sauri Baffa yace "taimako? Taimako? Wani irin taimako kuma, Sameer wacece wanan yarinyar dakake so ka aura?" shiru

yayi gabanshi nafaduwa baya karya kuma baima iya karyan ba, and koda family shi will find out anything akan Rahima yafiso su faraji daga bakinshi, but yasan his family bazasu yardaba. "Sameer Simran!" Ummi takira full name nashi dan ayanda yakeyi yafara sa tana tsoro itama tace "ba tambayanka abu Baffan ka yayiba" ahankali ya sauke ajiyan zuciya yace "she is Rahima a drug addict" atare daga Ummi har Baffa suke kallonshi, cikeda kokonto tsabagen son ta gasgata abinda kunnuwanta suka jiyomata tace "yar shaye shaye kake nufi Sameer?" gyadamai ma Ummi kai yayi batare dayabari sun hada idoba yace "yes tana shaye shaye, yanzu haka tana rehabilitation centre, inaso na aureta because I want to help her, inaso na taimaki rayuwanta, change her duk tabar shaye shayen tadawo yarinyar kwarai natsassa, I want to do jiha......." "are you mad Sameer?" Ummi tadakama Sameer wani mahaukacin tsawa tace "Sameer anya maganganun da akeyi akanka ba gaskiya bane kuwan, anya bakada aljanu?" girgixa kai yayi yace "Ummi lafiyata kalau, I know what am doing, taimakon ta zanyi" "kaci uwaka da taimakon" tabugamai uban dakuwa da hannu cikin fushi sosai tace "for good 39yrs yanzu Sameer fama mukeyi dakai kayi aure kaki, kanenka duksunyi aure sun hayayyafa, yanzu da mukai pressuring naka ganin u are not getting any younger, Baffan ka yabaka 30days kafito da wacce zaka aura, dakaga 30 days din sun cika shine kazo kana cemana yar shaye shaye zaka aura Sameer, nice zaka auroma sirika yar shaye shaye, shaye shayen natama haryay worse and dangantata da rehabilitation centre shine zaka auromin?, wasa kake yaro, gwarama kafito da wacce zaka aura kabar maganan wanan yar shaye shayen dakakeyi" Ummi ta shiga masifa shiru yayi yanajin ta harsaida tagama tai shiru sanan ya dago kanshi ya kalli Baffa daya tsareshi da ido dahar yanzu baicemai komiba sanan ya kalli Ummi kafin yace "am sorry Ummi and Baffa, ita nakeso na aura idan kuma bazaku barni ba shikenan bazan iya ja da maganan ku ba amman saidai nahakura da auren har abada" yakara she maganan ahankali, tashi Ummi tayi cikeda fushi tafita daga dakin abakin kofar dakin ta tsaya ta kwalama su Noor dake hiransu akasa kira. "Noor, Muhammad, Mu'az kuzonan, you guys should come and talk sense to kan yayan ku, ni yayanku zai auroma yar shaye shaye, kuzo kumai magana" tashi yaran sukayi duk atsorace this is the first time sukejin fadan Ummi da Sameer karara sukai sama duk dakin suka shiga Ummi tanuna musu Sameer dake zaune akasa kanshi akasa tace "kunga yayanku ko Noor yazo yana cemana yar shaye shaye zai aura da tsabagen shaye shaye ya taba kwakwalwanta har aka kaita rehab dan ai wayanda brain dinsu yatabu ne sabida shaye shaye ake dangantasu da rehab kunga wanku wai itane zai auro, kuma da daddaren nan yake so aje wajen babanta adaura auren" ganin yanda Ummi keyi yasa Noor yace "Ummi calm down ki zauna please" zama tayi kan kujera tana kallon Sameer din, Noor ya zauna akasa kusada yayan nashi sauran ma suka zauna ya kalli Baffa yace "Baffa menene me yake faruwa?" shiru Baffa yayi baice komiba yana kallon Sameer din, gyaran murya yayi yace "Sameer me kake cewa inhar muka hanaka aurenta saidai ka zauna ahaka bazakai aureba?" ahankali Sameer yace "Baffa ita kadai ce wacce raina keso ya aura badan komiba sabida inaso nai jihadi na taimaki rayuwanta, inkuma kun hanani bazan muku gardama ba amman ni bazanyi aureba kuma dan banda wata wacce nakeson kuma na aura" cikin wani irin yanayi Baffa yace "haka kace?" shiru yayi Baffa yadakamai tsawa yace "I said haka kace Sameer?" gyadama Baffa kai yayi ahankali batare dayabari sun hada idoba hakan yasa Baffa ya karkada kafa yace "good" ya kalli su Noor yace "kumutashi muje masallaci ankira magrib muyi sallan magrib daganan mu wuce muje mu dauroma yayanku aure" da sauri Ummi ta tashi tsaye tace "Baffa!" hannu Baffa

ya daga mata yace "kibarshi Sameer ba yaro bane yanada shekaru arba'in ba daya, Sameer yasan difference tsakanin right and wrong, sanan yasan in yan uwanshi sun yarda da abu dakuma in sunki, duk yasani, da ace shi yarone kaman su Noor da Mu'az da zamu iya hanashi amma yariga yawuce wanan stage din yasan meyake yi, if he choose this path dudda kin nunamai bakiso yace zaiyi ki barshi ba karamin yaro bane shiba, ni waliyinshi ne am only going there na sauke nauyina da hakkokina amatsayina na kanin mahaifinshi kuma mahaifinshi banda haka kuma babu komi, duk yanda yayi daidaine Allah bada sa'a" da sauri Sameer yace "Baff...." hannu Baffa yadagamai yace "I've given you that chance na magana and you've said wat u wanna say dan haka tashi mutafi banson jin wata magana daga gareka" shiru yayi yakasa tashi, "katashi mutafi nace!" ahankali yatashi yakasa daga ido ya kalli Ummi datake binshi da kallo cikin tsantsan bacin rai gaba Baffa yayi yakalli su Noor da duk suka tsaya yace "kumuje" binshi duk sukai abaya suka fita Sameer kaman kwai yafashemai aciki kasa fita yayi ya tsaya awajen kofa kafin ahankali yajuyo ya kalli Ummi suka hada ido baki yabude zaiyi magana Ummi tace "banson ji just go Allah bada sa'a" tai kwafa, zaiyi magana Baffa ya kwalamai kira daga kasa da sauri yafita duk ranshi badadi yasame su, batare da Baffa ya kallai ba yace "kira baban yarinya kace muna hanya" gyadamai kai yayi ahankali kannenshi sai kallonshi suke yaciro waya yay dialing number Abba.

Abba na zaune a dining su Siddiqa sun ijiyemai abinci yakasa shi expecting call din Sameer kawai yake yakira yacemai wasa yake yay hakane dan karya kaita kauye yaji wayanshi na ruri, da sauri ya dauka yakara a kunne, kafin yay magana Sameer yace "Abba Baffana yace nafadamaka we are on our way" Abba couldn't believe abinda kunnuwan shi suka jiyemai yama rasa mezaice da kyar ya tattaro yan kalaman bakinshi yace "Allah yakawo ku lpy" katse wayan Sameer yayi Baffa yace "kumu tafi" fita sukai daga dakin, sukai wajen Gate Baffa yaciro kudi masu yawa yamikama Mu'az yace "kaje tsallaken titi kasayo goro da sweet, kaje da gateman yatayaka dauka, kasamemu a masallaci" gyadamai kai Mu'az yayi yana kallon fuskarshi Baffa yawuce yafita yaran biyeda shi.

Kasa yarda Abba yayi da kyar ya lalubo number babban aminin shi Baban Aisha yakirashi yacemai yazo yanzu dan Allah, sanan yakira Chairman din NDLEA duk sukace mai gasunan zuwa, tashi yayi ciki dan ya shirya.

Akusan tare su Sameer da abokan Abba suka iso, shima Abba daman yashirya yaci gayu yana hango motoci yafito daga gidan ahankali yana kallon kowa yama kasa yarda, gaggaisawa aka shiga yi shi kanshi Sameer saida yay mamakin yanda Baffa bai nunama Abba komiba saima wani gaisuwan mutunci da aka shiga yi kaman ansan juna da dadewa gabaki daya sanan Abba yanuna musu masallaci yace "mu shiga, Bismillan ku yanzun nan aka idar da isha'i nariga na sanar da limamu zuwanku kumuje" atare aka dunguma aka shiga masallaci.

Zazzama akayi limam yafara gabatar da huduba kafin ya daura aure tsakanin Sameer Simran Sameer da Rahima Sambo Rikadawa, inda Baffa yaciro sadaki dubu dari da hamsin wanda sune kudin dake jikinshi yabiya mai Abba yakarba sadakin shafa fatiha. Sanan aka shiga gaishe gaishen farin ciki Sameer kanshi akasa yana zaune kawai shikadai yasan me yakeji, Mu'az yakawo sweet da goro limam yadeba yace za'a rabama jama'a gobe sauran Abba yasa gateman dinshi yay gida dashi, su Siddiqa na zaune a falo sukaga gateman na shigowa dasu goro, Zeena ne tace "na menene?" washe baki yayi yace "Alhaji yace nakawo gida nabarshi masallaci dawasu manyan mutane" yay maganan tareda juyawa yafita daga dakin.

Tattaunawa aka shigayi inda Abba yamasu Baffa introducing kanshi, sosai Baffa ya yaba da hankalin Abba ashe babban mutum ne kawai dai irin iyayen nanne dat are so unfortunate Allah yabasu yara marasa ji, ko kadan bai nunama Abba komiba har wajejen goma suka tashi aka shiga sallama aka tafi, ahankali Sameer ke biye dasu suka tafi Abba nadaga musu hannu, sanan Abba yakoma gida ranshi fess, kaman anmai kyautan aljanna, falonshi ya shiga yana murmushi Luba tace "Abba goron nan da sweet na miye?" murmushi yayi yace "don't worry my daughters I promise kaina sai mamanku tadawo sanan zan baku good news din" duk washe baki sukayi ganin Abba na farin ciki, yace "zan shiga study room dina, inkun gama ku kwanta" yay maganan tareda juyawa yafita yay study room dinshi, bude dakin yayi ya shiga ya zauna tunane tunane yake fall ranshi sanan ya kunna computer dinshi, wani page na italian world ya shiga kafin yadau number wajen da sauri yay dialing number da sauri yakara akunne saiyay magana. "I want full house furniture na royal Italian"...... Washe baki kawai Abba yakeyi yana wasu bayanai da banso kuji😛
56......

Koda suka koma gida kasa shiga falon yayi hakan yasa yawuce flat dinshi ahankali Baffa kuma ya tasa sauran yaran sukai bangaren Ummi, almost 1hr suka bata a flat din Ummi sanan suka fito Baffa da Noor da Muhammad kowannensu ya shiga motarshi dan komawa gida.

Dudda irin gajiyane dake jikinshi kasa bacci yayi, wanka kawai ya iya yowa yadawo bedroom din daure da towel a waist, he is so sad he is not happy he never wish for this to turn up like this, to Yaya zaiyi, agogo ya kalla hakan yasa yabude system dinshi dake kan bed din ahankali ya shiga Skype ya shiga kiran contact mai suna Ayaan, ringing kusan hudu kafin Ayaan yadauka yana zaune a office as usual sanye da pc, yana dauka yace "1 minute buddy" tashi yayi yacire lap coat din jikinshi ya sagale sanan yakarasa gaban wash hand basin din office dinshi ya cire hand glove yasa a trash ya wanke hannu sanan yadauko wani handy yadawo yazauna yana kallon fuskan Sameer ta screen din dayaga yamai wani iri, zama yayi tareda jawo kujeran gaba yace "wats wrong buddy?" wani irin ajiyan zuciya Sameer ya sauke ya fuzar da iska mai zafi yace "I got married an hour ago" da sauri Ayaan yace "y....ou, wait are you saying

you got married today ko mekake cewa ban ganeba?" cikin wani irin cool voice yace "I got married Ayaan, dazun nan" yafadi maganan tareda dafe goshin shi, shiru Ayaan yayi yana kallonshi kafin ahankali yace "Sameer you got married, yaushe kasami yarinya, yaushe akaje neman auren har aka daura, when did all of this happen batare danasani ba? So ranan nan damukai waya all you said to me akan bakada wacce kakeso u will want to marry a matured mace soja was all a lie?" girgixa mai kai Sameer yayi ahankali yace "kaima kasan your friend never tell lies" da sauri Ayaan yace "yes I know buddy, the news hit me ne kawai with shock kagane, talk to me Sameer wats happening? Besides you don't look good at all" dan lumshe ido Sameer yayi kafin yabude ahankali yashiga bashi labarin tun ranan da yahadu da Rahima harzuwa yau da aka daura musu aure yanzun nan. Ajiyan zuciya Ayaan yasauke yace "Lord! What a story, buddy in this world akwai evil people, and your worse enemy shine wanda kullum yanama dariya yana nunama yafi kowa sonka nan ko he is killing you, wlh I pity yarinyar like sosai ta mugun bani tausayi, ka burgeni da you know the father nothing akan halin matarshi kaiba munafuki bane koba komi darajan 3 children dinta masu hankali but tasani Allah baya bacci kuma wlh saiya sakama yarinyar da looks at her as mahaifiyar ta, yarinyar dake sonta tsakani ga Allah, yanzu tunda kadauke Rahima daga gidan shikenan sai muga inda zata kara ganinta tadinga bata kayan shaye shayen, and karka damu yanda Ummi ke reacting is normal every parent will act like that, ka lallabata kaita bata hakuri trust me zata sauko, kacire damuwa aranka yanda kaga abun nan yafaru haka Allah ya tsara you can't escape okay" gyadamai kai Sameer yayi taredayin dan murmushi hankalinshi ya kwanta, Ayaan yace "to yanzu wats your plan with Rahima?" dan lumshe ido yayi yabude ahankali yace "I don't have any plans, but inaso dazaran tagama rehabilitation din tadena shaye shaye ta chanza zan rabu da ita, taje ta auri mai sonta kota cigaba da school" wani mugun kallo Ayaan yamata yace "wat do you mean by kasake ta? Baxaka zauna da ita karufa mata asiri ba, kasan inta koma gidansu me Mummy zata cigaba dayine ko daga ina zata bullo" dan jim Sameer yayi saikuma yace "okay, zan nema mata wani mijin inhar tasamu tsayayye saina aurama ta shi" wani irin murmushi Ayaan yayi baicemai komiba yace "ok, yanzu dai ka lallaba Ummi, poor Ummi tagama planning how she's going to celebrate her first son marriage amma yazo ya lalata komi" hararan shi Sameer tayi yace "get back to work bye" ya katse wayan tareda kashe system din ya kwanta yay addu'an bacci yay shiru yana tunane tunane ahaka yay bacci.

Da asubahi yatashi as usual wanka yayi yafito ya shirya cikin farin jallabiya yafito yatada gateman yawuce masallaci dan yasan Ummi zata tada Mu'az.

Wuraren 6:30 shida Mu'az suka shigo gidan, Mu'az dukya wani koma kaman mara lafiya ganin Sameer is not happy, ganin yay falon Ummi yasa Mu'az yace "Ya Sameer yau bazaka fita jogging ba?" gyadamai kai yayi yana shiga dakin, falon babu kowa sai yar aikinsu dake goge goge tagaidasu Sameer bai amsaba yayi hanyar dakin Ummi shikuma Mu'az yasami kujera yay zaman shi a falo baiso yanishi suje gaida Ummi tare dan ko kadan baiso anama Ya Sameer fada agabanshi bashi kadaiba harsu Ya Noor ma, sun tsani suga anama babban yayan su fada

agabansu wani iri sukeji he can't explain the feeling, but the feeling is uncomfortable.
Sallama Sameer yayi ahankali yatura kofar dakin, hadadden dakin dake dauke da bban gado da hadaddun labulaye, Ummi na zaune kan wata Royal kujera ja dakenan ita kadai ce adakin one sitter tai relaxing bayanta tana sanye da hijabi hannunta rikeda charbi tana lazimi hada ido datayi da Sameer yasa ta lumshe ido bamatason sashi a idanunta, mugun haushin shi takeji bana wasaba, ahankali Sameer yamaida kofar dakin yarufe ya shigo yana kallonta shi kadai yasan yanda yakwshi fushin mahaifiyar shi agareshi sashi yake yaji kaman zai haukace, baida peace of mind karasowa yayi har inda take zaune ya zauna akasa, Murya chan kasa yace "ina kwana Ummi" kaman ma Ummi batasan wani hallita ya shigo dakinba haka tayi ta shareshi tacigaba dajan charbinta, jitayi zuciyarshi na kumfa Ummi maisonshi dake kula dashi kullum hakane yauke fushi dashi tamaki amsa gaisuwan ta, ahankali yasa hannunshi dakedan rawa yakama hannunta data rike charbi dashi, wani mugun kallo tamai batare data cemai uppan ba bakinshi narawa sosai yace "ki...yafemin....Ummi" dan gyaran murya yayi danji yayi muryanshi na dishashewa yace "I'm sorry Ummi, please ki yafemin" fizge hannunta tayi daga nashi tacigaba dajan charbinshi ahankali ya kwantar da kanshi kan kafafunta wasu irin hawaye masu bala'in dumine suka shigo zubomai, yakai almost 5min ahaka sanan yadago kanshi ya kawad da fuskanshi gefe yasa hannu ya goge hawayen tass, sanan ya kalleta da idanunshi dasukai ja sosai yace "kiyakuri Ummi dan Allah, zan tafi aiki karnai latti, mezan taho miki dashi inzan dawo? Akwai fruits?" ganin ko kallonshi batayiba yasa yatashi kaman wanda jinin jikinshi yakare yajuya yay hanyar kofa, hannu yasa zai bude kofa Ummi tadanyi gyaran murya da sauri yajuyo, babu alamun rahama kan fuskarta tace "in kaje dakinka ka tabbatar ka tattaro kayanka tatas ka jera a akwati kabarmin gida danyau bazaka kwanan mini agidaba, kariga kayi aure kabarmin gida kenan, and the so call yar shaye shayen matan taka koma ina kace take better go and bring her dan in mutane sunzo zasuje su ganta ba rehab zan dinga turasu ba gidanka zan turasu" tai maganan tana watsamai harara, juyawa yayi da sauri yafita daga dakin, ko kallon Mu'az dake zaune afalon baiyiba yawuce yafita Mu'az yabishi da kallo ya mugun bashi tausayi dan yaji me Ummi tacemai.

Fkat dinshi yaje ya shiga sauko da akwatinan shi dan baya iya ja da maganan Ummi jiyama he regard it as kaddara ce kawai, ahankali yashiga hada kayan shi na amfani barin ma takardun shi yana tunani yagama gidan tass amma dayake aiki yatasashi agaba baibi takan zubama gidan furnitures ba, message ne ya shigo wayanshi, ajiye kaya a akwatin yayi yadau wayar, ganin message daga Abba ne yasa yabude.
_"Assalamu Alaykum Son, I will really like to see you in person inkasamu chance maybe koda anjima ne I ka dawo daga aiki, sai secondary, akwai interior company danai contacting dan kayan dakin Rahima, they called sunaso suzo suyi taking measurement din dakunan dan yau zasu fara kawo kaya, I don't know how you will go about it thanks_
Dan jim yayi dan baiwani so Abba ya wahalar da kanshi shizaisa komi besides bawai auren dindindin bane yarinyar dazai rabuda ita, reply kawai yama Abba da address din gidan dan baisan mezaiyiba, hada kayanshi yayi daga bayama Mu'az ya shigo yatasashi suka hada tsaf a akwatuna guda hudu tsaf sanan ya shiga wanka agurguje yazo ya shirya cikin uniform Mu'az sai kallonshi yake, yana gamawa yatasashi suka gunguro kayan yasaka a Boot sanan ya shiga mota yatafi, hawaye Mu'az ya share na bakin ciki.

Wuraren karfe goma Mummy ta shigo gidan, parking tayi tafito taci gayu sosai har wata yar kiba yakara tasa wata dog uwar atampa dayasha stone work, jakanta tadauka sanan ta kwalama gateman kira tace "ya shigo da sauran kayan inya fito daga bayi" dan cewa yayi yana bayi tai ciki, sallama tayi ta shiga falonsu babu kowa sai su Siddiqa dake kallo suna ganinta duk suka tashi da gudu. "oyoyo Mummy, Mummy ya sunan ina tsaraba?" dariya tayi ganinsu tace "yanzu mai gadi zai shigo muku da tsaraba....." kasa karasa maganan tayi sabida jakunkunan goro da sweet data gani ta kalli yaran tace "wayan chan goron da sweet na miye?" Luba tace "na Abba ne jiya da daddare yabama mai gadi yakawo ciki, yacewai saikin dawo zai fadi mana goodnews din" da sauri Mummy tace "good news, what could possibly be this goodnews" ta kallesu tace "ina baban naku yake" "yana study room" jakanta tabawa Zeena tace "kaimin daki bari naje wajenshi naji wani news ne" juyawa tayi tai kofa zata fita kenan saiga Abba zai shigo murmushi tayi tadawo baya tace "Abban su ai wajenka zani, naga goro yara suncemin goodnews ne wai kace saina dawo zaka fada" shigowa dakin Abba yayi tareda kana hannun Mummy ya zaunar da ita kan kujera yace "ku zazzauna kuji" washe baki Abba yayi farin ciki kaman zai zuba ruwa akasa yasha, ya kalli goron sanan ya kalli Mummy yace "kinsan goron waye?" da sauri Mummy itama ta washe baki ganin yanda Abba ke murmushi tace "saika fadi" cikeda murna Abba yace "goron daurin auren yarki ce" cikin rashin ganekan zancen Mummy tace "daurin auren y'ata, wace y'ata?" da sauri yace "Rahima" dawani irin sauri Mummy tace "Rahima! Rahima Auta na, ita kama aure?" washe baki Baffa yayi yace "jiya tadawo ai itada Sameer yamaida ta rehab, so around 9 nadare aka daura auren" yay maganan yana chusa hannu acikin aljihu yaciro wasu kudade sababbi ya ijiye kan jikinta yace "ga sadakin ta nan dubu dari da hamsin" faduwa gaban Mummy yashigayi sosai da sosai jin ya ambato Sameer, ahankali bakinta har rawa yake tace "Abban su wa.....w....waka aurama Auta?" wani hadadden smile Abba yasaki mai sauti yace "you will not believe it, this calm, natsastsen yaron mai hankali Sameer dakika sani shiya aureta" wani dry saliva Mummy tahadiye tana kallon fuskan Abba da babu komi aciki sai farin ciki bakinta narawa sosai tace "wa......wani.....Sameer Alhaji?" da sauri Abba yace "sai ance kinfara tsufa kidinga fadama mutane me yarinya ce, lieutenant Sameer Simran Sameer dinne baki sani ba, Sameer na aurama Rahima" wani irin faduwa gaban Mummy yayi wani irin abu taji suna tasomata hakan yasa ta lumshe ido tareda sa hannu tadafe kanta tana kokarin dannewa, ganin yanda tayi yasa Abba yace "wat is it Wifey?" kaman jira take tawani ma Abba ihun da batasan ta iya irinnshi ba tace "for God sake don't call me Wifey Abban su because is being long you stop treating me as such, ka tashi kadaumin yarinya dasai ranan nan nasamu da kyar kafadi mini cewa kauye ka kaita inda bazata iya dawowa ba, sai yanzu kuma kana gayamin ka aurar min dda iya, Alhaji are you trying to show me niba mahaifiyar Rahima bane saisa kake yanke decision akanta without letting me know eh? Because I think I left this house yesterday in the morning amma har akai komi bakasan yakamata ka kira ka sanar dani ba, Alhaji karasa wabda zaka aurama Auta sai Sameer wanan tuzurun duka duka shekarun Rahima nawa? Ina zata iya zama dashi ko kake yakashe ta?" hannu Abba yasa zai jawota yace "calmdowm wife" da sauri su Siddiqa suka tashi suka fita daga dakin sukai dakinsu.

Abba yace "don't be paranoid, this is such a good news da yakamata ma we should throw a party, Sameer is a good man you know, mu godewa Allah tasami miji haka kinga yanzu hankalinmu zai kwanta munsan zai natsar da ita and discipline her above all we know she's in a safer hands koba hakaba" sharr hawaye suka zubo daga idanun Mummy tace "celebrate, Alhaji kaci we should celebrate? Kadau yar jinjirar yarmu kabama tsoho ne I will celebrate, yaushe Auta zata iya daukanshi, ka aurama yarinya tosho abokin babanta sa'an kane fa" murmushi Abba yayi yace "Sameer dan 39 ne sa'a na? Kinfara tsufa wifey, banda hakama yau kananun yara suka fara auran tsofaffi su zauna lpy kijisu shiru, I think all this maganganun dakike yi aren't necessary" cikin fushi Mummy tace "Alhaji Rahima fa a cikinshi take iya tsayinta, mesa ba zaka aura mata wani ba ko cikin yayan abokanen kane sai Sameer eh, wanan katoton tuzurun yaro jiki kaman basamude....." ganin tanata surutai yasa Abba kawai ya karkada kai yace "I need to run some errand anjima nadawo zan baki wasu kudi dazakiyi ma Rahiman hidima, aure anriga an daura ki dauka haka Allah ya kaddara, saina dawo" yadau car key shi dake kan center table yafita binshi da kallo Mummy tayi kafin tafashe dawani irin kuka, bata taba sanin zata dawo gida ta tarar da wanan bakin news dinba kaman zata mutu takeji, zuciyanta yay mata daci da zafi, Rahima ta auri wanda takeso wlh bazata yardaba, ita Rahima harta isa tai kishi da ita inaaa!
57....

Fashewa da kuka Mummy tayi taci kuka harta godema Allah, ranan haka tawuni cikin kunci da bakin ciki, gawani kishin jaraba dake cinta kaman zata hadiyi zuciya tamutu, hatta y'ay'anta kasa gane kanta sukayi. Wanan kenan.

Yana zaune a office dinshi har yamma baimasan a ina zai kwana yauba dan yan interior company nan nagidanshi a auna nan a auna chan anata kawo kaya, he is so worried akan Ummi dake fushi dashi, knocking kofarshi akayi hakan yasa ya kalli kofan tareda rufe system dinshi yace "common in" bude kofan akayi Noor ne da Muhammad suka shigo duk sunamai murmushi saikuma yaga matayen su rikeda yaransu a hannu sunci gayu hakan yasa yatashi kafin yaga Mu'az ya shigo rikeda wani cake da aka rubuta happy birthday ajiki da happy married life ga uban balloons, dan zaro ido yayi like wats all this, maida kofan Nabila tayi tarufe Mu'az yakaraso ya ijiye fine cake din kan table dinshi tareda kunna fireworks din hakan yasa dukansu sukahau mai waka. "happy birthday to you, happy birthday to you, Happy birthday to Yayan mu,

happy birthday to youuuu, hip hip hurray" sukahau tafi, murmushi yayi yazagayo hannu yasa yakarbi Princess daketamai dariya Nabila tace "ina yini Ya Sameer" ahankali yace "lpy lau" sanan ya kalli jaririyan Fadila ya shafa kumatun ta yace "babygirl you came to my office today" duk dariya akayi Fadila tace "happy birthday yayan mu, ina yini" ahankali yace "Alhamdulillah" sanan yanuna musu dogon kujeran office din yace "ku zauna" sanan ya kalli Noor da Muhammad dake tsaye yace "ku zauna" zama sukayi kan kujeran dake gaban table yanunama Mu'az stool yazauna shima kafin ya koma kan kujera ya zauna rikeda princess yay murmushi tareda kallon cake din yace "I've forgotten yau birthday dina ma" yasake murmushi sanan ya kalli Noor yace "thank you guys" akadanyi shiru, ahankali Noor yace "Yaya Sameer, I came here we all came here not just for this" ya nuna cake, yace "Ya Sameer tun ina dan karami I watch how you live your life akan gaskiya dayin abubuwan gaskiya, one thing dana sani kanka haryau har gobe shine you don't just do things anyhow kome kayi I know akwai reason behind it, Ya Sameer ko prostitute today kace zaka aura I will support you dan nasan kasan me kakeyi, I trust my brother and I stand with you in every step you take, worry not okay, Ummi zata sauko itama I assure you this" ajiyan zuciya yasauke yana kallon cake din kafin ahankali yace "there's more to wat am doing ku kannai nane dole ma sanar daku, banso iyaye susan maganan dan ba hurumin mu bane mutona mata asiriba is left for Abban su should find out dakanshi" labarin Rahima yashiga basu tatas, duk dakin dama Fadila da Mu'az sune masu saurin kuka saida sukayi, Sameer yace "I just see Rahima kaman kanwar mu su Asiya and Yusra, I look at the whole case like look at Princess, ga babygirl all of them are children nobody knows tommorow, lemme save this girl dan nima inada kannai da y'ay'a mata, and if by saving her from that wicked is by marrying her am ready to do it, shikenan" tasowa Mu'az yayi da sauri yafada jikin Sameer yahau kuka, ahankali Sameer yay patting bayanshi yace "kaga nahanaka kuka u see princess namaka dariya" dagokai yayi ahankali ya kalli yayan nashi yace "Ya Sameer I want to be like you when I grow up, u truly have a heart of gold" kanshi Sameer ya shafa yace "stand up jeka zauna awurinka" tashi yayi yakoma yazauna, Muhammad ne yace "to yaushe zakaje ka daukota daga rehab? Inyazo ta dinga zuwa as an outpatient saisu dinga bata appointment" ajiyan zuciya Sameer yasauke yace "Ummi tace nadaukota but yau ana zuba funitures, am planning gobe zan daukota" gyadakai Muhammad yayi da sauri Nabila tace "Ya Sameer ni banma gantaba but Allah yadauramin sonta already and I promise you zamu riketa as a sister kuma amana batare any stigmatisation or abu makamantan hakaba ko Fadila" gyadamata kai Fadila tayi tana share hawaye, Nabila tace "but inaso ka daukota da safe, ka kawota gidana ko Fadila, we call mai lalle da saloon agayara mata kai, da daddare saimu kaita dakinta, we have to make it special I think we should throw a party ko baby" ta tambayi Noor, kafin yabata amsa Sameer yadan yatsine fuska yace "No banson party, banson anything noise" tasowa Fadila tayi tazo wajen Yaya Sameer din tace "bamu kudi, we need to get kayan dazata sa ready gobe" Nabila najin haka ta taso itama tazo tace "yauwa kin tunamin yarinya ranan bikin ta bazata saka tsofaffin kayaba, Ya Sameer akwatinta fa" dariya Noor yayi yace "yauwa ku damai dan yayanmu zai iya ya share komi babu ruwanshi" yanda sukamai chaa aka yasa yadau wallet dinshi yabude yaciro Atm card yamika musu yace "gashi, pin 5474" ihu duk akayi cikeda murna Noor yace "ehen let's cut cake and feed yayan mu is his birthday" yanda sukamai hayaniya a office yasa yace "wai ya akayi aka barku kuka shigo Barrack dinan?" da sauri Mu'az yace "cha musu mukayi we are lieutenant Sameer Simran Sameer family and today is your birthday we are

giving you a small surprise" girgixa kai yayi suka shigo gutsuro cake suna bashi har yasamu da magrib ya tarkatasu suka tafi.

Washe gari!

Daren jiya bakaramin fada Mummy da Abba sukayi ba, tun yana ganin abin nata shirme harsaida yace mata waito me danna auramata Sameer me eh, shima yamata kacha kacha ganin ya shareta hakan kuma zaifi jawo mata olla dan tanason jin information daga gareshi yasa tasameshi safiyar yau tabashi hakuri sanan ta tambayeshi ya ake ciki yanzu, yace mata kampanin interior sungama saka mata kaya duk wani kayan bukata data sani tundaga kan kitchen dining labulalye da sauran su sun saka, dama quotation din dasuka min nakomi was 11.9m, nabasu 8m, to inaso anjima zan basu sauran kudin, Sameer yacemin zaije Rehab Centre yadauko ta da daddare zanje gidan nafadi mata dakaina na aurar da ita" da sauri Mummy tace "zamuje tare nai kewan yarinya na" dan shiru yayi kafin yace "no tafiyan namiji daban naku na mata daban, idan uba yatashi zaije gidan yarshi shi kadai yake zuwa" shiru Mummy tayi kafin ta gyadamai kai tace "shikenan gobe ni naje naduba gida idan da gyare gyare nayi" kudi Abba yaciro dayawa yabama Mummy gashi kimata siyayya sanan yafito tareda kwallama Siddiqa kira tafito yace "yauwa kije dakin Rahima ki tattara yan kayanta zan kawo miki babban trolley na, da school books dinta kihada komi kikai motana, make sure u pack anything dakikasan tanaso fa" da sauri Siddiqa tace "to Abba" ta shiga dakin shikuma Abba yashiga dakinshi yafito dawani babban jakan Lv yashiga dakin yabama Siddiqa tahau aiki, ganin batasauri yasa yashiga tayani gwanin ban sha'awa Abba is just so happy, jiya harda sallan dare dan gani yake Allah gata yamai daya bama yarshi dake shaye shaye kamilin namiji irin Sameer.

***

Wuraren 11 na safe yay parking motarshi agaban rehab din batare da security sun bari yay parking acikiba ya leko yace "Sir sorry, we are celebrating 20yrs anniversary yau saisa kowa anan yake parking you can come in sir" kashe motar yayi yafito Mu'az dake taredashi shima yafito yana sanye da kananun kaya, shikuma Sameer na sanye da uniform yay wani irin asirtaccen kyau ko mesa oho, sai kamshi yakeyi, rufe motar yayi suka shiga ciki shida Mu'az dake biyada shi, compound din yagani an gyara anyi decorating da balloons black and golden, ga tables da chairs da aka zuba awajen all patient dinsu maza da mata zazzaune suna shan

drinks wasu nacin abinci wasu kuma nacin snacks gawani soft music natashi, all the patients looks very happy sai hira ake, dan the only thing dake joining maza da matansu is sport randa za'ai sport other than that kuma babu saiyau da aka fitoda kowa sabida 20yrs anniversary da Hope Rehabilitation centre ke celebrating, ahankali yake tafiya yana kallon koina kaman eyes dinshi is searching for someone, chak ya tsayar da tafiyan dayakeyi hango Rahima dayayi dake zaune itada wani fair guy da naman idanunshi kenan so black tsabagen shaye shaye, tana sanye da uniform dinta na rehab saidai kanta babu kodan hulan nan data saba sawa kuma anbata taki sawane sabida an mata tsifa an wanke mata kan dama ance mata yau za'a kawo mai kitso tamata, an mata parking gashin aka bata wani pink ribbon takama gashin dashi tasaki jelan gashin dayakai har tsakiyan bayanta bakin dukya kanannade abinku da coily hair, bakaramin kyau tayiba sabida gashin mutane dayawa maza da mata anata mata magana sabida yanda tai kyau tai kaman wata little angel irin yaran yan gayun nan, tai mugun kyau, damasu biyune kadai a table dinsu tana rikeda cocktails a cup da straw keciki tana zuka shikuma yagama cin rice yana goge baki yana kallonta dan yarinyar ta masifan burgeshi kaman yasace ta yakeji yasakin mata murmushi yace "finally yau munsami normal food munci, amma kullum aita bama mutum abincin magani ewwww" yatabe baki, kyalkyacewa da dariya tayi ya mugun bata dariya dudda batasan guy dinba ita kadai ke zaune yazo yasame ta yazauna ya ijiye abincin shi yana shi yahau mata surutu.

Wani irin abu Sameer yaji yadaki kirjinshi ganin yanda take hirada wani daketa kallonta kaman zai hadiye ta kanta ba hula iska na kada gashinta, ahankali yashiga dunkule hannu kirjinshi namai wani irin zafi.

58.

Agurguje

Da sauri Mu'az yakama hannunshi yarike gam yana kallon inda Sameer din ke kallo yace "Yayan mu itace Rahiman?" gyadamai kai Sameer yayi ahankali batare dayabar kallonsu ba, baki Mu'az yasaki yana kallonta baisan lokacin dayace "wow! My Godddd! She is so beautiful wlh" wani haushine Sameer yaji yatasomai da sauri yajuya yay cikin office din Dr dan inyaje wajen zai iya abinda he might regret yashiga yamai bayani zaidau Rahima zasu dinga dawowa as an out patient, gyadamai kai Dr yayi sanan yabashi katin next appointment din Rahima ya kwalama Asabe kira da sauri ta shigo, yace "bring all Rahima's things, and come along with the Rahima" gyadamai kai tayi yajuya tafita Dr kuma yacigaba da hira da Sameer dake amsa shi dai dai dan jiyayi ranshi yawani yi masifan baci, almost 8 minutes suka bata sai aka turo kofan dakin Asabe ne rikeda katuwar jakar Sameer na sojoji da kayan Rahima ke ciki sai Rahima dake bayanta ganin Sameer zaune kan kujera a office din yana magana da Dr dawani mai

kama da Sameer din saidai ba sosai ba yasa taji gabanta yafadi da sauri ta saukar da kanta kasa, hannu Sameer yamikama Dr tareda tashi yace "thank you Dr saimunzo" sanan ya kalli Asabe yace "where is her hijab?" yamata pointing Rahima da yatsa batare daya kalletaba, hannun Rahima Asabe takama tace "wanan ko anbata hijabin bata yarda tasaka hakama hula duk suna cikin jakan nan" dagokai ahankali Sameer yayi ya kalleta kaman tasan kallonta yake itama tadan dago kai ta kallai hada ido sukayi da sauri ta sunnar da kanta, ahankali ta tsugunna tabude jakan hijabin dake saman kayan ta dauka ta zage zip din tareda zura hijabin, hannu Mu'az yasa yadau jakan ahankali yace "let's go" juyawa tayi tafita tareda Mu'az shikuma Sameer biyeda su, hakanan gabanta ke faduwa ganin a dawo ansake daukan ta again ina za'a kaita, bayan motan Mu'az yabude nata yana kallon fuskarta yace "shiga" shiga tayi ahankali tazauna batare data kalleshi ba ya maida kofan yarufe shikuma ya shiga ciki yazauna already Ya Sameer harya tada motan Mu'az narufo door dinshi yaja motar, tafiya sukai sosai sai kallon hanya take tai shiru har zuwa wani anguwa dabama tasan anguwanba duk zaman ta a Abuja, anguwan na yan gayune gidajen hadaddu, agaban wani gida Sameer yay horn mai gadi yabude musu ya shiga gidan, awajen parking taga sunyi parking, Mu'az yafito yabude mata baya ganin batada niyyan fita yace "fito Rahima" ahankali tafito su Nabila dake jikin window itada Fadila suna leke atare sukace "woww, Baby zokaga matar Ya Sameer she is so beautiful wlh"
Fitowa Rahima tayi ta kalli Mu'az cikin siriruwan muryanta tace "inane nan?" murmushi ya sakin mata yace "gidan Ya Noor ne nan" da sauri tace "Ya Noor? Wayeshi" ahankali yace "muje ki ganshi kanin Ya Sameer ne" ganin Sameer haryay flat yabarsu wajen yasa yace "muje kigani" ahankali take binshi duk tajita wani iri a daidai bakin kofan taga wasu kyawawan mata sun fito da saurinsu sukayo kanta. "Oyoyo Rahima" saiga wasu maza guda biyu suma su fito dataga suna kama da Sameer sosai saidai yafisu kyau da tsayi da cikan jiki duk antsaya ana kallonta ganin yanda ake kallonta yasa da sauri ta matsa wajen Sameer batai wata wataba takama hannunshi tarike gam idanunta nataruwa dahawaye, wani mahaukacin shewa suka shigayi ganin yanda takire Sameer shiko wani kunya yaji da sauri ya karbe hannunshi ya shiga ciki itakuma su Fadila sukai bedroom dinta da ita inda makeup artist kezuwa, karasawa wajen fridge Sameer yayi yabude yadau ruwa yabude bottle din yadan kurba sanan ya maida marfin yarufe ya kalli kannin nashi dake wani kallonshi yace "lemme go back to the office" da sauri Noor yarikemai hannu yace "wlh baxaka tafiba, boys oya" to his biggest surprise gani yayi ganinshi drag him to Noors bedroom sanan suka rufe kofa wani kallo Sameer yamusu Noor yadan sosa kai yace "Yaya munsanar da friends dinka kai aure munmayi inviting some to dinner damuka hada muku by 5 anjima sai bayan magrib mutafi gidanku, yanzu su Nabila za'a fara gyara amaryan ka" shiru kawai yayi yana kallonsu baice musu komi ba, yanaji yana gani suka hanashi fita.

Rahima kawai binsu take da dara daran idanunta tana gani aka shiga gyara mata kai wani gyara dabatama san kanshi ba, mai lalle namata hadadden gaske, aka kunna fanka banda AC dakin sabida lallen yay yabushe da wuri, duk wani shirin Amarya da ba'a rasaba saida suka mata harda wankan turare sanan akasa tai salla duk sukai salla, wuraren 5 makeup artist tataho

aka shiga yi mata makeup nafitina aka gama tsaf wani irin kyan datayi kaman balarabiya sanan akasa tasaka wani white gown sky blue dayasha stones yana jamata kasa sosai sanan aka mata dauri, Fadila ta jawota takai ta gaban madubi tana murmushi tace "kinga yanda kikai kyau kaman fatalwa kuwa" kallon kanta Rahima tayi kafin ahankali takalli Fadila tace "mesa kuketa min kwalliya haka?" dariya dukansu suka kwashe da sauri Nabila tazo wajen rikeda Princess tace "ki tambayi Ya Sameer, bari kiga mu shirya Fadila" shiryawa suka hau yi cikin wani hadadden kaya dasukai anko itada Fadila, sunacikin shiryawa Noor yay knocking yace "baby all set fa" da sauri tace "we are coming out yanzun nan Baby" music sukaji yana tashi daga compound shiryawa sukai tsaf sanan suka fitoda Rahima dasuka rufemata fuska da net suka fito tsakar gida da ita Ya Sameer suka gani zaune kan wani royal chair yana sanye da wata bugaggiyar shadda sky blue anko shida Rahima, ga wasu friends dinshi da su Noor sukai inviting saikuma su kannenshi da sukasha white shadda da some few friends da matayen su, basu da yawa but gwanin tsari zaunar da Rahima kusada Sameer sukayi, aka shiga party ga abinci dan masu girki aka bama kwangilan girki ga drinks, Rahima dai kallonsu take ganin anamata abu kaman wasu ango da Amarya, Sameer yariga yafadi musu baya rawa so basu damai ba su suka dinga shirmen su daga baya suka dauko Rahima dataki tai rawan, kallonsu kawai Sameer yake ganin yanda family dinshi are so happy da auren shi dudda ga yanda auren yazo zaiyaji inama Ummi was here yasan da abin yafi haka haduwa......

Wuraren Magrib aka gama sanan yasa aka dakatar da wakan suka fita masallaci, SU fadila sukai ciki da Rahima suka chanza mata kaya zuwa wani fine lapaya bayan sunsa tai salla sanan suka hada mata wani nagani tasha da kyar yana dawowa ya shiga mota yace afito da ita zasu tafi Abban ta na hanya, fitowa da ita sukayi, sukasha ta shiga gaba Sameer yaja motar zuwa gidanshi, gidane nagani nafada danya tsaru sosai, horn yayi wasu sojoji guda biyu taga sun budemusu Gate Sameer ya shiga da motan ya kashe yafito, ahankali tabude itama tafito tana kallon ko'ina saida ta zagayo sanan yafara tafiya binshi ta shiga yi har zuwa cikin gidan, innalillahi heaven shine furnitures din da aka zuba mata, duplex ne gidan hadadden gaske komi yahadu tsayawa bada labarin gidan bata bakine, horn dasuka ji yasa yace "sit Abban ki ne yazo" fita daga dakin yayi hakan yasa ta zauna ahankali tana tunani dakuma fargaban haduwa da Abban nata, sallaman Abban ta dataji yasa ta dago kanta da sauri suka hada ido da Abban dake kallonta, bakinta nadan rawa rawa tace "in...ina wuni Abba" zama yayi kan daya daga kan kujeran Sameer yazauna akasa ganin Sameer yazauna akasa yasa ta kallai sai itama ta zauna ahankali akasa, gyaran murya Abba yayi anatse kafin yafara da salatin Annabi ya kalli Sameer yace "Sameer kai d'a ne dakowani mahaifi inhar Allah yabashi irinka to ya godema Allah, you are a treasure dat personally I cherish, And Alhamdulillah for knowing in this life and Alhamdulillah da mutum kaman kai mai hankali ilimi yazamo miji ga yardana haifa, koma mezan fadama kariga kasani, kuma komame zan fada maka awanan daren you've already done that even more Sameer dan cewa zanyi ga Rahima nan matarka kariketa amana but kariketa amana tun kafin ma tazama matar taka, da ayau zanfadi namutu I will be at peace because nasan mutum kaman natare da y'ata kuma zai riketa amana, Allah yamaka albarka Sameer, Allah yabuda maka kofofin samu, sanan Allah ya azurtaku da zuri'a dayyaba Allah yabiya maka bukatunka na alkhairi Sameer" ahankali Sameer yace "Ameen Abba" juyawa Abba yayi ya kalli

Rahima da tunda taji Abba yacema Sameer Rahima matar shi taji kirjinta yamata nauyi, ahankali yace "Rahima! Ayanda kika taso da rawan kai aure kan natsar da yara irinku saisa namiki zabi zabin kuma Sameer ne, na daura miki aure da Sameer jiya misali 9 nadare, ga sadakin ki nan" yaciro wasu kudi dake envelope ya ijiye agefenshi kan kujera, yace "inaso ki natsu Rahima ki tuba, yanzu ke matar aure ce ki zubar da duk wata dabi'unki na banza, nina fadama Sameer makarantan ma yahanaki zuwa at all, yacemin zaki cigaba amma saikin chanza nan da next year, Rahima ni mahaifin kine kuma mahaifi baitaba tsanan abinda ya haifaba saidai ya hukunta abinda ya haifa idan yaron yay badaidai ba, duk wani abu dana aikata akanki sabida halinki ne, wanan auren da namiki shine last chance din danabaki, Rahima inhar baki zauna a auren ki ba kin natsu kin zubar da halayen nan naki na banza ba to ki rubuta ki ijiye saidai ki nemi wani uban da wasu yan uwan dan zanma cireki daga cikin yayana ne, kuma you know what I can do, ga mijinki nan kimai biyayya, yi nayi bari nabari, karnaji sirrin gidanki awaje, ki rike sirrin gidanki ki kare dukiyan mijinki, sanan ki kyautata tsakanin ki da mahallicin ki, ina miki fatan alheri, Allah yamiki albarka, Allah ya shiryar dake Rahima, sanan Allah ya yayemiki duk wanan halayen na banzan, Allah ya ganar dake ya natsar dake, ki kula da kanki kinji" gyadamai kai tayi tana chusa hannunta kan bakinta tana kokarin danne kukan dake taso mata tana kallon Abban, ganin haka yasa Abba yaji tabashi tausayi sosai ahankali yabude mata hannayenshi alamun tazo dawani irin gudu ta tashi tawani fada jikin Abba tafashe dawani mugun kuka dayazo mata daga zuciya, rungumeta back Abba ya bubbuga bayanta tareda yima kunnenta kiss yanajin wani sonta aranshi amma yarasa yanda zaiyi da rashin jinta ahankali yace "is okay kukan ya isa haka" sosai take kuka kaman zata shide cikin kuka tace "Abba am sorry natuba kaji, bazan karaba wlh, please kayafe min dan Allah" dago kanta yayi yasa hannu ya goge mata hawayen dasuka kasa dena zuba yace "naji nayafe miki Rahima, amma promise me kin dena shaye shaye zaki natsu kibi mijinki sauda kafa kinyi alkawari?" cikin kuka ta gyadamai kai Abba yay murmushi yace "then is settled, na yafemiki, zan dinga kiran Sameer ina magana dake kinji" gyadamai kai tayi yadau kudin sadakinta yasa mata a hannu yace "this is your money, sadakin kine keep it with you kinji" gyadamai kai tasakeyi tana kuka sanan yazauna da ita agefe ya kalli Sameer da kanshi ke kasa yamike tsaye tareda gyara babban riganshi yace "bari natafi dare yayi" Rahima tanaji tana gani Abba yatafi yabarta tai kuka kaman zata sume takife kanta akan kujera ba'a wani dau lokaci ba Sameer ya shigo dakin da akwatin da Abba yakawo mata na kayanta ya kalleta yace "stand up let's go upstairs" tashi tayi ahankali cikin kuka, stairs yahau tana biyeda shi har sama wani daki yabude dakin ya jarababben hadu ga makeken gado ya ijiye trolley agefe sanan yadan kalleta, idanunta sun kumbura sosai sai kuka take, ahankali yace "stop crying" jeki alwala kifito yay maganan tareda fita daga dakin, bayi ta wuce kaman yanda yacemata ta dauro alwala tafito wardrobe din bangon dakin tabude taga babu komi ciki sai kamshi sabuntaka dayake yi ahankali ta tsugunna tabude akwatin da Abba yakawo mata, hijabin datagani asama tadauka, natane nagida ja tasaka sanan tabude kofa tafito, afalon upstairs din taganshi tsaye kan dadduma tahowa tayi itama tana tafiya kafafunta na hardewa sabida yanda yake kallonta takasa dagokai ta kallai harta karaso wajen, baice mata komiba ya kabbarta salla ya jasu jami sukai isha'i sanan yay raka'a biyu na nafila da Annabi ya koyar yajuyo yakama goshinta yay mata addu'a yagama tass sanan yazare hannun ahankali batare dayamata wata tambaya ba dan yasan batawani je islamiyya ba. Katoton tray dake kan center table din wajen yanuna mata yace "eat" kallon abincin tayi kaji ne sai dayan tray din

drinks ne da farm fresh yogurt, girgiza mai kai tayi ahankali tace "am not hungry naci abinci achan gidan" ahankali yace "okay take it to the kitchen then" tashi tayi tazare hijabin tareda ijiyewa kan kujeran wajen tadan kallai tanaso ta tambayeshi inane kitchen amma takasa, hada ido sukayi da sauri ta sunnar da kanta kasa takasa magana sai wasada yatsun ta dasuka sha lalle take, ahankali yace "the kitchen is downstairs" gyadamai kai tayi ta tsugunna tadau tray din kajin sanan tawuce tafara sauka daga stairs din ahankali tana kallon ko'ina na falon, falon yamata kyau kaman me, dinning taje kofan datagani agefe tabude kitchen ne hakan yasa ta shiga, kitchen din babba sosai gawani Island da akayi a middle of it ansaka kujeru guda hudu anzagaye shi dasu, ahankali takarasa ta ijiye tray sanan tafito tahau stairs din har lokacin yana zaune a falon news yake kallo jinta hawo yasa yadago kai ya kalleta tray din drinks tadauka tasake sauka kasa taje kitchen tasaka su a fridge sanan tadawo sama, dakinta tabude ta shiga, kayan jikinta tacire dan duk sunbi sun isheta
59....

Kanta nawani irin ciwo hakama maranta bayi tabude ahankali ta shiga bayin yamata kyau sosai, wanka tayi da ruwan zafi sosai sanan tai brush da sabon brush din dataga an ijiye mata anan wurin, sanan tadau farin sabon towel datagani abayin tadaura tabude kofan bayin ahankali tafito sai kamshi jikinta keyi sabida wankan turaren dasu Nabila suka mata, hawaye daya zubomata tasake sharewa ta tsugunna ta shiga duba kayan akwatin idan akwai kayan baccin dazata iya sawa gashin kanta na warwarewa duk yazube abayanta, tana cikin neman kayan aka bude kofan da sauri tajuyo, hada ido tayi da Sameer da shima taga ya chanza shaddan dake jikinshi zuwa wani milk pyjamas dayadan bayyanar da kirjinshi dake cikeda gashi, kasa jure kallonshi tayi ta saukar da kanta kasa tama kasa cigaba da neman kayan, karasa shigowa dakin yay yamaida kofan yarufe yace "me kike nema?" murya chan kasa mai sanyi sosai tace "kayan bacci na" dan lumshe ido yayi yace "okay, zan kwanta gud night" dan dago idanunta dasuka cikada hawaye tayi ta kallai kaman wata mara lafiya kafin ahankali tace "gud night" bude kofa yayi yafita daga dakin ya kashe wutan falon saman sanan ya wuce dakinshi.
Bataga wasu kayan bacci ba sai wani barbie pants dinta dark pink, dan babba ne bai kamata ba adaidai hips dinta ya tsaya yarufe ko ina na bombom dinta, sai wata yar karaman t-shirt dinta plain white dakenan very light baida nauyi na crop dan iya cibiyanta ya tsaya hakan ya bayyanar da fine two lines waist bid dinta nayan gayu dan dakananun bid akayisu combination of silver da gold color bids yama dan tiny waist din nata mugun kyau, itadai anything leg chain da waist tana bala'in sonsu saisa take sawa, and tanada su daban daban dan tana chanzawa every every month, tashi tayi ta mayar da kayan tsaf cikin akwatin sanan tadau wani black ribbon ta kama gashinta dashi sanan takoma kan gadon ahankali ta kwanta tana kallon saman dakin tai shiru, juyawa tayi gefe tareda sauke ajiyan zuciya tana kallon window dakin da hadadden labulenta ya kare, gani taki kaman labulen namata shape din fuskar mutum da sauri tasake tajuyawa ta kalli kofa kafin ta lumshe idanunta da sauri trying to force herself to sleep kasawa tayi, bata iya bacci inhar batajin motsin mutane da maganganun mutane around her,

